[12/17/2019, 17:50] Takori: WASAN KANIN MIJI
SHIMFIDA

1/MUHARRAM HIJIRIYYAH
HANYA MAI HADIN ZUMUNTAR DOLE!

Dare ne mai tsananin sanyi, cikin watan Nuwamba. Hazo ya lullube duhun daren ta yadda ya fidda launi mai haske kamar hadadden hadari, wanda ya takura da yawa-yawan al'ummar birnin tarayyah.
Za a iya kimanta lokacin da misalin karfe goma dai-dai na daren ranar Alhamis. Dai-dai lokacin da LAILAH UMAR BALLAH, matashiya 'yar kimanin shekaru (25) ta iso filin jirgin saman Abuja. Laila tashe take da 'yar madaidaiciyar 'troller' dinta ruwan toka a hankali, kamar mai tsoron kada santsin tangaran din takawa (tile) ya tikar da ita.
Rataye a kafadunta na dama, jakar mata ce baka mai girma samfurin (vincci) data hadiye dukkan komatsanta masu muhimmanci.
Laila sanye take da doguwar abaya da mayafinta bakake wul! Kirar Oman, da takalmi rufaffe maras tsayin dunduniya. Ta karasa ciki a hankali ta hau kan layi domin mika kayanta ga masu binciken kwakkwafi na cikin gida (customs) kamin a auna su cikin jirgi. Tana daga cikin (boarding passengers), masu tashi zuwa kasar England, a wannan daren mai tsananin sanyi, mai kunshe da dimbin tarihi da kuma sabuwar rayuwa a gare ta.
Da ganin yadda Laila ke shige da ficenta,  kai tsaye, babu tsoro, babu dari-dari, wajen mika (passport) dinta mai dauke da Kambun Sarauniya (UK Visa) gami da katin  shaida (ID Card), a duk inda anka bukaci hakan kamar yadda ka'idar matafiya ta filin jirgin ta shimfida, ka san ba ta da duhun kai; wato dai ba yau ne ta soma keta hazo ba. Sai dai kuma kallo daya za ka yi wa kayatacciyar fuskar Lailah, ma'abociyar haske, zati da kamala, gami da kwarjini bayyananne daga sarkin halitta, ka karanto matsananciyar damuwa, tsoro da firgici, har ma da tashin hankali gami da matsananciyar nadama tattare cikin fararen kwayar idanunta.
Sai dai kuma ta kasance daya daga cikin irin mutanen nan da da wuya ka karanto damuwarsu a fuska farat daya, kasancewarta ma'abociyar fuskar murmushi. Duk da haka a yau, babu wannan murmushin, babu wannan annurin. Kamar yadda zuciyarta ke cunkushe da manyan al'amura masu girgiza zuciyar diya mace, tare da jefata cikin rayuwar ha'ula'i, haka dan kankanin bakinta ke tsuke tsam! Kamar ba ta tava murmushin ba a tsayin rayuwarta.
Ta daga kanta sama a hankali zuwa ga allon kwamfutar dake manne a saman kanta, mai dauke da (travel-routine) na ranar gaba daya. (LONDERS-HEATHROW 12:am), kenan akwai sauran mintuna talatin a gabanta, kafin su tashi.
Don haka ta bi layin sauran matafiya 'yan uwanta a sansanin da aka ware domin tsimayen lokacin tashin jirgi, ta samu kujera ta zauna. Ta bude jakarta ta dauko karamar gorar ruwan (Faro) mara sanyi, ta murde ta kai bakinta tana kwankwada, cikin wani irin yanayi mara fasaltuwa. Tsabar kishi ne ko ko gigicewa ce?
Tun da ta kafa ruwan a bakinta ba ta iya ta sauke ba, sai da ta zuke robar gaba daya. Gardin ruwan ya ratsa busashshen makoshinta da bakin cikin DA NAMIJI ya busar rayas! Ya saukar da 'yar kankanuwar nutsuwa a zuci da gangar jikinta. Ta dire robar a kas, ta aje dogon numfashi, kamin daga bisani ta sanya fuskarta cikin cinyoyinta ta fashe da kuka.

Wani irin kuka mai girgiza zuciya Laila ke yi, wanda ba ta tava yin shi a rayuwarta ba, kamar yadda tunaninta bai tava bata wai watarana irin haka na zuwa da za ta yi shi ba. Balle a kan MAZA, da ta raina ma wayau. Domin tana ganin ba ta daga cikin irin matan da ake cewa suna dandanar bakin cikin DA NAMIJI. Tun da babu ta inda Ubangijinta ya rage ta; tana da kyau, tana da gata, tana da gishirin rayuwa mai tsada (ilimi). Uwa uba nasabar mafi soyuwar jinsi, wato Arab.
In haka ne to mene ne silar wannan balaguron gare ta? Zuwa inda ba Uwa, ba Uba, ba masoyi balle dangi?

Har aka yi kiran (passengers) domin bincike na karshe wanda daga shi sai shigewa jirgi Lailah ba ta ji ba. A gefenta yake zaune, tun shigowar ta, yana nazarin wata takarda mai dauke da taswirar Birtaniya ciki da bai dinta.
Ya mike tsaye a yayin da kiran ya tsinkaye shi. Ya dauki jakarshi dake aje gefe mai dauke da kwamfutar (laptop) tare da shafa aljihun bayan shudin wandon 'jeans' dake jikinsa domin tabbatar da zaman tikitinsa da passport. Ya tabbatar suna nan. Don haka ya bi jerin-gwanon matafiyan dake shiga jirgi bayan an bincike su. Sai dai har zuwa lokacin sautin shesshekar kukan yarinyar mai taushi da raunana zuciya, ya kasa daina amo cikin kunnuwansa.
Ya yi taku a kalla biyar zuwa shida, amma ya kasa daurewa. Ya rage sassarfa, kana ya juyo. Ya kai idanunshi ga sashen da ya barta. Har zuwa lokacin tana nan inda ya barta, har zuwa lokacin kuma kukan take, kanta cikin cinyoyinta. Babu alamar tana da masaniyar cewa kowa ya tashi daga wajen ya barta, kai babu alama ma ta tsinkayi kiran da aka yi musu.

Wankan tarwada, dogo mai tsararren tsayi, ma'abocin ingarman jiki. Cikakkiyar fuska mai yalwar dara-daran idanu da wadatar dogon karan hanci zurr! Kai ka ce saita shi a kai a tsakanin idanunsa.
Ma'abocin yalwar girar idanu kwantacce, gami da gargasa na gashi a kowanne gava mai bukatar hakan a jikinsa. Dogo ne sosai mai nitsatstsen taku da wasu irin idanuwa masu sheki da daukar hankali, kai ka ce ruwan zaiba ne aka diga masu (oily-eyes). Fatar jikinshi shine bayyanannen sirrin kyawun da Allah yai mishi (fata ce irin mai taushin gani a ido). Sai ko wani irin haske (cool) mai nuni da gogayya cikin zuzzurfan ilimin boko, wanda dole ne ga duk wani bakin mutum mazaunin yankunan Birtaniya. Da gani babu tambaya, daga duba na farko, kaga Ba-kanon usuli.
A sannu cikin nutsatstsen takun shi ya karasa gare ta, ya tsaya dai-dai saitin kanta, ya dau kimanin mintina biyu a haka kamar mai nazarin, ya kamata yayi mata magana ne ko a'ah? Baya daga cikin halayyar sa shiga haular da ba tashi ba, kamin daga bisani yayi kundumbala ya yi mata sallama cikin murya mai taushi.
"Kina daga cikin masu tashi kuwa?"

A hankali Lailah ta cira kai, kamar a dan razane. Ta kai duban ta ga sashen da sautin ya fito, ba tare da duban fuskar mai maganar ba, idanuwan nan farare tas sun canja launi sunyi jawur tamkar an gumbuda musu barkono.
Ta mai da dubanta zuwa hagunta da damanta, wayam, babu kowa. Ita kadai ta rage, ta yi hanzarin mikewa ta rataya jakarta ba kuma tare da ta sake duban mai yi mata magana ba. Ta

ce, “Na gode”. Ta wuce babu ko waiwaye.

“Hakika Mallam Nasara kullum kara samun fasahar kirkire-kirkire yake…..”. Laila ta ce a zuciyarta. “Wato jirgin ma yanzu sai dai kawai ka shige shi, ba tare da ka ganshi ba. Kafar shi kafar hanyar da ka fito, sai dai kawai ka ganka cikin wani daki wai shi jirgi mai fuka-fukai. Inama ace yadda yake da fasahar kirkire-kirkire, haka yake da fasahar rungumar kowanne jinsi da zuciya daya, ba tareda wariyar launin fata ba?
A bayyane yake bature bai tava son baki. Ko ya so shin, akwai voyayyen dalili. Muhimmi shine idan har ya san zai samu amfana daga gareshi.
An ce an bamu ‘yancin kai amma ba’a daina bautar damu ba. Turawan Ingila basa aiki, kwance suke a gida, mu din dai har yau mu ke yi musu bauta. Suna kara bunkasa suna kara havaka muna kara durkushewa. Masu fasahar mu sun tattare a gindinsu suna musu bauta. Suna kara bunkasa su. Sun ki suzo su gina al’ummar su. Sun kasa ganewa har yau cewa shi dinnan (nasara) makiyin su ne. Kansa kawai ya sani da al’ummar sa, su ‘bayi’ ya daukesu. A kullum kara like masa muke muna kara dakusar da kan mu. Bamu da abin koyi sai shi da akidojinsa na banza, alhalin halakar da kan mu kawai muke yi.

Ta juyar da idanunta ta wulwula cikin jirgin. Daga farkon shi har karshen shi bakaken fata kawai take hange, musamman kabilar Yarbawa. Suna tururuwar tafiya bauta ma bature. Sun baro iyaye da kakannin su cikin gonakin kauyuka suna noman Doya, Manja da Cocoa. Don samun abin kaiwa baki, basa ko tuno su. Jar fatar usli dake cikin jirgin ‘yan kalilan ne, wadanda yawanci aiki ne ya kawo su Najeriya. Lailah tayi tsaki tare da huci don karin bakin-ciki. To amma me zata iya a kai? Sai ido sai du’a’i.
Tunaninta ya dawo ga tata rayuwar, da dalilin nata balaguron. Tana da yakinin cewa ba bautawa Bature zata ba, kamar yadda mutanen mu suka raja’a a kai a UK. Neman ilmi zata. Domin ta yi wa kanta hukuncin da addini ya tanadar a kanta, wanda ita kanta ba ta sani ba, a yanzun tana nan a musuluncinta ne? Koko ta fita ne?
Bata yarada da cikar imaninta ba….., bata yarda da kanta ba…..! Tana cikin rudani, tana neman mafita,….. tana cikin nadama, tana cikin tsoron rashin cikar imaninta, tana cikin tsoron mahaliccinta, tana cikin tsoron anya Ubangijinta zai yafe mata?
“Sa’eed!” Ta fada cikin rishin kuka. “Sa’idu!” Ta sake maimaitawa cikin karkarwar murya. A yayin da ta zauna a mazauninta na kujera mai lamba (22), hannun dama, na cikin jirgin (British Airways). Kafin wasu irin dumammun hawaye su kara wanke kyakkyawar fuskarta.
Ba kuma tare da ta yi wani kokari na sharewa ko voyewa ba ta ce a fili…..
“Allah ya isa tsakanina da kai Sa’eedu….Allah Ya isa!!!”
Ta sake mai da kai cikin cinyoyinta ta ci gaba da kuka.
Da a ce cikin al’ummar mu ne Lailah ke yin wannan sambatun, la-shakka da an tsaya kallon zararriya-mahaukaciya, amma ga wadanda ba halayyarmu daya ba, ko kallon ta ba su yi ba, kowa ta kansa yake, kowa kansa ya sani.
Babu wanda ya kula ya damu da halin da take ciki sai mutum guda, musulmi Bahaushe dan uwanta, wanda har zuwa lokacin ke bibiyarta da ido, da zuciya.
“…..Budurwa har budurwa…., kyakkyawa har kyakkyawa, mai kyau matuka. Amma Allah sarki! Watakila tana da ‘Psychological Problem”.

Ya raya cikin wasikar jakinsa.

Hakika duk inda musulmi yake, zuciyarshi ta sha baban da ta arne ko ya ya ne. Allah ya halicci dan musulmi da zumunci ga dan uwansa musulmi, ko da basu hada jini ba, wato ko da haduwar kan hanya ce. Musamman a inda suke sune 'minority group' wato a inda suke da karanci. To hakan ce ta faru da ABBAS. Ya kasa dauke hankalinshi daga Lailah, ya kasa daina jin son taimaka mata. Ko ba da komai ba; da son gusar mata da wannan dimbin damuwar da take ciki ko ya ya ne, koda da fatar baki ne. He want to turn this sadness to joy…., he want to make these tears- murmushi.

Jingine yake tuntuni a hanyar da ta raba first class seats da kujerun baya yana kallon ta, amma tsayuwar shi bai hana masu wucewa hanyar wucewa ba.
Ya duba lambar mazauninshi jikin tikitin hannun shi, ya mayar aljihun bayan wandonshi. Ya karaso inda take fuska cike da fara'a ya sake yi mata sallama a karo na biyu.
Kanta na fuskantar taga ne, tana kallon taurarin dake makale a sararin samaniyar subhana, ma'abota haske gami da hasken fitilun lantarki kala-kala da ya mamaye duhun daren, tana iya hangen gine-ginen gidaje, motoci da ma'aikatan birnin tarayya miri-miri kamar abebaden wasan yara, kamar a tafin hannunta.
Juyowa kawai ta yi fuska babu annuri, ba tare da nuna ya fuskanci halin da take ciki ba ya ce.
"Hello lady, can I've my seat here?"
Tare da nuna mata tikitinsa mai nuna cewa shine 'occupant' na kujerar da ke manne da tata, wato mamallakin kujera ta (23).
Hannu kawai tasa ta dauke jakarta da ta dora a 'seat' din ta ajeta kasan kafafunta. Ta mai da kai inda take fuskanta tun farko, wato tagar jirgin, ba tare da ta ce da shi ci kanka ba......
"Taron tsinannu! Taron mugaye, taron mayaudara, macuta, maha'inta, 'yan tofin Allah tsine! Duk kune........ MAZA!!!"
Ta ce cikin zuciyarta. Tare da kai tausasan yatsunta ta yarfe wasu matsiyatan hawaye da suka kara shimfido mata.
"Iko sai Mai-Duka!"
Shi ma ya fadi cikin-cikinsa.
"Watakila bayan 'Psycho-disorder' Mamanta ko Babanta sun rasu, a wannan hutun da taje na 'summer'. Allah sarki! Gaskiya ba karamin rashi bane rasuwar iyaye. Karewa ma, it's the greatest loss of all losses! Shi zai gaya ma kowa ya ya rayuwar dan Adam take wakana babu iyaye? Ya ya dan Adam yake ji idan bashi da wanda zai zo ya rava, ya saki jiki da zuciya ya gaya mishi damuwar shi? Ya ya yake ji idan ba shi da mai daukar nauyin lalurorin rayuwarsa, har ya samu ya mike ya gina kansa?
Sai dai kuma Allah ya kawo mu wani zamani da (dutyn) Uwa ko Uba kawai shine su kawo ka duniyar, amma ko kai kadai za ka iya rayuwa, idan har ka san me rayuwar ke nufi, da inda ta sa gaba.
Sai ka fuskance ta a yadda ta zo, ka manta da komi, ka kasance mai binsu da addu'a.

Aka ba da shelar a daura 'belt' jirgi zai nausa. Kowa ya daura ban da Lailah. Sarkin sa-idon nata ya kuma cewa a ransa.

“To ko dai ba ta ji ne?
Amma kuwa a ganinsa da hakan bai sa ta kuka ba!.
Sai me don Allah ya rage ka ta wani fannin?
Ai dole ba zai hada maka komi 100% ba. Dole idan ya baka wannan ya hana maka wancan don ya jarrabi imaninka ya ga cewa, za ka gode da ni’imomin da yai maka ne ko a’ah?
Za ka butulce ta hanyar kuntatawa kanka? Idan ka gode sai ya karo maka da wata falalar daban ta inda baka zata ba.
Don haka a ganina in nine ke ‘yammata ba zan yi kuka ba. A hakan zan daddage in jure in fuskanci rayuwa. In shiga al’amuran duniya a dama dani domin babu maraya sai raggo. In kasance mai godewa Ubangijina (Yawaita Hamdala) wannan ba shine karshen rayuwar ba!! Kuma babu cutar da Allah ya saukar ‘yammata ba tare da ya saukar da ita tare da maganinta ba, sai tsufa, sai mutuwa.
Sai in ci gaba da neman waraka. Sai dai hakan ba yana nufin zan dakatar da al’amuran ci gaban rayuwata bane, a’ah, ci gaba zan yi, har zuwa sanda (Arrahmanu) Sarkin Rahma ya ga damar yaye mini. Idan kuma ya fi son ganina a hakan? Ow.k! All it takes….!!!”.
Shi kadai yake ta sake-sakensa, har da su watsa hannuwa gami da yarfar dasu tamkar wani zautacce sabon kamu.
Haka ita ma ba ta fasa kukanta ba, ba ta kuma da alamun dainawa. Sassanyan sautin kukan na kara ratsa kunnuwansa, tare da yamutsa tunaninsa a kanta. Yana kara raunana raunanniyar zuciyarsa, musamman kasancewarsa mutum mai matukar rauni a kan tausayin MACE.
Zuciyarshi ta gama lugwigwita, domin tun da yake bai tava jin irin wannan kukan ba, mai girgiza zuciya, mai ratsa kashi da vargo. Tsigar jikinshi ya soma tashi, bai san sanda ya rintse ido ba ya ce.
“Na hadaki da Allah kanwata ki daina wannan kukan!”
Da sauri ta cira kai ta dube shi da jajayen idanunta da suka rine kamar gauta. Yana son yin shisshigi a kan al’amarinta......
“Haka kuke da farko,… nuna tausayi da kulawa, har sai mace ta yi kuskuren fadawa a tarkon ku, sai ku cuce ta ku raba ta da farin cikinta……”
“Kuka na dinga yinshi kenan…. har karshen rayuwata!”.
Magana take a zucci, ba ta san har ta suvuto ta fatar baki ta shiga kunnensa ba. Murmushi ya yi kamar bai ji abin da ta ce din ba.
Ya ce, “ ki daura ‘belt’ din ki”. Ba musu ta jawo ta makala a kugunta. Don kada ya sake damun ta da magana, ta sake mai da kanta cikin cinyoyinta.
Ya dauki ‘earpiece’ da aka ajiye a kowacce kujera ya manna ma kunnen shi, tare da murdo rediyon BBC harshen Hausa yana sauraro. Sai dai a zahiri ya yi hakan ne domin kare kunnuwansa da raunanniyar zuciyarshi daga sautin kukanta, mai lugwigwita zuciyarsa da kassara gavvan jikinsa. He donno why her cry weakens him…..(bai san meyasa kukanta yake raunana zuciyar shi ba). Mai raguwar zuciya ba zai iya daurewa ba sai ya tayata, and he don want 2 be among….. !(baya so hakan ta faru dashi). Jirgi ya mike sosai bayan ya gama ruguginsa mai gigitarwa, ya soma keta hazo ya naushi kasar Birtaniya.

Sai da ya kama hanya sosai ya zare ‘earpiece’ din tare da daukar karamin bargon ‘British-Air’ ya warware ya rufe jikinsa, daga kafadu zuwa cinyoyi saboda wani irin sanyi da ya soma keta

vargon jikinsa. Wanda inda sabo to sun saba.
To haka da yawan al'ummar jirgin suka yi, aka yi light-up wasu suka soma barci. Wannan ma duka ban da Lailah.
Ya mika hannu aljihun bayan kujerar da ke gabansa ya dauki mujallar (TNT) ya soma buda shafukanta, ba don komi ba sai don kawar da hankalinshi daga kan wadda ba ta damu da shi ba, bare al'amarin sa.
Ba ta damu da kowa ba, ba ta san me yake yi ba. She's undoubtedly suffering a zuci, ruhi, fuska da gangar jiki, da al'amarin da duk tunanin mai tunani ba zai tava bashi ba.
A fuska she looks innocent…. A kwayar idanunta tsoro ne karara….. A shimfide kan fuskarta nadama ce tsantsa….. A karance kan siraran levvanta istigfari ne. Zuba suke tarara daga cikin idanunta, hawaye ne.
Baya iya banbance rubutun da hotonan da ke cikin mujallar, baya ganin komi a kansu face kyakkyawar fuskar Lailah, tare da sauraron zazzakan sautin kukanta.
'Yammatan jirgi zuka-zuka, farare kal cikin vingil-vingil din (minis) da rufaffen takalmi, bakaken 'suit' da shudin 'tie'.
"Looking so cool..........."
Ya fada ta hanyar motsi da tausasan levvansa. Sai dai kuma duk gyaran ku da kwalliyar ku you are not as good looking as she is,  (baku kaita kyan gani ba) duk da ita ba ta yi kwalliyar ba. Karewa ma hawaye ne sharkaf, jave-jave a idanunta. Haka ba ta nuna kowacce gava ta jikinta ba, in ka dauke shatin fuskarta.
Sai dai kana iya hango kwantaccen gashi baki wuluk mai sheki da walkiya daga saman goshinta, sakamakon mayafinta da ya dan zame baya cikin rashin saninta. Wanda ke nuni da ba bafullatana ba ce.
Wannan kyan ya kere na fulfulde, kyau ne da launin mutane biyu ya haifar, wato baki da fari (half - caste) da aka fi sani da ruwa biyu, daga uwa da uba.
'Yammatan suka iso layin da suke tare da dan tebirin su mai tayoyi (troller) mai dauke da duk wani nau'i na ababen jika makoshi, tun daga kan shayi, wine (giya), coffee, ruwa, jus da kwalayen taba nau'i-nau'i.
Cike da ni'imtaccen murmushinsu suke tambayar Lailah da ke kife da kai abin da take so.
Ko kallon su ba ta yi ba. Dan sa-idon nata, tuni ya ari bakinta ya ci mata albasa, ya ce a bata ruwa mai sanyi ta jika makoshinta.
Daya daga cikinsu ta ce,
"Hala amarya ce? Honey moon in the heart of England?"
Murmushi Abbas ya yi.
"Yap....... but we 've  a little misunderstanding (mun samu 'yar kankanuwar rashin fahimta) shine take fushi, irin na mata da miji, kin gane?"
Ta yi murmushi ita da abokin tafiyarta ta ce.
"Wannan ba wani abu bane, abu ne da ke faruwa a cikin SOYAYYAH. Idan babu irin wannan babu ingantacciyar soyayyar a zuci. Cool down my friend……".
Ta fadi tana mai dafa kafadun Lailah. Har da dan jijjigata.
Mamaki da haushi ne suka kashe mata baki ta kasa cewa uffan har suka wuce, bayan sun cika mata dan kofin su da ruwan abarba mai sanyi.
"Kulawa ma yabawa ce".

In ji Malam Bahaushe. Idan Abbas na tunanin irin shisshiginsa zai yi tasiri ya samu kulawar Lailah, wadda ke kallon dukkan maza 'naked' (tsirara) babu sauran mutunci babu sauran aminci da su a idanun ta ya yi kuskure. Har suka sauka a Heathrow ba irin shisshigin da bai mata ba, amma uffan ba ta ce mishi ba. Hakanan bata kalleshi ba.
Da yawan ma'aikatan jirgin sun yi zaton da gasken mata da miji ne duk da yadda fuskarta da ma zuciyarta suke a jagule.
Don da za su fita jirgin ma'aikatan na ta yi musu fatan alkhairin 'honey moon' ne cikin kasar su (kamar yadda ya ce) yana amsawa a dokance. Yana binta kamar jela, kamar wani 'body guard' , ko ko mai take mata baya, da kula da al'amarinta.
Duk wannan na faruwa ne cikin Air-port din 'Heathrow' cikin dakikan da basu fice mintuna talatin ba.
Da suka zo kanta wato wajen tuhumar ingancin visa na karshe ga wadanda ba 'yan kasa ba, wanda daga shi sai shigewa cikin garin London. Ya fahimci Lailah ba ta tava shigowa Ingila ba, domin daga ganinta ta fara tsorata daga tsabar binciken da ake yi mata, har ta zamo perpleded (rudaddiya).Ya ce sai ta tsallake wannan 'inter-view' din tukun shine na karshe. Tare da gaya mata cewa ta kula sosai wajen basu amsoshin tambayoyin duk da suka yi mata, ban da dadi ban da ragi, domin hakan na iya janyowa a hanata shiga.
Hankalin Lailah ya kai kololuwar tashi, idan da abin da yake na karshe da ba ta son ji a wannan lokacin, to komawa gida Najeriya ne. A dai wannan lokacin da ba ta san matsayin rayuwarta ba. Ta zo ne domin yin karatun da za ta yi wa kanta hukuncin da addini ya tanadar a kanta.
To amma why a Britain?
[12/17/2019, 17:50] Takori: Idan ilimin addinin musulunci ne ai yana kasar musulunci. Wannan kuma yana daga cikin dalilanta na son vatar da hankalin kowa nata daga tunanin inda take. Ta san nan ne kadai waje na karshe da iyayenta da shi kansa ba za su tava tunanin za ta zo ba, tunda ba ta tava zuwa ba. Kuma bata da kowa.
Sai dalilinta na biyu shine, tana da masaniyar cewa babu kasar turan da ke zaune da al'ummar musulmi lafiya irin Ingila. Kasa ce da ta bai wa kowa dake cikinta 'yancin yin addininsa da walwalarsa, ba tsana ba tsangwama, idan har ka bi ka'idojin da ta shimfida maka. Wannan shine babban dalilin ta na zavar kasar Ingila a matsayin mafaka ga ruvavviyar rayuwarta.

Lailah ce tsaye can gefe a kanta tare da (UK Boarder Agency) masu binciken ingancin bisarta na karshe kamin su barta ta wuce. Tana amsa tambayoyi na karshe. A nutse take tsaf, cikin kamalarta da voye vacin ranta, tana mai amsa dukkan tambayoyin da a kai mata daki-daki da tsaftataccen turanci mara amo. Sun gamsu, sun yarda da zamanta cikin kasarsu baya nufin ha'inci ko vad-da-kama, ko kuma ci - da - gumin - wani. Saima su da za su kara bunkasa tattalin arzikinsu daga asusunta wanda ke cike taf da (sterling pounds).
To nan suka fi kauri, don haka suka daga mata kafa ta wuce. Ta fesar da ajiyar zuciya mai nauyi, domin ta riga ta tsorata da tambayoyin ka-ka uwar ki ta haife ki da suke antayo mata.
Ta yi tunanin idan aka ce ta koma gida a yanzu ina za ta dosa? Ba ta fata, sai ta yi wa kanta ilimin da zai tallafi gurvatacciyar rayuwarta.
Already shi har ya dau jakarshi. Ta dan yi mintuna kamin tata ta iso ta dauka. Suka jero gwanin ban sha'awa kamar mata da mijin gaske zuwa bakin titi.
Hadaddun Jeep-Jeep 'yan gujif-gujif amma wai tadi ne (drop), su Laila ta fara yin tozali dasu a

jere raras suna tsimayen mai hawa.
In kin san wani abu wai shi dacewa, wato (matching) na karshe, to Lailah da abokin tafiyarta ne, wanda har zuwa wannan lokacin ba ta yi mishi wani kyakkyawan kallo ba balle ta tantance kamanninsa.
Shi kuma haka nan ya bi ya nace ya manne kamar wani tsohon maye yana bibiyarta kamar bindi. Ba tare da damuwa da halin ko in kulan da take nuna masa ba.
Ya lura ba ta cikin cikakkiyar nutsuwa, haka nan ba ta san ko 'ina ba. Sai dai kuma ba ta da duhun kai, don ba ta tambayi kowa ba. Ta san iliminta zai mata jagora a ko'ina.
Ta karanta adireshin makarantar da ta zo, (20 Creffield, Earling, London), ta maida takardun inda ta dauko su a jakarta, ta nufi daya daga cikin tasin.
Tun kan ta karasa wani dan motsattsen Bature ya iso gare ta ya amshi jakarta yana kokarin sanyawa a boot.
Hannuwanshi biyu ya sanya ya ciro jakar daga boot din tasin, ya ja Baturen gefe yana murmushi ya ce da shi cikin harshensa.
"Kyale ta fushi take, ka san amare abu kadan sai su hau, su yi fam!"
Baturen ya kyalkyale da dariya ya ce, "To ai kai ma abokina amare lallava su akeyi".
Ya ce, "Ina lallava ta tana kara hawa sai ka ce alkubus, ka gane rigima ce da Madam, ta fi son mu sauka a DUNDEE ni kuma na fi son London. Shin akwai inda ya kai London dadin 'honey moon' ne a Birtaniya?"
Da sauri Baturen ya girgiza kai ya ce, "A'ah, garin sarauniya ai babu kamar shi a duk fadin Ingila".
Ya juyo ga Lailah yana murmushi wadda tuni ta yi mutuwar tsaye.
"To kin ji sai ki daina fushi, ki daura aniyar zaman London da kin ki da kin so. Ina da 'oyster' (katin hawa jirgin kasa) har biyu, zan baki guda. Gara mu bi 'train' yafi saukin kudi.Wuce muje Ma sis.........."
Wannan karon da Hausa yake magana don kada mai tasi ya fahimce shi. Ya zaro fam ishirin cikin wallet dinshi ya mika ma mai tasi, amma ya ki amsa, su kai sallama ya yi gaba.
Ba ta da zavi ban da ta bi shi, domin da jakarta da nashi ya hada ya wuce.
Ba ta tava ganin mutum mai shisshigi irin wannan ba. Haka ba ta tava ganin mutum mara zuciya irin shi ba.
"Uffan ban ce maka ba, kallo  wannan baka ishe ni ba. Amma 'still' baka fasa naci ba".
Ta furta cikin takaici, tare da jan wani matsiyacin tsaki, "Tsuuut!"
Ya ji sautin tsakinta, amma bai san ko me ya sata yin tsakin ba. Ya murmusa har cikin ransa ya ce.
"haka nake kiyi hakuri dani, naci akan abinda na kwallafawa rai, nake kuma son sani. Wanda akafi sani da 'curiosity'. Am curious about you! Yanzu meke damunki? Yunwa ko gajiya? Kada ki damu, I'll cook deliciously for you........ (zan miki girki mai dadi, ni gwani ne wajen girki, lokacinda matata ke raye).

A mamakance  Lailah ta cira kai ta dube shi, wannan karon cikin ido. Ta tsorata, ta mamakantu, haka ta firgita da abin da ta gani cikin kwayar idanunsa (Mohammed sak!).
Amma hakan bai kada ta ba kamar zallar kyau da haiba irin na wannan mai naci. Duk da cewa baki ne amma bakin shi mai kyau ne. Ta ko'ina ba ta inda Ubangiji ya rage sa.

Ba ta san yaushe murmushi ya suvuto daga bakinta ba. Karo na farko da ya ji sautin muryarta ba cikin kuka ba.
Ya lumshe ido yana bude su dukka a kanta, sun kada sun yi jawur. Wannan karon sautinshi ya yi kasa very cool! Ga dukkan alamu tunanin mutuwar matar ya tava zuciyarshi.
A hankali ta ce, “I’m sorry”.
Ya ce, “Na gode”.
A marairaice ya ce, “Ki yi hakuri ki karve ni LAILAH”. (Ya ga sunan ne a jikin passport dinta). Ko da a matsayin abokin tafiya ne, bana nufin komai dake sai alheri Lailah. Lailah ina so na taimaka miki ne, ta wani fannin in taimaki kaina. Kin amince dani Lailah?”
Ta karaya, amma bata son nuna karayar tata a kan MAZA. Tana da tabon su, tana da danyen mikin su cikin ranta, tana da mummunan kullaci a kan al’amarin su;
Sune suka rabo ta da iyayenta da basa hada kaunarta da ta kowa. Sune suka rabo ta da mijinta da aurenta. Sune suka rabo ta da ‘yan uwanta da aminanta...... Sune.....sune.....sune suka yi wa zuciyarta gyambo da har abada ba zai warke ba.
Sune suka yi mata miki mai rudani, suka sanyata cikin rudanin rashin sanin sahihanci da ingancin addininta......
In haka ne ita wace irin wawuya ce da za ta amince ta sake fadawa a tarkon su haka ‘so early?’ (da wurwuri?)
Ta girgiza kai ta furta mishi da karfi, “Never! (Fau-fau). Babu ni babu Da Namiji!”.

Ya yi saurin juyowa idanunshi sun kada sun yi jawur, yana son tantance sanadin wannan ANGER (fushin) da ke cikin muryarta.
“Why Lailah (me ya sa)?” Ya bukata.
“Ai ba duka muka taru muka zama daya ba. Kowa sunan shi yake amsawa. Kada kiyi mana jimilla a rashin kirkin, wannan rashin adalci ne!”.
Ta soma kokarin kwatar jakarta tana magana, wannan karon cikin kuka.
“Am not your wife (ni ba matarka ba ce), so why the disturbance? (meye dalilin wannan takurawar?)
Ka kyale ni in yi tafiyata, ka kama hanyarka in kama tawa, ka yi wa Allah ka rabu dani........”
Kuka ya ci karfinta.
Karfinta ya kare domin ta kasa kwatar jakar. Karfin mace, da karfin namiji. Balle zabgegen mutun irin ABBAS. Wadanda irin su tsiraru ne a cikin al’ummah.
Sai ta tsuguna a nan kan kafafunta ta sa mishi kuka mai gigitarwa, tana rokon shi Allah da Manzon shi ya ba ta jakarta ya yi tafiyarsa ya kyale ta.
Shi ma sulalewa ya yi nan a gabanta a kan gwiwoyinsa idanunshi a rikide, amma ba kukan yake ba.
Numfashinshi ke gwagwarmaya da sauri da sauri. Ji yake in duk duniyar nan za ta taru a kansa ba za ta raba shi da Lailah ba!.
“Hanya mai hadin zumuntar dole….”, in ji ‘yan Magana. Lailah ta gamu da gamonta. Ta ci kukanta ta koshi, ta tabbatar ba zai rabu da ita ba sai dai su kwana a nan. Ta yi tunanin hada shi da ‘yan sanda kawai su yi masu katangar karfe. Daga baya wata zuciyar ta ce da ita, “A kul, shi din kin san wane ne?” Bai yi kama da irin mazan da mace za ta wulakanta ta kwan lafiya ba, bai yi kama da wulakantaccen mutum ba. Haka bai yi kama da wadanda ‘yan sanda za su

girgiza ba, tun da kasa ce da kowa ke da 'yancin kansa.
Ba ta da zavi ban da dangana, ta yi gaba tana huci ya bi ta a baya yana murmushin cin nasara. Suka gangara ta liftar kasa zuwa 'Rail-Station' na Heathrow, suka yi amfani da katunan Abbas na hawa jirgin kasa suka hau jirgi mai zuwa cikin 'Central-London'.

***

12/SAFAR HIJIRIYYAH
Cikin jerin gwanon masu saukowa daga matattakalar jirgin 'Royal Air Moroc' har da Engineer Mohammed Bauchi, fari sol da shi bafulatanin Jama'are, ga dukkan alamu babu tambaya, cikin caftan na 'ash colour' shadda mai taushi da walkiya. Agogon (RADO) baki sai sheki yake cikin tattausar fatar hannunshi da bakin lallausar gashi ya baibaye.
A very serious person (wanda babu alamun wasa cikin al'amarinsa), wato irin mutanen nan masu wuyar sha'ani da rashin walwala. Sai dai fa in ka san wata kalma wai ita 'aji' na karshe, to Mohd. ya mallaki dukkanninta.
Dan kimanin shekaru 35, Mohammed, yana da tsayi sosai da lange-langen jiki na fulanin usli, wadanda suka jiku suka zurfafa suka gogu cikin ilimin addini da na boko.
Ga wanda duk ya san Mohammed Jama'are, ya san shi da wannan halayyan nashi na (seriousness), watau daukar abinda ke gabanshi da muhimmanci a kan komi. Babu abin da yake bai ma lokaci kamar aikinsa da abubuwan da ke gaban shi, na ci gaban rayuwar shi.

Tun kan ya idasa saukowa daga matattakalar ya zura hannu cikin aljihun kaftaninshi ya fiddo wayarshi ya kunna, yana kiran kanin shi Sa'idu ya zo ya tarbe shi.
"Big Bro. isowa haka unexpected?"
Ya fada cikin kasalalliyar murya.
"Da tun jiya ka sanar damu, yanzu haka ina cikin Jama'are, Inna ba ta jin dadi".
"Ow.k, ba matsala, bari in kira Lailah, ai tana gida ko……?"
Shuuuu...... 'network' ya katse, don haka bai ji amsar Sa'id ba.
Ya lalubo lambar ya kira, sunan 'eclairs' ya soma yawo a 'screen' din. Ta yi kara har ta gaji babu agaji.
A karo na biyu ya sake kira. Wannan karon ma ta yi ta vurarinta har ta gaji, 'eclairs' ba ta agaza mata ba.
Cike da kosawa ya sake kira a karo na uku, ta yi har ta gaji ta tsinke don kanta. A serious person, abinki da dama ya ya lafiyar giwa? Nan da nan ya kufula, gaba daya ya kashe wayar don haushi, ya figo jakarshi zuwa harabar 'air-port' ya samu achava ya dane, mai machine ya rike jaka a gabansa, bai tambayi ba'asi ba ya figi babur, ga dukkan alamu wannan oga a kule yake, don haka bai tambayi inda za a ba sai da ya mula don kansa ya fada mishi.

Gidan na daga jerin farko-farko na gidajen unguwar (Fati Mu'azu Links) cikin Bauchin Yakubu, gida ne 'flat' karami hawa daya ma'abocin wadatar shuke-shuken furanni masu launi daban-daban da kamshi daban - daban. Karamin gida ne da ya kunshi duk wasu nau'o'in abebaden jin dadin rayuwa cikin tsari da sanin ciwon naira.
Abin nufi, babu almubazzaranci, babu fariya, haka babu son nuna isa. Komi ka gani cikin gidan mai amfani ne, haka ba a yi dakuna rankatakaf ba adadi ba.
Kwata-kwata dakuna ciki uku ne da makeken falo, sai (boys quater) daga waje da (study room)

mai kunshe da littattafan  da suka  shafi mazauna gidan.
Maigadi ya saki baki bude, ganin maigidansa na sauka daga kan dan achava da jakar kayansa. Ya ciro kudi ba tare da ya kirga ba ya mika mishi ya wuce yana godiya.
Malam Surajo bafullatanin garin Dambam ta jihar Bauchi, kuma amintaccen maigadin maigidan, ya karvi jakar uban gidansa ya yi ciki da ita ba tare da ya jira ubangidan ya gama kiraye-kirayen wayar da yake yi ba.
Ya yi matukar mamakin ganin motar matar gidan na nan. Rufe cikin tamfol, sai dai ga dukkan alamu an jima ba a yi amfani da ita ba, sakamakon kura da ta yi futuk ita da tamfol din.
Motoci uku ne dama a ma'adanar gasunan. Wanda ke nufi tana cikin gidan, tana ganin kiran wayarshi amma don iya shege irin nata ta ki amsawa da gangan.
Ya yi kwafa kana ya tura kai cikin gidan. Ko'ina a bude, ba a sanya makulli ko daya ba.
Sai dai fa ko'ina futuk yake da kura kamar babu halittar dan Adam a gidan. Tuni Malam Surajo ya aje jaka ya fice domin da alama ogan na cikin masifan nashi da ya saba.
Yana tsoron kada bai kar zomo ba a ba shi rataya, don haka ya yi hanzarin daukar buta ya zaga bayi domin gabatar da alwalar sallar azuhur.
Niyyarshi yau sai Allah kadai zai saukar da shi daga fushin shi, duk dadin bakin nan nata…, duk kissa da kisisinar nan nata….., duk lailaya da rarrashin nan nata……, duk taushin hannuwan nan nata........da tausasan levvan nan nata, masu mantar da da namiji duk wani jin kai, takama da mukaminsa. Yau sun yi kadan su sauke fushin takwaran Manzo.
To amma fa ko wajen zama bai gani ba a dai wadannan fututuk din 'leather' din masu kama da an yi wata ba a hau ba.
Babu motsin kowa, babu motsin komi balle 'yan wake-waken nan nata na zabiya  'Nancy Agram' idan tana 'yan girke-girke da kaye-kayenta cikin kitchin.
Jikinsa ya soma yin la'asar. Kai tsaye ya fada kitchin babu ita, ya banka dakin barcin su.... a nan ne idanuwanshi suka gano mai abin al'ajabi.
Kafatanin kayanta da ke cikin ma'adanar kaya gasu nan baza-baza a kan gado. Ga alama an kwashe wasu ne an bar wasu. Ya yi kira da murya mai karfi....
"LAILAH!"
Kiran ya dauki amon da ya karade ilahirin gidan. Ya sake bude iyakar muryar da Allah ya halitta masa.
"LAILAHHH! LAILAHHH!!!"
Shi kansa sai da amsa kuwwar ta hargitsa cikin kwanyarsa.
Davas! Ya sulale ya zauna da mazaunansa bisa carpet.
"Me ke faruwa ne? Ina ta tafi? Babu sallama balle neman izini? Wannan ba halayyarta ba ne, ba ta tava ba, ba ta da kowa a nan sai shi, sai iyayenshi da ke kauye wajen wa za ta je?"
A sukwane ya kara zaro waya ya kira dan'uwansa. Ta yi ruri har ta gaji, ta yi gunji ta yi vurari mamallakinta ya ki dagawa. Da ya sake kokarin kira a karo na biyar, mai abar ya kashe ta gaba daya.
Cike da mahaukacin mamaki ya tattara hankali da kuzarinshi wuri guda, ya mike tare da zuwa ga lokar gado ya dauko makullan motar sa.
Sai a lokacin tunanin Malam Surajo ya fado mishi. Da sassarfa ya fito ya nufi dakinsa, ya idar da sallar azuhur kenan bai kai ga mikewa daga sallayar sa ba.
Ya tsaya daga bakin kofa ya tokare cike da jarumtakar voye tashin hankalinsa da gigicewar sa.

“Malam Surajo ina matar gidan nan ne? Ko’ina a bude, kuma a hargitse. Kuma kura futuk, anya lafiya?”
Malam Surajo ya jinjina kai ya dubi ubangidansa a nutse ya ce.

“Yammacin ranar ta yi min alheri mai yawa, irin wanda ba ta tava yi min ba.
Ta ce, “Watakila Surajo wannan ita ce haduwar mu ta karshe. Na yi tafiya Surajo sai wata rana”.
Ta dauko damin kudi ta bani, ta kuma bani wannan ‘yar takarda ta ce in baka”.
Tamkar wanda kwai ya fashewa a ciki, da kyar ya mika hannun daman shi Malam Surajo ya daga buzun sallarshi ya ba shi takarda nannade cikin ambulan.
Daga inda yake tsaye ya warware takardar idanunshi na ganinta dusu-dusu.

Mohammed Dina…..!
Na yi tunani iyaka tunani, bincike iya bincike, na kasa gano tsakanin ni da kai WANE NE MAI LAIFI?
Da na kasa ganowa sai na bai wa Allah zavi. A daren ne kuma na yardar ma kaina cewa rabuwar mu ita ce mafi ALHERI.
Domin ba za ka tava yafe min ba......nima kuma ba zan tava yafewa kaina ba.
Idan na yi wa kaina hukuncin da ya rataya ga kuskurena, watakila wata rana mu gana.
Ina rokonka idan ka kuma yin wani auren, Mohammed dina....ka yi kokari kada ka maimaita kurakuranka.....ka rage ‘seriousness’ din nan naka…. ka bai wa matarka kulawa da dukkan kaunar da take bukata daga gare ka......
-LAILAH BALLAH!

Kanshi ya daure tam, ya yi zafi rau. Ya kai yatsa baki ya ciza da karfi wai ko barci yake ya farka. Ya tabbatar idon shi biyu.
A karo na biyu ya sake bin kyakkyawan rubutun Laila ya karance tsaf.
“Me na yi miki Lailah? Wane kuskure na yi miki haka da zafi da kika zavi bari na?”
“Ka manta ne? Sarkin tsokanar? Ta saba ‘trick’ kala-kala, yanzu haka tsokana ce kawai take yi ba za ta wuce wurin mahaifiyarta ba”.
Wani dan guntun sako daga zuciyarshi ya tunasar da shi.
Don haka cike da kwarin gwiwa ya linke takardar ya jefa a aljihu, ya bar dakin Malam Surajo yana tafe yana kiraye-kirayen waya domin nemawa kanshi tikitin zuwa Alkahira komi dare.
[12/17/2019, 17:50] Takori: ***
Tarba ta musamman Momi Najla ta shiryawa surukinta cikin babban birnin Alkahira. Tun da ya yo waya cewa ga shi nan a filin jirgi a zo a tarve shi, ita da kanta da kannen Laila biyu Sanah da Najat da kuma babbabn Yayansu Isma’il suka zo taren shi. Isma’il na tuka motar. Autarsu Najat ta zo da gudu ta rungume shi da ta hango shi yana nufo su tana tambayar shi.
“Uncle Pilot za ka tuka ni a jirgi? Uncle Pilot AINA UKHT LAILAHHH?”
Hankalinshi in ya yi dubu to ya tashi, tsigar jikinshi ya mike, ya kidime ya razane. Wannan na nufin, Lailah ba ta wurin su.
Da wane ido zai dubi Momi Najla da ta danka mai amanar rayuwar marainiyar diyarta?
Gwiwoyi a sage, gavovi a kassare, ya zube a gaban Momi ya kasa ko gaishe ta. Isma’il ya

kama kafadunsa ya mikar dashi, sai ya fashe musu da kuka.
Kan ka ce meye wannan Najat ta shiga taya shi, saboda tsabar haduwar jinin su, yana matukar son yarinyar ita ma tana matukar son shi. Ba don komi ba si don kwadayin ya tukata a jirgin sama, wanda shi ne babban burin rayuwarta.
Momi ta matso gabanshi a hankali, jikinta a sanyaye ainun.
“Haba Mohammad, kada ka yi min haka. Me ya faru da Lailah? Wannan ba girmanka bane.......”
Isma’il ya kama kafadunshi, “Abokina Lailah rasuwa ta yi? Ka gaya mana ai mu musulmi ne, dukkaninmu sane muke da cewa ko ba dade ko ba jima rai zai koma ga Ubangijinsa!”.
Ya girgiza kai, amma ya kasa magana. A karo na biyu Momi ta ce.
“Mohd. idan Laila mutuwa ta yi kwananta ne ya kare..........!”
Ya yi hanzarin tura hannu aljihu ya zaro takardar Laila cikin ambulan ya mika ma Isma’il, don baya son wannan kalma ta mutuwa da suke ambatawa Lailansa.
A nutse Isma’il yake karanto ma Momi wasikar Lailah, har ya dasa aya. Dukkaninsu suka yi zuru! Abin tausayi, ba ma ya Mohd. wanda yake jin kansa a victim na duk abin da ya samu diyarsu.
Kanshi ya yi zafi zau da tunanin wane kuskure ya aikatawa Lailah da har ta zavi barinsa? Abin da ko a mafarki bai tava kawowa ba.
Bai tava tunanin dai-dai da rana daya Laila za ta iya rabuwa da shi ba, saboda tubalan da suka gina soyayyar aurensu ba tubala ne da ake amfani dasu wurin yin aure a wannan zamanin ba......
Shi kuwa Isma’il dage kai sama kawai ya yi bai san me yake tunani ba.

***

Wani abin mamaki shine, Lailah da abokin tafiyarta duk makaranta daya suka zo, wato ‘Muslim College, London’.
A tsarin makarantar basa ba da accommodation wato muhalli da abinci, don haka bayan sun gama da registrer  din makarantar (Aaliya Arnall), kai tsaye cikin gari suka fito. Suka yi ‘yan tsince-tsincen dan abin da za su ci, amma basu shiga ‘restaurant’ ba. ‘SAM CHICKEN, chips, da gwangwanin ‘pepsi’ suka samu suka ci. Suka koma cikin makaranta inda aka hada su da wanda zai taimaika masu wajen neman muhalli.

Abbas ya zo neman kwalin shi na Ph.D ne yayin da Lailah ta zo neman kwalin masters. Duka a cikin makarantar ‘Muslim College’.
Babu jimawa suka samu gidan zama na haya na wasu mutanen ‘Lahore’ a (Acton Town), kusa da makaranta, don daga nan ko basu hau ‘bus’ ba zasu iya zuwa makarantar a kafa. Dakuna ciki dai-dai, shi yana a saman bene ita tana kasa.
Kuma a washegari suka fara daukar lectures, maimakon biyan kudin haya duk sati sun dunkule sun bai wa maigidan (Landlord) kudin shekara daya.

Sai ya zamanto wata irin shakuwa na shiga tsakanin Lailah da Abbas, shakuwa mara fasaltuwa. Sannan tsaftatacciya, domin kowanne yana ganin mutuncin dan uwansa. Kuma kowannensu ya san ciwon kansa.
Idan shi ya rigata dawowa zai dafa musu abinci, haka idan ita ta riga dawowa. Tare suke zuwa 'shopping', tare suke zuwa cefane, 'café' da sauran su, rayuwar su gwanin ban sha'awa kai ka ce Yaya da kanwar shi ne.
A cikin gidan ba su kadai bane, akwai mutanen India da wata mata 'yar kasar Somalia. Idan Abbas shi ya yi abinci sai ya kwankwasa mata kofa ta bude ya mika mata, haka idan ita ce ta yi. Duk kokarinta na ta yakice Abbas ta kasa, domin mutum ne har mutum, mai tausayi da kyautayi mai yawan gaske.
Lokutan daukar lakcarsu ba daya ba, don haka a kullum daya ke riga daya dawowa gida. Wanda ya riga dawowa gida shi zai dafa abinci.

Rayuwar London mai cike da abubuwan debe kewa, zaman lafiya da kwanciyar hankali, sai ta taimaka ainun wajen rage ma Lailah dimbin damuwar da take ciki mai neman janyo mata 'psychological depression'.
A wajenta Abbas (kawa) ne, wato (aboki) kuma mutumin da za ta iya tutiya da shi matsayin wanda ya taka muhimmiyar rawa wajen rage mata dimbin damuwar nadamar rayuwar da take ciki.
A hutu na farko da suka samu bayan share watanni uku suna daukar darasi, Abbas ya same ta a dakin ta bayan ya nemi izinin shigowa.
Suka yi wa juna kyar da ido kamin su sakar ma juna dariya. Ya ja kujera ya zauna yana mai fuskantar ta.
"Ko zan samu dan rakiya?"
A sanyaye ta ce, "Zuwa ina?"
"Zuwa 'Lake-Windermerre' a Cumbria, picnick nake bukata Lailah. Kwakwalwata tayi zafi, karatu yayi yawa a cikinta so, ina son samun 'peace of mind' (hutu) koda na yini daya ne.".
Cike da murmushi ta aje littafin da take nazari ta ce.
"Bani minti ashirin na kintsa".
Ya fita ya ja mata kofar ya ce,
"Plz… hurry".

Ta jirgin kasa suka bi zuwa 'Cumbria,' kauye ne awa ashirin da hudu (24 hours) daga London. Ga alama hakanshi zai cimma ruwa ya samu Laila ta bayyana mishi tarihin rayuwarta da ta voye ko zancen, ba ta so.
Domin a ganinta ta riga ta tsere, ta yi nisa da rayuwarta ta baya. Wannan karon ma suka hau jirgin kasa ta hanyar amfani da 'oyster' dinsu. Rataye da 'picnic bags' dinsu. Mai dauke da abinda zasu ci, da wanda zasu sha, 'camera' da sauran su.
Lailah sanye take da bakar 'coat' wadda ta zo har gwiwoyinta da bakin wandon 'channel'. Ta yane fuskarta da kankanin gyale daga 'pashmina'. Ta saje tsaf da turawan Ingila, ta yadda in ba fada maka aka yi ba ba za ka iya tsince ta daga cikin su ba.
Yayin da Abbas ke sanye da shudiyar suwaita long sleeve da bakin 'jeans' shima, kai da ganinsu ka ga 'students' zaunannun Birnin Sarauniya.

Zaune suke a bakin ‘Lake’ din kafafunsu duka cikin ruwan. Abbas ya dube ta da kammalalliyar fuska, ta samu kanta da jin wannan mutum kamar Yayanta Isma’il, zuciyarta ta amince da shi. Ita kanta bata san dalili ba.
Ya ce, “Lailah is high time in ji abin da ya rabo ki da gida, ko zancen wani da ya shafe ki baki tava yi min ba. Jikina ya bani ba haka kawai cikin dadin rai kika zo karatu kasar nan ba.  Is this friendship?”
Ta ce, “Zan gaya maka Abbas, duk da cewa ban san karvar da za ka yi wa labarin ba”.

****

FARKON LABARIN

Haduwata da Mohammed, a babban filin jirgin saman Egypt  ne (Cairo International  Air-port), za mu raka mahaifinmu zai tashi zuwa kasar Najeriya. Mahaifinmu dan uslin kasar Najeriya ne, dan Kano, amma mazaunin Egypt, tun daga zuwa karatu ya samu aiki saboda kyawun takardunsa. Likita ne kwararre a ‘general hospital’. Ya yin da mahaifiyarmu ta kasance ‘yar usulin kasar Egypt. Ya aure ta tun auren saurayi da budurwa.
‘Patient’ dinsa ce tana da ‘ulcer’, ya kasance duk wani ‘treatment’ dinta a hannunsa yake.
 Suka gina ma zuciyoyinsu wata irin soyayya wadda daga iyayenta basu samu wata matsala ba, wai don kasancewar shi ba dan kasa ba.
Shi daman maraya ne ba uwa ba uba. Sai Baffanninshi biyu a Kano. Suka yi aurensu a nan Egypt ya sayi babban gida a can suke zaune cikin soyayya da amana.
Isma’il shine babban dansu, sai ni, sai ‘yan biyun Momi Sanah da Najat. Mohammed matukin jirgin sama ne, wannan shine babbar matsalar da muka fara cin karo da ita a rayuwar aurenmu. Shi Mohammed dan asalin garin Bauchi ne, wani gari Jama’are. Su biyu kacal iyayensu suka haifa daga shi sai kanin shi Sa’eed.
Akwai  rata sosai ta shekaru goma tsakanin Mohammed da Sa’idu. A lokacin da aka haifi Sa’id, girma sosai ya cimma mahaifinsu Malam Yahya, wannan ne dalilin da ya sa Sa’eed ya dawo hannun mu da zama lokacin yana karatu a Tafawa Valewa University Bauchi.
Mohammed ya ware ma Sa’eed dakin zama a boys kuaters, ya fara karatunsa cikin nasara. Inda yake karantar ‘Geography’. Wankan tarwada ne mai kyakkyawar sura, yana da kazar-kazar da fara’a mai yawa, yana da kirki da ladabi ga dan uwansa, da ni da nake matsayin matar Yayansa.
Kirkin Sa’id ne ya sa muka zamo wasu irin aminai, duk abin da ke damuna kafin Mohd ya sani na fadawa Sa’id.
A ganina shine mai lokacina, saboda mijin bana jin dadin sa. Mohammed, wani irin mutum ne tough, serious, ba shi da lokacin iyalinsa ayyukanshi na tuki suna gaba da komai.
Sai ya yi watanni uku yana yawo a duniya. Da fari na uzurce shi da cewa yanayin aiki ne, amma a matsayina na mace mai jini a jika wannan aikin na Mohd. na ci min tuwo a kwarya.
Farkon auren mu ya zamanto ba haka bane, don a lokacin yana fafutukar neman aiki ne muka gamu. Da ya samu aikin ne abubuwa suka sauya, don haka zuwan Sa’id gidan mu ba karamin farin ciki hakan ya haifar min ba.

Digirina na farko na yi shi ne daga jami’ar Al-Azhar a kan Falsafa (Philosophy). Ina matukar son

mijina kwatankwacin yadda yake so na. Domin a kan soyayya da kauna muka gina auren, tun mahaifina yana raye. Mohammed ya dauki son duniya ya dora a kaina, sai dai kuma abin takaicin ba shi da lokacin da kowacce mace take bukata tare da maigidanta, yana hadawa kanshi zafi da yawa kamar shi kadai ne matukin jirgi a duniya.
Daga baya ne Sa'id ke yi min bayanin ai bayan Virgin Atlantic da yake wa aiki wasu kamfunan daga ko'ina irin su MEA, KLM, Royal Air Moroc, da sauransu suna daukar shi haya saboda kwarewar sa.
Amma a matsayina na matarshi abokiyar rayuwarshi bashi da lokacin da zai zauna ya yi min wannan bayanin, sai dai kullum ya ce bana yi mishi uzuri da yawan ayyukan da ke gabansa.
Sa'eed ya dawo makaranta a wani yammacin Litinin ya same ni a kitchen, yai sallama ya shigo, ya karve ni a firar dankalin da nake yi.
Ya ce, "Gaskiya Aunty Lailah ya kamata a samo miki yarinya mai aiki mace kina wahala fa, ke kadai a gidan nan".
Na ce, "Da hakan za ta faru da na yi murna".
Ya ce, "On weekend, (cikin karshen sati) zan je Jama'are zan fadawa Hajiya za a samu insha Allah".
Na ce, "Na gode".
"Yaya bai yo waya ba? Ina so in mishi zancen kudin 'registration' ne. Kin san an ce shekarar kwana gashi har shekara ta zagayo za mu shiga level 300".
Na ce, "Har nawa ne?"
Ya ce, "Bai kai 20 thousand ba".
Don haka a daren ranar na kirgo kudin registration na ba shi cikin kudin da Mohammed ke bar min.
Ban rasa ci ba, ban rasa sha ba, ban rasa suttura ba, amma na rasa soyayya da kulawar mijina.
Sai Sa'id ya zamo wani mutum mai kula da ni da debe min kewa, ta hanyar irin wasannin nan na kanin miji da barkwanci ga matar Yaya.
Shakuwar mu da Sa'eed din har ta zarta misali, saboda yadda yake nuna min kulawarshi a kan al'amura na da damuwarshi a kaina.
Idan ka ganmu a kanti muna sayayya ko a kasuwar wunti muna cefane sai ka dauka mata da miji ne.
A satin muka shirya tafiya Jama'are ni da Sa'eed gaida Hajiyar Mohd. Hajiya ta rasa inda za ta sani don murna, ta kuma rike ni sai na kwanan mata biyu. Don ita kanta wannan yanayin aikin na Mohd. na damun ta, don dai ba yadda za ta yi ne.
Da daddare mun yi shirin kwanciya Hajiya ke yi min nasiha cikin hikima na in kara hakuri da yanayin aikin Mohd. Ita kanta ta damu, to amma yaya zamuyi? Tunda dai hanyar abincinshi kenan, kowa da inda Allah Ya tsaga mishi hanyar abincinsa.
A raina na ce, "In ban yi hakurin ba ya ya zan yi? Ya riga ya rabani da uwata da 'yan uwana, kuma ba shi da lokacina.
Idan dai don kudi ake wannan aikin babu samar ma kai da zuciya, kwakwalwa hadi da gangar jiki hutu, sai in ce ban san inda Mohammad zai kai kudin da yake samowa ba".
A kan hanyarmu ta dawowa Sa'eed ya dukufa lallashina, don ko fuskata mutum ya kalla ya san ina cikin matukar damuwa.
Yake ce min, "wata rana sai labari Aunty Lailah, ki kara hakuri a kan naki na da, shi Yaya da

kanshi zai gane wata rana ba ya kyautawa, ya ragewa kanshi aiki ya rungumi iyalinshi, in kuma kin amince in yi mishi magana to, duk da yana daga cikin irin mutanen da da wuya ka doshe su da irin hakan".
Ban ce komi ba, abin da na sani shine, auren Mohammed ya fice mini a rai, burina tunda ba shi da lokacina, to ya sallame ni in koma cikin 'yan uwana gaban mahaifiyata, duk da bai tava iyakance min zuwa ganin su ba.
Shakuwar mu da Sa'eed sai abin ya kara gaba. Ya zamanto girki ma wannan tare muke yin sa, kallon kwallon kafa da daddare duk tare muke yi, kamar wasu mata da miji.
Har na kan kissima a raina wani lokacin ni kam da ma Sa'eed aka aura min da na more. Duk da yake yaro dan shekaru ashirin da bakwai ya sn yadda zai yi ya tafiyar da mace da nuna mata abin da ta fi so a gidan aure, wato soyayya da kulawa.
Za ka so ganin mu muna kallon ball har da tafawa, saboda shi dan 'Arsenal' ne ni 'yar 'Real Madrid', mu takarkare mu yi ta musu kowa yana kare kungiyar sa.
Mu yi girke-girke mu ci, a karshen mako mu yi 'sanitary' mu gyare ko'ina na gidan mu.

Yana da yawan zama a 'study', musamman lokacin jarrabawa ba ya wasa. Yaro ne haziki mai kirkin gaske da saurin shiga rai.
A satin da su Sa'eed suka fara zangon karatunsu na farko a level 300, Mohd ya iso, kai ka ce ba mijina ba, ban yi wani doki ba balle in yi wasu shirye-shirye domin tarbarsa.
To shima din bai damu ba, don ya san shi din har kullum mai laifi ne a gare ni, bayan a ganin sa yana sauke duk wasu nauyi da Allah ya dora masa a kaina idan ya zo bayan kowanne watanni ukku.
Ya rage nawa in dubi yanayin aikinsa inyi mishi uzuri ko kar in yi, don shi kan ga yadda ya nuna ya gaji da kananan korafe-korafen da nake damun shi dasu a kan rashin sa cikin gidan, tun da dai ba dauka na zai yi ya goya ya dinga yawo dani cikin duniya ba. Bai kuma iyakance min zuwa ga 'yan uwana a duk sanda na so ba.
To amma mene ne auren? Ina da tambaya, 'yan uwana mata. Shin wannan shine ginshikin auren ko me? Ba na samun ginshikin aure, don haka am not satisfied with my husband.
Don haka Mohammed har ya gama kwanakin shi biyu ya koma bai samu wani edcellent welcome  daga gare ni ba, kamar yadda shi ma ya ke complaining(korafin) na hana shi hutawa, na dauki vacin ran banza da wofi na daurawa kaina.
Idan bai fita ya nemo min ba me zai ba ni? Ko nufina shine ya jive a gida kada ya yi amfani da damar da Allah ya ba shi na morar iliminsa? Mutane nawa ne suke neman 'chances' din (damar) da yake samu basu samu ba?"
"Su 'chances' ba a hakura da wasu don a huta, a kula da bukata da rayuwar iyali?" Na tambayeshi watarana.
Ya ce,
"Lailah you'll never understand me, (bazaki tava fahimtata ba), tunda kin riga kin damu kanki. Na gane ki, irin matan nan ne da suke so miji ya like musu kamar kaska, kin san da irin aikina kika aure ni, a kan me yanzu za ki uzzure ni?"

Don haka har ya koma bamu yi rabuwar arziki ba.

Ta duba agogon hannunta kana ta dubi Abbas.
“Ya kamata mu tafi gida haka yamma ta yi sosai”.
Abbas ya zare kafafunshi daga cikin ruwan suka mike suna harhada kayansu.
Ya ce, “Ni dai na so ki karasa min labarin nan a yau”.
Ta ce, “Some other tym, bana jin dadin jikina sosai, sannan ga yamma ta yi”.
Suka jero suna tafiya cikin hirarraki kanana, sai ka rantse mata da miji ne”.

****

Abbas ne a kitchen din gidan yana kiciniyar daura masu sanwar abinda za su ci da daddare. Ba komi bane ‘source’ ce da za a ci da biredin alkama.
Ya kammala y rufe komi ya gangara kantunan dake kasa ya mika ‘yan sisinsa (penny) ya sayo biredin ya dawo kitchen din, ya dauki na Lailah da nufin ya fara mika mata kafin ya dawo ya dauki nashi.
Ya iso jikin kofarta ya kwankwasa, shiru ba a amsa ba. Ya sake kwakwasawa a karo na biyu......
A wannan lokacin da ya dan saurara, sai ya jiyo tana kakarin amai kamar fitar rai.
Don haka ba tare da wani tunani ba ya murda kofar a sukwane ya isa gefen gadon da ta jike da amai, ya aje plates din da ke hannunsa a gefe.
Ya ce, “Lafiya Lailah?’
Cikin tsananin tashin hankali da firgici bayyananne, zane varo-varo a kyakkyawar fuskarsa.
Ta yi mai nuni da ya ba ta ruwa, ya dauko gorar ruwa a ‘bed-side fridge’ dinta ya valle hancin ya mika mata, ta kuskure baki ta wanke fuska. Ta koma jikin filo ta kwanta tana maida numfashi a galabaice.
Duk abin da ta saka ma cikinta a yinin ranar ta amayar da shi, har da wani kore-kore cikin aman. Sabida babu sauran abinda za’a amayar din.
Ya zage tukuru yana gyara wajen bayan ya tattara zanin gado ya jefa a bokiti.
Sai da ya gama aikin aman tas ya fesawa dakin ‘room-fresh’ mai dadin kamshi, zuwa lokacin Lailah ta fara rawar dari, hakoranta sun soma karo da junansu.
Ta ce, “Rufa min bargon nan, Abbas sanyi...”
Ya dauki lallausan bargon ya rufa mata, amma ba ta daina rawar darin ba sai ma abin da ya karu.
Don haka ya gangara kasa ya koma nashi dakin ya dauko nashi bargon ya kara mata. Ya koma kan kujera daya kwallin-kwal dake cikin dakin ya zauna cikin kulawa ya ce.
“Za ki iya kokartawa muje asibiti?”
Girgiza mishi kai ta yi alamar “A’a, ba za ta iya ba”.
Lallai lafiya… uwar jiki, lokaci daya ta rafke Lailah a daki, shima ta hana shi hidimomin gabansa, balle halartar ‘lectures’.
Ya je dai ya ba da edcuse a kan Lailah, amma shi ba shi da hujjar da zai bayar. Don haka ciwon Laila tsawon sati guda ya shafi karatun sa ba da wasa ba.
Wannan ba shine a gabansa ba, lafiyar kawarshi, abokiyarshi, aminiyarshi Lailah ne.

A rana ta bakwai ne dai ya takura mata ala dole ta mike, duk ta rame ta zaizaye dama jikin ba wani jiki ba.

Ya dauko jibgegiyar coat dinta ya jibga mata, ya manna mata bakar hula da socks na hannu.
A wannan lokacin na karshen watan January, lokacin da London ke fama da snow , har ya soma tunanin rashin sabo da yanayin ne ya haifar ma da Laila wannan mugun zazzavi da vomiting. Wato (amai)
To amma ina ruwan sanyi da vomiting (amai)? Haka dai suka gangara kasa, suka hau bus, ko da yake daga nan ma unguwar da suke (Acton Town) za su iya karasawa NHS da kafafunsu, sai dai don baya so ta jigata ne.
Abinki da dalibai ma'abota inshora, nan da nan su kai 'booking' ganin doctor, aka soma daura Lailah a kan gwaje-gwaje, wanda ya kai su hard a su dibar fitsari, jinni, don binciken zahirin abin da ke dmaun ta.
"Congratulations!".
Siririyar Baturiyar ta ce da shi tun kamin ta iso kujerar da suke zaune. A tsammaninta su din mamallakan juna ne (ma'aurata).
Ta sake cewa, "Congratulations, nan da watanni bakwai muna maka albishir din mallakar bouncing baby".
Daga shi har Lailah ba su fahimce ta ba. Don haka ya kama hannun Laila kada ta fadi suka koma ofishin doctor.
Ya ce, "Meke faruwa ne doctor? Me ke damun Lailah?"
Ya washe baki shi ma cikin yi mishi albishir din cewa matar shi na dauke da juna biyu ne".

Wata kara da Lailah ta saki ta kuma sulale a nan ta fadi sumammiya ta razana su. Abinka da wadanda suka san muhimmancin patient, nan da nan aka yi rubdugu a kan Lailah aka kuma umarce shi da ya fita.
Ya dawo bakin kofar dakin likitan ya jingina da bango, hankalinsa ya masifar tashi, ya rasa dalilin suman Lailah don anyi mata albishir din kasancewar ta mai juna biyu.
Ba da auren ta ba? Me zai dame ta don an ce tana da juna biyu? Duk da can a karkashin zuciyarsa wani dunkulallen abu ne ya tokare kirjinshi, tun sanda Lailah ta soma ba shi labarin rayuwarta, ya kuma fahimci tana da aure, ya soma canja tunanin shi a kanta, ya kuma yi dalilin da ya sa ya fara ja baya da ita, amma tun da ta fara ciwon ya samu kanshi da son taimaka mata.
Amma bai ga dalilin da don an ce tana da juna biyu za ta daga hankalinta ba. Al'amuran rayuwarshi gaba daya sun canja, tun haduwar shi da Lailah.
Yana fama da wani lamari mai girma cikin zuciyarshi a kanta, shi kadai ya san halin da yake ciki a kan Lailah, dare da rana, wuni da safiya. Tun a ranar da ya soma dora idanunshi a kanta.
Hatta a marigayiyar matarshi bai tava tsintar kanshi a al'amarin dake faruwa da shi a yanzu game da Lailah ba.
Ba ya tantama soyayya ce mai girma, kuma mara adalci. Tun da dai wadda ake mawa matar aure ce ga wanin sa. Don haka ya san cewa al'amarin ba zai tava yiwuwa ba.

Kwanansu biyu a asibitin ana yi ma Lailah karin ruwa da kulawa ta musamman. Tunda Lailah ta dawo cikin hayyacinta kuka take, wanda bai san dalilin sa ba.
Rarrashin duniya Abbas da 'nurses' sun yi amma kamar kara izata suke, har aka sallamo su suka dawo gidan da suke zaune Lailah ba ta bar tsiyayar da hawaye ba.

Ya yi sallama a kofar dakinta dauke da plate na soyayyar ayaba (plaintain) da apple (tuffah) a cikin leda, da fresh milk har da 'ya'yan inibi.
Ya ja tebir ya dora mata ya sanya ta a gaba a kan dole sai ta ci, ta soma ci kamar mai cin magani, ta rasa inda za ta sa kanta. Rabonta da abinci har ta manta.
Kuka take wurjanjan a lokacin da take rokonsa da ya taimaka mata a cire cikin da ke jikinta.
Abbas ya sa mata ido yana kallon ta, a ladabce ya ce.
"Lailah".
Ta saurara da kukan ta dube shi tana shessheka.
"Ke fa da bakin ki kika gaya min cewa kina da aure?".
Ta daga mishi kai bayan ta sa havar kallabinta ta fyace wata matsiyaciyar majina.
"To 'why' (meyasa) za ki ce a kashe rai alhalin da ubansa?"
Maimakon ta ba shi amsa sai ta kara tsinkewa da kukan, na yau har ya fi na kullum, tamkar wadda aka yi wa bushara da rasuwar uwa da ubanta.
"Allah-kareem!"
Ya furta cikin zuciyarshi. Ji yake kamar ya dauko damuwar Lailah ya aza ma kanshi don ta huta. Shi bai ga dalilin da za a cire cikin da yake da uba ba. Koma babu uban shi a haife dan a ba shi yana so.
Babban burin shi kenan a duniya, ya ganshi da dan kanshi, wanda kuma gurin haihuwar ne Allah ya karvi ran matarsa.
"Lailah idan ba kya son dan ne ni ki haife ki bani, wallahi Lailah baki san yadda nake addu'ar Allah ya bani da ba.
Idan Ubangiji ya baka da ya yi maka kyautar komai, wadda wani ko wata bazasu tava baka ba. Ki tuna ke musulma ce, wadda ko ba dade ko bajima za ta tadda Ubangijinta.
Shin me za ki ce da Ubangiji a bisa wannan muhimmiyar kyauta da ya yi miki kika butulce? Baki da tabbacin cewa wannan shine kadai kwanki a duniya. Wasu suna nan suna nema ruwa a jallo koda zasu karar da  dukiyoyinsu, amma Allah bai basu ba
A matsayina na dan uwanki musulmi ina mai tunasar da ke cewa, idan kika zubar da ciki kamar kin kashe rai ne, kuma wallahi Allah ba zai barki haka ba.
Idan laifi uban dan ya yi miki za ki huce a kan dan tayin dake karkashin mahaifa kin yi babban kuskure, wanda ko ba dade ko ba jima wata rana za ki yi nadama.
Idan bakya so ina mai shawartarki ki daure ki haife, ni Abbas ina so, ki bani. Zan yi mishi uba, idan bakya son uban shi, ko idan wani laifi uban nashi ya yi miki har ta kai ki ga yin wannan gurvatacen tunani."
Lailah ta juyar da kai cikin matse hawayen idanunta. Ga dukkan alamu ranta ya soma sanyi. Ya ci gaba da yi mata nasiha hadi da ba ta misalai kala-kala, har ta saddakar da tana son fayyacewa Abbas dalilinta na yin hakan.
A ganinta idan ya ji dalilinta shine mutum na farko da zai goya mata baya ta yi abin da take da nufin yi.
[12/17/2019, 17:51] Takori: ****
Matsala ta biyu da muka kara cin karo da ita ni da Mohammed, ita ce matsalar rashin haihuwa. Shekarun mu biyar tare amma haihuwa shiru, babu ita babu alamunta.
Daga baya ma Mohammed ya zo yana zargina da yin 'planning' a voye, bayan kuma a zahiri ba hakan bane.

Muka koma biye-biyen teburin likitoci suka yi ta zakule-zakulen su har suka tabbatar matsalar daga gare shi ne.
Idan har yana son haihuwa to yana bukatar ai mishi aiki, don haka daga ni har shi muka tattara maganar haihuwa muka yi watsi da ita. Sai dai duk inda Mohd ya ga 'ya'ya sai ya karar da lokacinshi a kansu.
Na lura Mohd na matukar jin dadin yadda alakata take da Sa'eed, domin dan gaban goshinsa ne, su biyu kacal iyayensu suka haifa kuma mahaifinsu ya jima da rasuwa.
Yana so ya zo ya tadda mu a falo muna ta nishadi, tunda dai shi baya da lokacin mu.
A wani weekend Sa'eed yake yi min zancen yarinyar da zai aura Zaliha, ajinsu daya ne a makaranta, yana son in fadawa Mohd. don gidan su Zalihan sun takura idan ba zai fito ba za su bawa wani. Shi kuma yana son yarinyar sosai.
Na ce,
"Sa'eed da rigima kake, kana fafutukar kwalin karatun farko za ka hada ma kanka aure?"
Ya ce,
"Wallahi da gaske nake Antina, ina matukar son Zaliha, idan kuma ban same ta ba ban san ya ya rayuwata za ta kasance ba, ku taimaka mani".
Na ce, "Ni don ta ni ai mai sauki ce, amma Yayanka ka fi kowa sanin shi".

Ko da Mohammed ya zo, bayan wasu watanni kamar yadda ya saba, na yi mishi zancen, bai wani ba zancen muhimmanci ba, don haka ya koma ta vangaren Hajiya.
Na ke jin ita ce ta tusa Mohammed din a gaba sai da ya amince aka yi ma Sa'eed baiko da Zaliha, amma aka ja lokacin sosai zuwa sanda za su kammala karatun su.
Sa'eed ya dauko Zaliha har gida ya kawo min ita, yarinyar kyakkyawa amma ta waye da yawa. Na yi mishi maganar hasashe na ya ce "haka nan nake son abata".
Gab da kamawar watan bikinsu muka samu wani mummunan labari, wato hatsarin Zaliha da iyayenta a kan titin Abuja, duka babu wanda ya tsira.

Hakika Sa'eed ya shiga matsanancin tashin hankali wanda ta kai shi da furucin babu shi babu aure a duniya.
Shekarun mu biyar da aure Sa'eed ya tafi NYSC jihar Cross-river. Don haka sai na kasance cikin kadaici da kewa. Da dai kadaici ya isheni sai na tattara na tafi Egypt wajen mahaifiyata, bayan na nemi izinin Mohammed ta waya.
Zamana da 'yan uwana sai ya zamo magani ga dimbin damuwar da nake ciki. Momi ta kasa daurewa don ganin muguwar ramar da nake yi. Ta sani a daki a wani maraice tana tambaya ta. Ban voye mata komi ba na zayyane mata matsala ta. Momi ta ce,
"Tun farko ke kika kawo yaron nan Lailah kika ce kina son shi, alhalin kin san yanayin aikinsa, ban ga dalilin da za ki daura ma kanki damuwa yanzun ba.
Idan har kina ganin ba za ki iya ba, to tun wuri ki nemi da ya sauwake miki".
Na yi jim! Ina tauna maganar Momi, in ce Mohammed ya sake ni? Abune da ba zan tava iyawa ba, domin dai auren soyayya muka yi, duk da halayen sa na rashin kulawa da soyayya a gare ni 'still' ina son kaya na.
Don haka har na koma Bauchi ban yankewa kaina shawarar komi ba, tunda dai 100% na yarje ma zuciyata ina son mijina.

Ginshikin aure kam ba na samu, wato auratayya. A hankali dai na fahimci jinsin mu ba daya bane, yana cikin jinsin mutanen da seduality wato auratayya bai dama ba, ya yin da ni kuma nake a rukuni akasin hakan.
Dole haka na daure ina ci gaba da cin dan uban hakuri. Da dadi ba dadi muna zaune a hakan. Rashin Sa'eed sai ya zamo min kamar rashin babbar aminiya. Ya shiga jikina sosai, mun amincewa juna, duk wata matsalar junanmu da junanmu muke shawara, na kuma lura sosai Mohd ba karamin jin dadin hakan yake ba.

Ta duba agogon 'swatch' dake daure a fatar hannun ta, ta dubi Abbas, "lokacin sallah yayi, mu je mu sauke farali". Ya sauke tagumin da yayi da hannayenshi biyu yana sauraronta, ya mike yana duba nashi agogon shima.
****

Kwance yake a mike bisa doguwar kujerar da ke karamin falonshi yana nazarin jaridar 'Daily-Trust', sai dai da ganin irin kwanciyar da ya yi ka san ba ta lafiya ba ce, alal hakika yana cikin matsananciyar damuwa.
A karo na wajen dari da hamsin kenan, ya sake 'dialling no Lailah, kamar yadda computer ta saba yi mai vavatu yau ma vavatun ta shiga yi mishi, cikin sanar da shi layin a rufe yake.
Kararrawar shigowa falon ta yi kara, da kamar ba zai kula ba, ya dai daure ya mike ya isa ga kofar ya bude.
Ya bayyana a falon cikin kyakkyawar shiga ta caftan na farar shadda mirrow, suka yi ido hudu da dan uwansa da baya da ya shi a duniyar baki dayanta.
Ya matsa kadan ya ba shi hanyar wucewa suka zauna a tare cikin kujeru masu fuskantar juna.
A saluve Sa'eed yake kamar wanda ya sha duka, ya ce, "Yaya har yau ba labari?"
Bai saurari amsar shi ba ya ci gaba da cewa.
"Ni ina ganin a kai zancen cigiya kafafen yada labarai".
Mohammed bai amsa ba, illa ya mike ya isa ga kitchen ya fiddo ma dan uwanshi abin sha mai sanyi na'ya'yan itacen 'tropical juice' hade da tambulan, don ga dukkan alamun shi a gajiye yake da uwar tafiyar da ya niko tun daga jihar Cross-river.
Hakika yana tausaya ma dan uwanshi halin da ya shiga a dalilin vatan matarshi, wanda kuma shi ne sila.
Anya idan Mohd ya ji irin cin amanar da ya yi mishi zai tava yafe mishi? Idanuwansa suka kada jajir, amma sun kasa tsiyayar da hawaye.
Ya tashi tsamo-tsamo da shi ya nufi hanyar baskwata, don ganin ga dukkan alamu Mohd din bai son damu yanzu cikin halin da yake ciki.
Wayar shi dake gefe ta yi ruri, ya mika hannu a kasalance ya dauka. Isma'il ne yayan Lailah. Bayan sun gaisa ya ce,
"Babu labari a nan Bauchin har yanzu? Mu ma nan mun baza cigiya har a sauran kasashen da ke makotaka damu wadanda take da kawaye a can, ba amo ba labari".
Mohammed ya ce
"Nan din ma babu, amma yanzun nan Sa'eed ya kawo min wata shawara a kan na baza cigiyar a nan gida Najeriya".

Suka yi sallama kowannen su zuciyar kamar-kamar me.

A iyaka tunaninsa, bai san laifin da ya yi ma Lailah takamaimai ba, lafiya kalau suka rabu. Sai dai da ya yi nazarin wasikarta ya fahimci a kan halayyar da yake mata ne ta gwammace ta yi nisa da shi, tun da ta kasa magantawa kanta, shima ya kasa maganta mata.
To a yau ga shi a dalilin halayensa aikin ma gaba daya ya kasa a dalilin rashin ta.
Daman an ce baka sanin muhimmanci da amfanin mutum sai ranar da ya suvuce maka. Ya rasa inda zai sa kansa a dalilin rashin Lailah, ya yi nadama matuka da irin halayen da yake yi mata wanda ba sau daya ba, ba sau biyu ba ta sha gaya mishi cewa ba ta so, ya daina.
Amma bai dainan ba, sai sanda ya rasa ta. Shi da dan uwanshi suka shiga kafafen yada labarai na garin Bauchi suka sa cigiyar Lailah har da hotunanta.
Amma har kwanaki suka tura shiru kamar an shuka dusa. To ina ga mahaifiyarta da ta tsugunna ta haife abarta?

****

Ya kwankwasa kofar dakin a hankali rike da karamin ‘tray’ da ya dauro  karamin ‘tea flask’ da kayan shayi.
Ta zo ta bude cikin nutsuwa ta yi wani irin fari ta rame ta zuge duk a lokaci daya. Ya aza ‘tray’ din a kan wani dan karamin tebir da ke dakin, ya ja kujera ya zauna ya soma hada mata shayin, ya kammala ya shiga firfitawa.
Kallon shi take cike da tausayin kulawa da taimakon da yake yi mata a matsayinshi na wani mutum da basu hada dangantakar komi da shi ba, face abokin kan hanya kadai.
“Abokin kan hanya?”
Ta kalubalanci furucinta. A gare ta zuwa yanzu matsayin Abbas ya zarta wannan. He is someone she respect most!.
Ya shiga zuciyarta da yawa, ta yadda har tunaninta ke canzawa a kanshi, zuciyarta na gayyatar shi da wani matsayi mai girma. To ita kanta ba ta da ‘standing’, abin nufi. Ba ta san matsayinta ba balle ta soma tunanin irin wannan, tana da aure ko babu? Ba ta sani ba.
Har ya kammala firfita shayin ya miko mata ba ta farga ba, ta yi nisa a tunanin ta.
Ya ce, “Lailah!”
Ta yi firgigit ta ankara. Ya mika mata shayin wanda ba ko tantama tana sha za ta amayar da shi.
Ya kan ce, “Ya fi babu dai tun da ko ya ya ne wani zai zauna a cikin hanjin cikinta”.

Abbas gwanin jinya da karfafa gwiwa, Abbas mai kyau, Abbas mai kirki…ya kan nuna mata wannan ba komi bane, babu wanda baya fuskantar challange  (kalubale) a rayuwa. And is up to us to accept such challenges mu bita da duk fuskar da rayuwa ta zo mana.
Ya ce,

“Ni tashi na yi ba Uwa ba Uba Lailahhh. Haka nai ta gararramba a gidan wan mahaifina, sai dai na kasance daga cikin hazikan yara, duk da gararramba ta.
Da na kare karatun sakandire gwamnati ta dauki nauyin karatuna a nan Ingila, kin ji abin da ya

rabo ni da gida.
Duk karshen shekara ina zuwa in gai da wan mahaifina. Da na kare karatun digiri na farko ya yi min aure da diyarshi Hasina, muka taho nan tare, inda ta rasu a ya yin haihuwa.
Na zo gida Najeriya ne gai da Baffan nawa, na hadu da ke a filin jirgi". Wannan shine takaitaccen tarihi na.

Ba ta san me ya sa ba hankalinta ya kwanta da Abbas sosai ba, har take jin shine mutum na farko da za ta kwaye ma cikinta, a kalla ko ba komi zai ba ta shawarar da za ta amfane ta, da kuma yadda za ta yi ta gyara kurakurenta.
Ya ce,
"Uhm? Ina sauraron ki...?"

****

"A kullum ina tausar Sa'eed a kan rasuwar Zaliha, ina nuna mishi ya yi hakuri haka Allah ya rubuta musu cewar ba mamallaka juna bane a gidan duniya.
Ya hakura ya nemi wata da ya kare NYSC ya yi auren shi. Duk da ina jin wani dan kishi-kishin abin a raina.
Shakuwata da Sa'eed har ta kai matsayin da zuciyoyinmu suka soma karkacewa, al'amarin da bamu tsammana ba (sha'awa). Na fahimci hakan ne daga yanayin kallon da Sa'eed ke min, da wanda nima nake mayar mishi.
Ya zamanto ko abu Sa'eed zai karva a hannuna sai ya san yadda ya yi hannun shi ya gogi fatan hannuna.
Muka soma wata irin rayuwa ta daban har ya zamanto Sa'eed babu inda ba ya shiga a dakuna na ba tare da la'akari da halin da zai iya samuna a ciki ba.
Muka sake muka shantake muna abin da muka ga dama, sai dai bamu tava yin babban aiki ba, wannan kam muna kula muna jin tsoro. Bamu tava yi ba, kuma bamu da niyya. Amma 'yan 'romances' dinnan bamu dauke su komi ba.
Har ya kammala hutun zangon shi na farko na NYSC ya koma cike muke da kewar juna. Kamar mu tafi tare.

Wasu watanni uku ris Mohammed ya kara a kan wadanda ya saba, suka zama shida ris kafin ya waiwaye ni.
Bai san zuwa wannan lokacin ni tuni na rufe babinshi na daina kewar shi ba, don haka ya yi mamakin yadda har ya yi 'yan kwanakin da zai yi ya kare zai koma bai ji na yi 'complain (korafi) ba.
Bai sani ba ni tuni na samu madadin sa ba. Don haka lafiya-lafiya muka rabu wannan karon yana ta sa min albarka.
Wata ranar lahadi Sa'eed ya zo har kofar dakina ya yi sallama, sanye nake da kayan barci masu laushi ina shirin kwanciya barci.
Sai ya tsaya kallona galala, shi kadai ya san abin da yake kissimawa a ranshi. Ya kare ya ce.
"Aron wayarki nake so ki bani zan kira Hajiya wayata babu chaji".
Na dauko waya na taso zan miko mishi ya hada dani ya rungume cikin wata irin rikitacciyar siga.

Na samu kaina da biye mashi, domin nima cike nake da kishirwar abin.
Cikin dan lokaci mune har a kan gado cikin al'amarin da ba zan iya fassarawa ba. Ban tava samun 'satisfaction' (biyan bukata) da Mohammed irin yadda na samu a Sa'eed a ranar ba.
Wannan shine babban kuskuren da na tafka a rayuwata, ya kuma yi dalilin barowa ta gida, don ban ga sauran amfani na a cikin gidan ba.
Da muka dawo hayyacin mu ne na fahimci aika-aikar da na tafka, ko in ce muka tafka....."
Ta dakata ta share hawayen da ke kwaranyo mata, ko motsi Abbas bai yi ba, yawun bakinshi ya dauke, ya kuma rasa wa zai bai ma laifin a cikin su duka ukun.
......Tsoron abin da muka aikata ya shige ni. Tsoron ingancin addinina da aurena ya addabe ni. Tsoron mahaliccina da abin da za ya tambaye ni ranar da na gamu da shi ya shiga girgiza zuciyata.
Mohammed kam bai sani ba, amma Ubangijina Ya sani, kuma ni da na aikata na sani. Sai dai duk na dauki laifin na aza ga Sa'eedu, wanda kuma daga baya da na yi kyakkyawan tunani sai na ga cewa dukkanin mu muna da laifi.

Na jima da neman gurbin karatu a wannan makarantar ta yanar-gizo ba tare da sanin Mohammed ba, kuma 'admission' bai zo mini ba sai a dai-dai wannan lokacin.
Na duba gabas na duba yamma, kudu zuwa arewa, ban ga inda zan kai nadamata ba, baya ga tafiya in barsu baki daya.
Don bani da bayanin da zan yi ma Mohd. Bani da bakin da zan fuskanci Ubangijina idan na cigaba da zama dashi zaman zina. Amma shi din ai mai afuwa ne ga bayinsa. Don haka na taho, har kuma hakan ya yi sanadiyyar haduwata da kai a filin jirgi.

Sai kuma ga wani sabon al'amarin.... 'ciki'?" Ta furta cikin tashin hankali.
Bana tantama ciki na Sa'eed ne, don kamar yadda lissafin asibitin ya nuna, ya yi dai-dai da ranar faruwar al'amarin Abbas........" Ta ci gaba da kuka.

Da da hali, da ya rungume ta ya rarrashe ta, shi kam tun da uwarshi ta kawo shi duniya bai tava jin irin wannan kwamacalar ba, kuma iya amfani da hankalinsa da tunaninsa ya kasa rarrabe wane ne mai laifi?
Ya gyara murya idanunshi sunyi jawur, ya zamo daga cikin kujerar da yake zaune, ya durkusa ya zauna a gabanta, ya mika hannuwa kamar zai kamo hannuwanta sai ya fasa.
Cikin muryar lallashi ya ce, "Lailah! Ni dai shawarar da zan baki kada ki kashe rai. Ki ji tsoron mahaliccinki, ki bar masa kudura da iradarsa.
Ni Abbas na ji nine uban dan da za ki haifa, ki haife ki bani zan yi mishi uba har karshen rayuwata.
Babu wanda ba ya yi wa Ubangiji savo, dukkanin mu masu savo ne ta wannan hanyar  ko ta waccan.
Abin bukata shine, tsarkakken tuba da tabbacin ba za a sake komawa izuwa zunubin ba.
Sannan a ganina bai kamata ki yiwa Momin ki da 'yan uwanki haka ba, yanzu gashi kin barsu cikin tashin hankali.
Gara da a ce mutuwa ki kai sun san kin mutu, amma vatan dan mutum ba karamin tashin hankali bane ga iyaye.

Ina mai shawartar ki da ki sassautawa zuciyarki, duk wani tsanani yana tare da sauki, kuma babu wanda ba ya yi wa Ubangiji savo a bisa rashin sani ne ko akasi. Sai in ce ke kuma wannan ita ce kaddarar ki".
Hankalinta ya kwanta da nasihohinsa, amma a duk lokacin da ta yi tunanin wai dan kanin miji za ta haifa, da aurenta, tana ji tana gani, zuciyarta kara dimaucewa take.
Ya ci gaba da tausarta da kalamai kala-kala, yana nuna mata wannan ba shi ne karshen rayuwar ba. Ta ci gaba da istigfari ta fuskanci rayuwar dake gabanta.
[12/17/2019, 18:28] Takori: ****
Ya kwanta a hankali bisa madaidaicin gadonsa, ya rasa abin da ke damun sa. Wani al'amari ne da bai tava faruwa da shi ba ke cin ransa.
Duk wani tunani nasa da ya mallaka ya dunkule ya warware a kan LAILAH. Bai tava tunanin Lailan matar aure ba ce yake kauna, yana da burin ta zamo uwar 'ya'yansa, ashe dukkanin su basu da 'yancin wannan al'amarin.

Ya yi parkin din motarshi kirar 'Ferrari' a kofar gida mai malalen siminti, irin gidajen nan na masu kudin da can wani lokaci da ya shude cikin garin Jama'are.
Ya fito ya rufe kofar ya bude boot din motar ya yafito yaran da ke ta wasa a gida mai kallon su, suka zo ya sanyasu suka kwashe kwandunan doya da dankali su kai cikin gidan.
Ya yi sallama a kofar dakin mahaifiyarsa, daga can ciki Hajiya Baida'u ta amsa tare da yi mishi kallon kauna, kafin ta amsa sallamar shi. Ya zare takalman shi ya sanya kai cikin dakin.
Ya samu kujera mai fuskantar mahaifiyarsa ya zauna, kai da ganinsa da kuma irin zaman da ya yi rigija…. ka ga wanda kwanciyar hankali ya yi wa karanci.
Ta tura mishi kwanon gurjiyar dake gabanta kamin ta mike ta je kitchen ta shiryo masa abinci mai rai da motsi.
Sai da ya ci abincin ya sha ruwa kafin da ta yi masa wani irin kallo ta girgiza kai.
"Anya Mamman! Kana nemawa kanka sauki cikin tunanin yarinyar nan? Na rantse da Allah ba ta sonka, da tana sonka da ba ta yi maka wannan abun da ta yi ba, data tabbatar zai daga maka hankali, tunda tana sane ta yi tafiyarta ba shi ke nan ba?
Kiri-kiri ta nuna maka ta gaji da zama da kai ne don baka haihuwa, shi ya sa ta yi tafiyarta amma ka bi ka kwazzabi kanka banza da wofi, sai ka ce dan kankanin yaro ne ya vata. Kana ta asarar kudinka a cigiyar banza.
Tsiyar auren 'kwara' kenan, don ba za su zauna ba. To yaran yanzu ne idan kun so auren mace kamar da ya so fitowa cikin mahaifiyarshi, ba za ku yi aure a gida ba inda a ka san mace, aka san asalinta, a'ah, ku sai kyal-kyal banza".

Maganar Hajiya ta shige shi ainun, da gaske Lailah ba ta sonsa! Ko ta so shi a baya, yanzu ta daina!! Da tana sonsa da ba za ta tava gajiya da zama da shi ba, kowanne irin hali ne da shi kuwa.
Balle kuma yana iya kokarin sa wajen fita hakkin ta. Da gaske ne Lailah gajiya ta yi da zama da shi don rashin haihuwa shi ya sa tai tafiyar ta?
Zai so ya ganta a wannan lokacin, ko don ya yi mata wannan tambayar.
Hajiya ta gyara zamanta ta ce,
"Ban da abinku na 'ya'yan zamani da ba a yi muku gwaninta, da sai in ce mai zai hana ka yi

auren ka ka huta?
Ga nan ‘yar kanin mahaifinka A’isha, ta gama karatun digirinta na farko a jami’ar Bayero, mai zai hana ka tuntuve ta?”
Ya yi ajiyar zuciya abin tausayi, ya ce, “Hajiya duk yadda kika ce dai-dai ne”.
Ta ji dadi, ta shiga sanya mishi albarka.

A ranar ya soma zuwa wajen A’ishar, doguwa, baka, mai kyakkyawar sura. Ya yaba da hankalinta da nutsuwar ta, don haka ya sakarwa Hajiyar shi bakin aljihu ta soma shirye-shiryen aure.
A karshen satin Sa’eed ya zo, nan ya tsinkayi labarin auren. Ya samu dan uwanshi a gidansa da yammacin ranar asabar.
“Yanzu daga Jama’are nake, Hajiya ke gaya min wai ka amince ka auri A’isha”.
Ya ce, “Eh, haka ne, Lailah ta yaudare ni Sa’eed, ta yadda har ban san ba ta kauna ta ba sai yanzu, da tana kauna ta da ba ta yi min abin da ta yi min din nan ba”.
Sa’eed ya ce,
“Ba yaudara ba ce Yaya! Idan ka dubi wasikarta da kyau, za ka fahimci halayyarka ne ba ta so. Sai dai nima na yi mamakin dalilin da ya sa ta zavi tafiya, fiye da ta nemi saki”.
Ya ce,
“Koma dai mene ne ni aurena zan yi, tukuicin kaunata gareta kenan, to ta je, Allah ya ba ta sa’a”.
Sa’eed ya ce,
“To idan kuma ta dawo fa?”
Ya ce,
“Bana jin Lailah za ta taba dawowa gare ni. Da za ta dawo, da zuwa wannan lokacin koma mene ne in ta yi don ta hora ni ko don na gyara kuskuren da nake mata da tuni ta dawo”.
Sa’eed dai ya rasa abin cewa, can karkashin zuciyarsa kuwa nadama ce fal, don ya san shine silar wannan al’amarin.
A wani bangaren tunanin ranar da Allah zai tona asirin cin amanar da ya yi wa dan uwansa mai kaunarsa yake yi, don ya san ba shi da fuskar da zai dube shi daga ranar, ya kuma tabbata ko ba dade ko ba jima wata rana Allah zai bayyana al’amarin.

****

Ya kwankwasa kofar ta taso a hankali ta bude, sanye da bakar jallabiya kirar Oman a jikinta.
Ya shigo rike da ledar magunguna a hannunshi na dama, ya yin da hagun ke rike da wata ledar cike taf da ‘ya’yan inibi.
Suka yi ma juna murmushi a takaice, ya ja kujera ya zauna ita kuma ta koma bakin gadon tana fuskantar sa.
Ya ciro magunguna a leda ya valla ya mika mata tare da dauko mata gorar ruwa mara sanyi a firinjinta.
Ta amsa ta soma hadiya, ya ce,
“Lailah, yau dai ki daure ki shirya muje makaranta, don na ga jikin da sauki. An kafe maku time-table din edam tun shekaranjiya”.
Hanadi, mutuniyar Somalia wadda dakinta ke kallon na Lailah ta yi masu sallama ta shigo, ta

samu gefen gadon da Lailah ke zaune ta zauna suka gaisa.
Ta ce,
“Kwana biyu bana ganin ki kin fito ko kin shiga kitchen, shine na ce bari in zo in ga ko lafiya?”
Tana maganar ne cikin harshen Turanci. Cikin jin dadin kulawar da ta nuna a gare ta ta ce.
“Wallahi kuwa, ina fama da zazzavi ne”.
Ta ce,
“Ayya! Ga shi nan duk ya ramar da ke, Allah ya kawo sauki”.
Su duka suka ce,
“Ameen”.
Suka dan tava hira Abbas bai tofa musu ba, sannan ta tashi ta yi musu sallama ta fita.
Shi ma fita ya yi don ya ba ta dama ta shirya. Ta dauko farar suwaita ta sanya, ta kawo doguwar ‘coat’ har gwiwarta ta sanya tare da dogon wandon ‘cherokee jeans’, ta sanya socks na hannu da na kafa da rufaffen bakin takalmi maras dunduniya.
Ta dauki katuwar jakarta mai dauke da littattafanta ta rataya, ta janyo kofar dakinta ta sa makulli ta rufe.
Ta gangara kasa dakin Abbas, ta kwankwasa ya fito shi ma a shirye cikin DKNY, (trouser and shirt), da bakar suwaita a kai. Ya yi matukar yin kyau, suka jera suka fita. Suka tsaya a ATM na bankin ‘Lioyds’ ta dauki kudi suka karasa makaranta da kafafun su.
Da suka dawo suka tsaya a kantin ‘Morrisons’ dake nan cikin unguwar su (Acton) suka yi ‘shopping’ suka dawo gida.

Haka Lailah ta ci gaba da rainon cikinta da taimakon Abbas, tun tana damuwa da bakin ciki har ta daina.
Yau da lafiya gobe babu, haka ta daure tana karatun ta. Sai da cikin ya shiga watanni biyar sannan ta samu lafiya, kai in ka ganta a wannan lokacin ba za ka ce ciki gare ta ba, saboda yanayin shigar ta na kaya masu kauri.
Allah sarki Abbas, tun daga wannan lokaci ya soma sayan kayan jarirai yana tarawa (unisex). Lailah dai ba ta tava sayen komai ba, ita dai ta mika wuya ga duk yadda rayuwa ta zo mata, don ba ta da tsimi ba ta da dabara.
Abbas ya samu aikin koyarwa (temporary) a wata makarantar sakandire (private), ya zamanto Lailah ta daina tava ajiyarta ta banki, ya tsaya mata a kan komi, itada jaririnta dake ciki.
Katon na locozade, katon na fresh milk, cret din kwai, kwalin apple da kwalin inibi, duk haka yake ajiye mata ba ta kuma isa ta yi godiya ba, yanzun nan zai hau fushi da ita.
Ya hanata yava ajiyarta ta banki sam, tana mamakin wannan al’amari, kulawar da yake nuna mata da kwarin gwiwar da yake ba ta ya wanke duk wani bakin ciki da ke zuciyarta, sai fatan Allah ya raba ta da cikin da ke jikinta lafiya.
Cikinta ya shiga watanni na tara, ranar wata alhamis sun dawo daga awo a NHS. Abbas ya mika mata waya ya ce lallai ta kira Mominta su gaisa.
Atleast ko ba ta fadi mata inda take ba, ta sanar da ita tana nan lafiya don hankalinta ya kwanta. Yana mai nuna mata mace mai haihuwa a kan gava take, baya fata, amma in ta  mutu a ya yin haihuwa me za ta ce da Ubangijinta a kan mahaifiyarta?
Jikinta ya yi matukar sanyi da nasihohin sa, jiki a sanyaye ta soma dialling number Momin, wadanda suke kamar karatun sallah a cikin kanta.

Bugawa daya- biyu Momin ta dauka, ganin bakuwar lambar ta kasar Ingila. Lailah ta yi sallama Momin ta amsa, sai dai ba ta gane mai maganar ba.
Lailah ta kai hannu ta share hawayen da suka zubo mata ta ce,
“Momi nice Lailah.....”
Momi ta ce,
“Hasbunallahu wa ni’imal wakil! Lailah!! Ashe kina raye kika tafi da gangan kika barmu cikin tashin hankali?”
Ta soma kuka. Ta ce,
“Wallahi ba da son raina bane Momi”.
Ta ce,
“Koma me ke damun ki Lailah da har ya sa ki barinmu na dauka kafin kowa ya ji ni za ki fara nema ki fada min damuwar ki, amma ba ki tsallake ni ki barni cikin tashin hankali ba.
Da auren ki Lailah…….. ki tsallake mijinki ki tafi wata uwa duniya, kin san hakkin aure kuwa? Amma tun da hakan kika zavarwa kanki ai shi kenan”.
Ta kashe wayar ba tare da ta sake sauraron ta ba.
Hankalin Lailah duk inda yake to ya yi kololuwar tashi, ta tabbata Momi ta yi fushi da ita, fushi kuwa mai tsanani tun da har ta ki sauraron ta.
Ta mika ma Abbas wayar tana kuka sosai. Ya barta ta yi abunta mai isarta, bai katse ta ba. A karshe tashi ya yi ya bar mata dakin don ta ji dadin yin kukan sosai.
Ya kuma cire layin ya sanya wani don shi ma yana ganin ba yanzu ne ya dace lokacin da Lailah za ta koma gida ba.

A can Alkahira Momi zugum ta yi cikin kwanciyar hankali, ko ba komi yanzu hankalinta ya dan kwanta tun da ta tabbatar Lailanta na raye, kuma cikin koshin lafiya.
Tun da har ta fara tunanin neman ta wata rana za ta yi tunanin dawowa. Ko da Isma’il ya shigo ta gaya mishi Lailan ta yo waya cewa ya yi ta ba shi lambar.
Ya gane lambar ta kasar Ingila ce, amma bai san wane yanki bane. Yayi-yayi ya kama layin ya kasa dole ya hakura.
A ranar Lailah ba ta yi barci ba, tausayin Mominta ya hanata barci na abin kunyar da ta jawo mata da kuma tunanin yadda za su karvi abinda za ta haifa.
Don ba za ta voye ba gaskiya za ta fadi duk ranar da Allah ya mai da ita gida, don ta san aurenta vatacce ne a addini.
Ga rashin Babansu ga rashinta, ta san abun ya yi wa Momin yawa, musamman yadda take sonta fiye da sauran ‘yan’uwanta, take kuma nunawa karara.
Suka smu hutun makaranta har na tsayin watanni uku. A irin wannan lokacin yawancin dalibai kowa kasarsu yake tafiya.
Ban da Lailah da Abbas, a wannan lokacin cikin ya yi katoto ya kuma yi kasa sosai, don haka suka sa rainon cikinsu a gaba, baya awa biyu cikakku bai san halin da take ciki ba.
Yana kuma yawan jaddada mata cewa duk wani motsi da ta ji ba dai-dai ba ta kira wayar shi. Ita har tausayi yake ba ta, ba shi ya kar zomon ba amma ya dauki rataya ya dora a kafadunsa.
Ranar litinin da daddare misalin karfe goma sha biyu na dare. Lailah na barci ta tashi da wani irin azababben ciwon baya, kafin ta ce meye wannan ta ji ta sharkaf cikin wani abu da ke bin kafafunta.

Ta soma salati nan da nan ta yi kokarin daukar wayarta a kan ‘bed-side lamp’ ta yi dialling no Abbas, ba wani vata lokaci ya ce
“ya ya ne? Haihuwar ta zo ne?
Ta ce, “I think so.....”
Ya kashe wayar ya jefar da bargon da yake ciki ya kira hospital van, cikin ‘yan mintuna ta iso da nurses ya yi masu jagora suka fito da Laila sai NHS.
Kwana daya, biyu Laila na cikin matsananciyar nakuda amma ta kasa, in ka ga kai komon Abbas a wannan lokacin sai ya baka tausayi.
A kwanaki biyun nan kaf ba abin da ya sanya a cikinsa sai ruwa, kamar shine mai nakudar.
A karshe aka sanya mata ruwan nakuda har leda biyar amma duk a banza. Don haka suka nemi shi mijinta (kamar yadda suke tsammani) da ya saka hannu ayi mata CS don ceton ta da yaron gaba daya.
Ba tare da wani tunani ba Abbas ya rattaba hannu, nan da nan likitoci suka fara aikin ceton rai. Ya samu ‘waiter chair’ ya zauna yana yi wa Lailah addu’ar fatan alheri.
Awanni biyu cur aka dauka ana aikin kamin wata nurse ta fito daga dakin da aka shigar da Lailah.
Da sassarfar shi ya mike ya cimmata. Ta dube shi cikin tausayi ta ce,
“Am sorry, yaron bai zo da rai ba. Ya dade da mutuwa a cikinta”.
Ya yi ajiyar zuciya mai karfi ya ce, “Lailan fa?”
Ta ce,
“Komi lafiya tare da ita”.
Ba ta rufe bakinta ba aka turo Lailan a kan gadon marassa lafiya zuwa dakin kwana.
Ya ja kujera dai-dai kan Lailah ya zauna, ba a jima ba ta bude ido sannu a hankali tana kallon shi.
Ya dora sassanyan hannunsa a goshinta, abinda bai tava yi ba, yanzun ma bai san yayi ba, rudewa ce. Ya ce,
“Are you alright Lailah?”
Ta girgiza mishi kai. Sannan ne ya samu nutsuwar zuciyarsa.

Kwanansu uku, wajen da aka yi wa Lailah ‘operation’ har ya fara kamewa, aka sallame su a rana ta hudu. Bayan asibitin ta hadata da nurse da za ta dinga zuwa gida tana taimaka mata har kwana goma sha hudu.
A kwanakin nan duka ba ta bar tsiyayar da hawaye ba, na asarar jaririnta. Hakannan Allah Ya dauki kaunar yaron Ya sanya mata. To haka shi ma Abbas da ya dauki rai ya dora a kan abin da Lailah za ta haifa. Ya gama yin duk shirye-shiryen tarvarsa.
Da ta murmure ta koma makaranta, kowa da suka sani tsammani yake ita da Abbas mata da miji ne, daga su sai Allah suka sani.
Jegon Lailah a kasar England, ya zamo wani abin tarihi a rayuwarta da ba za ta manta ba. Haka babynta da ya koma ga Mahaliccinsa har abada ba za ta daina tunaninsa ba.
Abbas ya ce, “Yana da kyau ta fara istigfari tun daga yanzu, domin yana ganin lokaci ya karato da ya kamata ta soma shirin komawa gida, tunda karatun ya zo karshe.
Ba tare da musu ba ta bi shawarar Abbas, sai dai har yau ba ta san da fuskar da za ta dubi Mohammed ba.

****

Watanni uku bayan nan suka karvi kwalin masters din su, shi kuma Abbas saura shekara daya ya karvi na PhD. Jikin Lailah a sanyaye suka soma shirye-shiryen tahowa Egypt.

A ranar wata litinin Momi ba ta zata ba ba ta tsammana ba, kararrawar kofar shigowa ta kada, mai sanar da su cewa akwai bakon d ake son a bude masa kofa.
Budewar nan da za ta yi suka yi arba da diyarta Lailah. Lailah ta rungume mahaifiyarta tana kuka mai tsanani.
Sanah da Najat, suka taso cikin al'ajabi suka rungume 'yar uwarsu. Tare suka rankaya falon cikin yi ma Allah godiya maras iyaka.
Sai da murnar ganin Lailah ta lafa, take sanar dasu tana da bako, don haka Momin ta ba wa Najat makullin sashen baki ta ce ta bude ma bakon Lailah. Akai masa ruwa da abinci.
Momi ta fiddo waya ta kira Isma'il daga wajen aiki ta ce ya zo yanzu-yanzu ya ga abin mamaki, addu'arsu ta kwana da kwanaki farat daya yau Allah Ya karva.
Isma'il ya iso gidansu a sukwane, amma maimakon ya yi murna si ya rufe ido ya soma balbale Lailah da fada, ta inda yake shiga ba ta nan yake fita ba a kan tashin hankalin da ta jefa su a ciki har tsayin shekaru biyu cur.
In ban da sharar hawaye ba abin da Lailah da Mominta ke yi. Daga baya shi ma sai ya rungume 'yar uwarshi ya fashe da kuka.
Suka yi kukan su mai isar su, kamin da Isma'il ya fiddo waya ya kira Mohammed, wanda already ya yi aure.
Hakan bai hana shi tsallake aiyukan gabansa ba ya yi landing a Egypt. Suka tsaya cirko-cirko shi da Lailah sai kallon-kallo, the one that is always hunting his dream….

A hankali jama'ar dake katon falon suka shiga zamewa, ya zamo daga Lailah sai Mohammad dinta, wadanda suka yi cirko-cirko suka ci gaba da kallon juna kamar yau suka fara ganin juna.
Tsohuwar soyayya ta motsawa Mohammed, ya mika hannu ya kamo hannun Lailah, sannu a hankali ya hadata da jikinsa ya kankame ta ya rungume, a hankali ya kama sakin wata irin sassanyar ajiyar zuciya.
Wasu irin dumammun hawaye suke kwaranyo daga idanuwan Lailah, hawayen da ita kanta ba ta san ko na mene ne ba, na nadama ne? Na tunanin gurvataccen auren ta ne? Ko ko na tunanin da wane harshe, da wace fuska za ta fuskanci Mohammed?
A hankali ta soma zamewa daga jikinsa, ta durkushe a kasa kan gwiwoyinta ta soma girzar kuka mai cin rai.
Shi ma binta ya yi ya zauna dirshan a gabanta, ya ce,
"Lailah duk kukan nan na mene ne? Kin tafi a bisa na yi miki laifi, ko ko don ni ba na haihuwa? Kin kuma yi tunanin dawowa wanda mun yi farin ciki da hakan.
Don haka ban ga me zai saki kuka ba, illa mu yi tunanin matsalolinmu da neman hanyar warwaresu domin cimma rayuwa mai amfani.
Sai dai ban sani ba ko za ki iya ci gaba da zama dani duk da rashin haihuwata ko a'a?"
Ta yi saurin cira kai ta dube shi, cikin muryar kuka ta ce,

“Ban tava tunanin in guje ka ba wai don ba mu haihu ba, illa don hujjoji nan da na ambata maka cikin wasikar da na bar maka.
Sannan ni din wata mai babban laifi ce a gare ka da da Ubangijina. Sai dai nima ban san me ya kai ni ga aikatawa ba. Amma ina da tabbacin cewa na yi tsarkakakken tuba wanda Allah (S.W.T) ya yi alkawarin karvar sa, wato tuba da tabbacin ba za a sake komawa izuwa zunubin ba”.
A hankali ya ce,
“Laifin me kika yi min Lailah? Gaya min komin girmansa.......”
Ta mike daga jikinshi ta ba shi baya, ta isa ga taga tana kallon harabar gidansu inda ruwan sama ke sauka a kan korran ciyayin da suka yi wa gidan kawanya.
Ta vata shiru na lokaci mai tsawo, tana hango girman laifinta, hoton ranar da ta kira “bakar rana” na gilmawa a idanunta.
Hawayen idanunta na tsiyaya duk da ta amince da tubanta. Ganin ba ta da niyyar cewa komi, ya kara taku ya isa bayanta, ya dora hannu a hankali bisa kafadunta.
Ta juyo suka yi ‘facing’ juna idanunta sharkaf da hawaye, kafin ta mika hannu ta share su, sannan cikin karyayyar murya ta ce.
“Za ka iya yafe min idan na fada maka cewa har haihuwa na yi da Sa’eed?”
Idandunan shi ne suka yo waje tamkar an busa masu barkono, ya kasa furta komai, kai kamar ma bai ji dai-dai ba.
Ta share ambaliyar hawayen da suka shimfido mata ta ce,
“Aure tsakanina da kai ya haramta Mohammed.... shaidan ya rinjaye mu mun aikata cin amana a gare ka.
Ni kaina ban san ya aka yi ba, sai da mai afkuwa ta afku. Ina cikin kunyar ka, ina cikin kunyar Mahaliccina………
Ka yi afuwa a gare ni Mohammed, ko na samu sassauci wurin Ubangijina.
Na tafi domin ina ganin zaman nawa ba shi da amfani, aurenmu ya riga ya gurvata, na yi asara kuma na ci amanarka, duk da kai ma kana da naka kamashon.
Tun da an tambayi Manzon Allah (S.A.W) cewa, “Kwana nawa ne mace mai aure za ta iya yi ba tare da namiji ba?”
Ya ce, “Kwanaki arba’in”. To ni casa’in nake yi ban ganka ba.
Sai ya nuna shi yana da lokaci na, yana kula dani tamkar matarsa, yana kyautata min tare da bin duk wata hanya don ya sama min farin ciki.
Sannan ka dauko baligi ka hada da matarka wacce ke cikin shekaru na kuruciya,  alhalin kai din baka nan. Ta ya ya varna ba za ta faru ba......?”

Tun da ta soma magana bai yi magana ba binta yake da ido, da zuciya. Jin al’amarin yake kamar almara ko mafarki.
Idan ma Lailah ta kullawa dan uwanshi wannan sharrin ne don ta rabu da shi, wanda tuni ya fahimci take-taken ta kenan, ko don ta hada shi da marayan dan uwansa da baya da ya shi a duniya, to, ta yi karya, ta kuma yaudari kanta”.
Ta dai tafi ta yi gantalinta ta yi shegenta, ba zai tava yarda da wannan tozarci ga dan uwansa ba.
Ya daga rinannun idanun shi da suka kada suka yi jawur suka kankance ya ce,
“LAILAH!”

Dagowa ta yi a hankali ta dube shi, har yanzu kuka take.
Ya ce,
“Mece ce hujjah? Ko shaidar da zan yarda da ke, wadda shari’a za ta yarda da shi ta gurvata/haramta auren namu?”
A mamakance ta dube shi, wato duk irin bayanin da ta yi mishi bai yarda da ita ba. Ta ce, “Na dubi Allah ne na fallasa maka sirrina da yake voye.
Wanda babu wanda ya sani daga ni sai dan uwanka, don in samu afuwa da yafiyar ka ko na samu saukin hukuncin da Ubangiji zai yi min idan na ha’ince ka muka ci gaba da zaman ZINA....”
Tare ta ya yi.......
“ZINA? Ai kin je kin yi abarki, wannan ke da Ubangijinki. Amma AURE NA yana nan ba abin da ya same shi, ba kuma wanda ya isa ya sheganta min shi tun da ban gani ba.
Wace mace mai mutumci ce za ta tafi turai tsayin shekaru biyu ba tare da muharraminta ba, ta ce wai wani wanda ke Najeriya ne uban shegen nata?
Kin ganni nan duk son da nake yi wa mace ba ta isa ta tozarta ‘yan uwana in kyale ta ba. Don haka ki nemo uban shegen ki a inda kika baro shi, ba cikin zuri’ata ba”.
Lailah ta soma hasala, zuciya ta harzuko ta.
Ta ce,
“To me ya yi zafi Mohammed? Ka yar da kwallon mangwaro ka huta da kuda mana?”
Ya yi mata wani irin kallo wanda ta kasa fassarawa, domin kallo ne na kiyayya da rashin kauna, wanda ba ta tava gani cikin kwayar idanunshi ba.
Ya yi wani irin miskilin murmushi ya ce.
“Ai hakan kike so. Na kuma ramfo ki yarinya. Sai ki sake dabara wadda kowa zai yarda dake ba sai kin tozarta dan uwana ba. Don hakan ba karamar illa ba ce ga mutuncinki a idon duniya. Aurenmu babu rabuwa.
Ba shege daya ba, ko dari ne zan karve su tunda ni musulunci ya baiwa. Don haka ki shirya gobe mu wuce gida kawai cikin mutuncin ki.
Na yi alkawarin ba mai jin wannan katovarar taki daga bakina, sai idan ke kika sake furtawa. Zan yi kokarin in gyara kuskurena kamar yadda kike so Lailah. Amma wannan magana, ki barta.
Ki yi haka ki binne ta tunda baki da hujja ko shaida ko kotu ba za ta karve ta ba.......”
Ta katse shi,
“Allah shine shaida ta, kuma ba zan yi zama na zina ba. Da din ma soyayya ta rufe min ido nake zaune da kai Mohd. Kana kwara ta, nake jure bakin cikinka har na kai kaina ga halaka. Ba don Ubangijina ya yi gaggawar farkar dani ba, na san da har yanzu ina cikin halaka. Ka tambayi duk malaman da ka sani.... babu aure tsakanina da kai, tunda na kwanta da shakikinka, alhalin kana raye.
Mohammed na soka, na soka da zuciya daya, kuma har gobe ina sonka, ba zan iya komawa aurenka ba muddin ina cikin hankalina.
Amma tun da ka ce sharri na yi wa Sa’eed, to muje a hakan, wata rana gaskiya za ta yi halinta.....”
Da sauri ya katse ta,
“Ban sake ki ba Lailah.....ki kwana da sanin wannan. Ba kuma zan tava yin hakan ba, in dai

sunana “Mohammad!”.
Don haka na baki kwanaki uku ki yanke mai fissheki, za ki bini mu koma ne, koko zan ji sammaci daga kotu........?”
Fuuu! Ya fita ya banko kofar har sai da Lailah ta razana, mamaki kam yau ta sha shi kamar ya kashe ta, ta yadda mutum mai ilimi kamar Mohammed ya mai da kanshi katoton jahili cikin addini, saboda soyayya da ta rufe mishi ido.
Ta dade tana sake-sake ita kadai, ko dai ita ma ta bar maganar ne kamar yadda ya ce a barta ba tare da ta tozarta kanta ba?
Idan ta ce kotu za ta kai shi a kwatar mata sakin aure kanta za ta tozarta. Duniya ta ji abin da WASA DA KANIN MIJI ya janyo mata.
Asirinta ya bankadu har Momi da sauran ‘yan uwanta su ji, ta kuma san har ‘ya’ya da jikoki ta barma kanta abin gori.
Abu mafi a’ala dai shine a bar maganar, amma kuwa idan ta ci gaba da zaman auren da Mohammed din da har gobe zuciya ba ta hutawa da kaunar sa, zaman ZINA, tana sane, wane hukunci Allah zai yi mata?
Ta fashe da kuka sosai tana yi a hankali kada wani ya jiyo ta, kuka mai cin rai da soya zuciya. Ta yi tunanin bari kawai ta je ta nemi shawarar Abbas a dakin baki, domin kuwa shi babba ne da ya fi ta kaifin hankali da kaifin tunani.
Sannan shi ne mutum na farko da idan ta bi shawarar shi take ganin alfanunta. Bata nadama a cikin duk shawarwarin da yake bata.
Ta fada toilet ta wanke fuskarta da sabulu, ta sauya abayar da ke jikinta ta murda kofar ta fito. A babban falo su Momi ne da su Najat sun yi shimfidar leda suna cin abincin dare, sai lokacin ne ma ta tuna rabon ta da abinci tun na daren shekaranjiya.
Amma wannan ba shine a gabanta ba, fita ta yi harabar gidan ta doshi dakin baki. Ta yi sallama har sau hudu ba’ a amsa ba, sai ta murda kyauren ta shiga.
Babu Abbas babu ko jakar kayan shi. A kidime ta dawo falon tana tambayar Isma’il ina Abbas? Hannu ya tura cikin aljihu ya fiddo ambulan fara tas ya mika mata. Ya kara da cewa.
“Ai tun zuwan Mohammed, da na gaya mishi shine mijinki ya tafi. Ya ce 4 o’clock flight zai bi zuwa London.
Dama burinsa shine ya rako ki ya kawo ki gida, sauran bayanan za ki ji a cikin wasikar”.
Cikin sanyin jiki da kasala ta mika hannu ta karvi ambulan din.
Sanah ta cika plate da shawarmah ta mika mata, hannunta har rawa yake saboda yunwa. Ga wata kewa da ta lulluve zuciyarta, irin wadda ta dade bata ji ba a rayuwarta, tun bayan rashin mahaifinta.
Abbas wani mutum ne mai muhimmanci da kima a gare ta da ba za ta tava mantawa da shi ba. Hanya ce ta hada su, amma tana jin shi da wani muhimmin matsayi a zuciyarta da ba za ta iya tantance wanne irin, matsayi ne ba.
Ga dai mahaifiya ga ‘yan uwanta, ga kanne da yayye musamman Isma’il wanda a yanzu yake matsayin tamkar mahaifi a gare su, amma jin ta take kamar ita kadai ta rage a duk fadin duniyar.
Haka nan take caccakar abincin ba don dadi ko dadin rai ba, illa don ta faranta wa ‘yan uwanta da mahaifiyarsu da suka zubo mata ido don ganin sauyawar da jiki da fuskarta suka yi da jin cewa bakon ta ya tafi.

Ba ma kamar Isma'il dake kare mata kallo cikin nazari. Gaba daya ta susuce ta zama kamar wata firgitacciya.
Tun dawowar ta ya fahimci da abin da ke damun ta, tana kokarin voyewa. Ganin cewa juriyarta ta kare kada ta fashe da kuka a gaban su, sai ta aje cokalin a hankali ta mike ta yi dakinta.
Isma'il da Momi Najla suka bi ta da idanu masu cike da damuwa.
Ba ta bude wasikar Abbas ba sai da ta yi sallar isha'i, ta kara da shafa'i da wutri. Ta daga hannuwanta sama tana hawaye tana rokon Allah ya yafe mata, ya kawo masalaha cikin rikitacciyar rayuwarta.
Sannan ne ta bude wasikar Abbas, ga abin da ke rubuce:

LAILAH!
Haduwar kan hanya ce ta zamo haduwar zuciya...aminci, kyautayi da abota ne suka hadu suka yi gingimemen gini a zuciya..., wanda hakan ya janyo zuciyar ta ke so, amma baki ya gaza furtawa.....
Sai dai kuma sau tari fuska kan gaza boye zahirin abin da ke zuciya…… domin zuciyar na ragaita, a rashin sani na ashe bani da 'yancin wannan al'amarin....
Don haka na wuce London, a duk lokacin da kika tuna ni Lailah..... ki sanya ni cikin kyawawan addu'o'inki. Ina yi miki fatan ALHERI.....

Ta dade tana maimaita wasikar Abbas, amma ta kasa fahimtar ta, ta karanta ya fi sau hamsin amma ba ta fahimci sakon da yake son isarwa gare ta ba.
Wane al'amari ne ba shi da 'yancinsa? Zuciyarta ta halarto mata da amsoshi da dama, ciki kuwa har da mai cewa.
"BA SHI DA 'YANCIN AURENKI TUNDA KE MATAR AURE CE......!"
Sai ta kwantar da kanta a kan dardumarta, tana hawaye. Abbas shine irin mijin da take so, take fata, take kuma addu'a, Allah Ya bata, miji wanda ya san hakkokinta, ya ke wanzar da lokacin shi da hidimomin rayuwar shi wajen kulawa da mace. Yake ririta ta tare da tattalin ta. Sai ta samu kanta da kewar Abbas, kewa mai yawa kuwa.
Yayin da daya vangaren na zuciyarta ya ki kewar Mohammed Jama'are, wanda ke son su koma su yi zaman zina, da son ranta ko babu.
Ta alkawartawa ranta da dai ta komawa auran Mohammed, gara ta karasa rayuwarta babu aure, don ba ta ga so da kauna da aminci a cikin shi ba.
A wani vangaren kuma idan ta ki Mohammed shi Abbas a ina za ta nemo shi? Ya ga mijinta ya dawo ya yi tafiyarsa ba tare da ya yi mata sallama ba, balle su fuskanci juna su shawarta mafita ga rayuwarsu.
Ina za ta nemo shi? Kano da girma, ina za ta nemo shi ba ta san komi a kan garin da yake ba balle mazauninsa....
Ta kifa kanta cikin tafukanta ta soma kuka mai cin rai, kuka irin wanda ta dade ba ta yi a rayuwarta ba. Kukan sabo, soyayya da kewa, soyayya mai laushi da taushi, da ba ta tava tsintar kanta a ciki ba.
Daga karshe barci ya sace ta cike da mafarkai barkatai marasa kan gado, duk a kan Mohammed da Abbas.
Don haka da kyar ta samu ta yi sallar asuba a kurarren lokaci. Ta koma ta kwanta, ba ita ta tashi

ba sai karfe goma na safe da Momi ta kwankwasa mata kofa.
Ta yi mika ta yi salati sannan ta zo ta bude kofar.
Kallo daya Momi ta yi mata ta ga fuskarta a kumbure, idanunta sun yi luhu-luhu sun yi jawur. Ta kama hannunta, har bakin gadonta sannan ta rungume ta. Ajiyar zuciya mai nauyi ta suvucewa Lailah.
Hawayenta suka kwaranyo a bayan mahaifiyarta, ta yi kukan ta ma'ishi, Momi Najla ba ta dakatar da ita ba.
Ta tabbatar akwai abin da ke damun diyarta wanda zurfin ciki irin nata ba zai bari ta bude baki ta fada ba.
Ta kai hannu tana shafar bayanta tana lallashin ta. Ta ce.
"Idan baki gaya min abin da ke damun ki ba Lailah wa za ki gaya mawa? Ni mahaifiyarki ce, da ta tsuguna ta haife ki, nice farko da ya kamata in san damuwar ki, in yi kokarin da zan iya in warware miki ita.
Jiya na ga Mohammed ya fito cikin fushi, sannan tun da aka gaya miki tafiyar wanda kuka zo tare kin kasa ko cin abinci. Kar dai ki ce dani aure kika yi a kan aure Lailah?"
Magana take cikin sanyi, da zuciya irin ta UWA, sannan ta kakkafe ta da idanu. Lailah na girgiza kai tana cewa.
"Lala-lala Ummi......"
A hankali ta soma zayyana mata komai. Ta kare da cewa.
"Kwanaki uku kacal ya bani in bishi mu koma a bar maganar, ko in kai shi kotu in kwaci takardar saki.
Duk yadda na so in nusar da shi rashin ingancin aurenmu ya ki sauraro na. Har yana zargina da yiwa kaninshi sharri. Ummi ina cikin wani hali na kuncin zuciya da rashin yarda da kaina......
Me zan yi Ubangijina ya yafe mani ya kawo mani maslaha cikin rayuwa ta? WASAN KANIN MIJI bai kare ni da komai ba sai jefa ni a halaka da wanzar dani cikin bakin ciki da nadama...."
Ta ci gaba da kuka a kan cinyoyin mahaifiyarta.
Momi ta rasa abin cewa, sai LA'ILAHA ILLALLAHU….. Allah ya kawo mu wani zamani gurvatacce..... zina ta zama ba komai ba, daga wajen marasa auren da masu auren ma.

Ba ta tava jin irin wannan kwamacalar a cikin aure ba, sai dai al'amarin da ya riga ya faru ba abin da za a iya yi a kai sai dai ayi kokarin gyarawa, don a guji gaba.
Ta dago fuskar Lailah daga cikin cinyoyinta ta ce.
"Kema kina da laifi Lailah, me ya sa a lokacin da ya bijiro miki da bukatarsa baki yi wani kokari na kare kanki ba?
Me ya sa kika zavi yin nisa damu fiye da ki gaya mana a yiwa tufkar hanci? Ayi abin da ya dace tun a lokacin?
Laifuffukan ki suna da yawa Lailah. Kin tafi zuwa wata duniya ba tare da yardar mijin da ke auren ki ba, kin kulla alaka da wani da namiji da ba muharramin ki ba. Me zai hana soyayya ba za ta gitta a tsakani ba? Da aurenki Lailah?"
Lailah dai ba baki sai kuka. Ta yarda ita ma da laifinta. Ta kama hannun Momin ta rike cikin nata.
Cikin rishin kuka ta ce,
"Na yarda nima ina da laifi Momi.....sai dai na tuba, na dade ina tuba ga Ubangijina.....tuba irin

wanda Ubangiji ya yi alkawarin karbar sa.... wato tuban da aka tabbatar ba za a sake komawa izuwa zunubin ba”.
Sai Momi ta rungume ta,
“To yanzu me kike so da rayuwarki? Kin shirya zama mutuniyar kirki ko za ki ci gaba da yin alakar kusanci da mazan da ba muharramanki ba?”
Ta yi saurin katse Momi da cewa,
“Na shirya zama ‘yar kirki Momi a gaba dayan sauran rayuwata......”
Momi ta ce,
“Aurenki da Mohammed ya riga ya lalace, sai dai dukkaninku ku yi hakuri da shi.
Maganar zuwa kotu domin karvar takarda a hannun Mohd. ma ba ta taso ba. Domin kanki za ki tozarta. Za mu nemi sulhu da shi, jibin zan ganku tare. Amma ki yi dauriya, dole Isma’il ya ji zancen nan, don shine waliyyinki.....”
Lailah ta zaro ido,
“Zai tsane ni Momi, zai yi Allah wadai dani Momi”.
Ta ce,
“Shirmen banza kenan, an ce da ke hannunka na rubewa ka yanke ka yar ne? Baki yi tunanin hakan ba a lokacin da kike hutawar haram da kanin mijinki? Tashi ki bani wuri tun nima din ban tsane ki ba”.
Mikewa ta yi tana goge hawayen idanunta. Ta shiga ‘toilet’ ta sakar ma kanta ‘shower’ ko ta ji sanyi a zuciyarta.

****

[12/17/2019, 18:28] Takori: An zauna a falon marigayi mahaifin su Lailah a ranar (26) ga watan Maris na shekarar 2000.
A gefen Mohammed Jama’are kanin shi ne Sa’eed Jama’are, wanda tun da ya shigo falon kanshi ke sunkuye bai dago ba.
Sai Isma’il Yayan Lailah, kusa da shi Lailah ce cikin abayat da Momi a gefenta. Sai Hajiyar su Mohammad a gefe wadda fuskarta babu alamun rahma, kada ma su ce sulhun a mayar da Lailah gidan danta za’a yi, don a cewar ta Lailah karuwanci ta tafi Turai ba wani karatu ba.
To sai kuma kallo ya koma sama, a inda ta ji sulhun da Balarabiya Najla ta nema, wato a warware auren Lailah da dan nata sakamakon kazantar da auren da suka yi da WASAN KANIN MIJI.
Ta dube su tsaf, a ranta ta ce ‘yan kundun uba.
Sannan ta mike ta bugi kirjinta ta dubi Momi ta ce, “Ni Baida’u ban haifi dan iska ba, ‘ya’yan nan biyu su Allah ya bani ban taba ji an ce an gansu suna aikata wani aiki na assha ba.
Balle Sa’idu ya nemi matar Yayansa da yake mutuntawa fiye da ni, yake kaunarta da zuciya daya.
Ta je can ta nemi abokin shaidancin can a inda ta je karuwanci....Takarda kuwa ko baku ce ba dama za a ba ta, don tuni na aurawa dana mace ‘yar usli wadda na san asalinta. Don haka.......”
“A’a, Hajiya ki yi hakuri ki zauna ayi maganar nan a tsanake..........” Sa’eed wanda ke sunkuye da kai ya fadi cikin sanyin murya....
Ya kara da cewa,
“Don Allah Hajiya ki zauna....”

Ta koma ta zauna tana hararar sa..... Shi kuwa Mohammed jifanshi ya yi da wani kallo mai tarin ma'anoni da dama.
Amma Sa'eed ya maida kanshi kasa, ba tare da ya sake hada ido da kowannen su ba ya ce.
"Hajiya da Yaya ku gafarce ni, tabbas abin da Lailah ta fada cewa mun aikata gaske ne. Mun tava kusantar juna amma sau daya ne cikin ribatar shaidan.
Zancen haihuwa ne ban san da shi ba, don ina jin tun a ranar da al'amarin ya faru ta bar gidan, nima ban kara ganinta ba ko ji daga gare ta ba sai yau.
Don haka Yaya ka yi hakuri, ka kuma yi min duk hukuncin da ka so.......kasancewa ta wanda ya yi maka cin amanar da baka tava zato ba, na raba ka da abin da kake so, ba don ka daina son shi ba.
Yaya daga ni har Lailah ta wani vangaran bamu da laifi, ko me muka yi kai ka bamu damar mu yi shi....."
Kafin ya karasa Mohammed ya kai masa wani wawan mari, ya bishi ya shake da kyar Isma'il ya kwace shi. Ya galabaita yana haki abin tausayi.
Hajiya ta ce,
"Rufe min baki tun ban tsine maka ba, kai kuma Mamman rubuta takardar sakin ka basu idan ka haifu cikin iyayenka......rubuta musu yanzun nan ka bani, ko in daga maka nono wallahi…….".
Ya sunkuyar da kai hawaye fal idonsa. Isma'il ya bashi biro da takarda.
Yana rubutun hawaye na jika takardar, ya rubuta saki daya jallin-jal, ya mikawa Isma'il, ba tare da ya damu ya goge hawayen da ke zuba tarara daga idanunshi ba.
Cikin macewar jiki Lailah ta daga ido ta dube shi, anyi sa'a a lokacin shi ma ya dago sashen da take. Sai ta ji hawaye sun tsinke mata na tausayin Mohammed, tsohowar soyayyar dake zuciyarta ta motsa. Da gudu ta bar falon ta yi cikin gidansu ta fada bisa gadon Momi tana kuka, mai fita daga karkashin zuciya.

****

Kwata-kwata rayuwar Lailah ta sauya, domin duk inda macen da ta san ciwon kanta take, wannan kalmar ta 'saki' ba karamin tashin hankali bane a gare ta, ko da auren kiyayya ne kuwa, balle auren da aka gina a kan turbar so da kauna.
Gaba daya ta susuce ta fita hayyacinta, tsakaninta da mahaifiyarta sai gaisuwa, don tun ranar da su Mohammad suka daga gida Najeriya ba ta kara ganin hakorin Momi Najla ba.
Ta ce sai ranar da ta ganta a dakin aure, sun daina jera kafada, sannan ita dai ba ta tava ZINA a tsayin rayuwar 'yammatancin ta ba, balle da auren ta.
Isma'il ko kallon ta ba ya yi balle ta ga hakoransa. Duniyar ta yi mata kunci ta buwaye ta. A wajen kannenta su Najat kawai take jin sanyi, wadanda basa rabo da dakinta suna yi mata hira, suna wasanninsu.
Aka kwashe sati biyu a haka, rama da zugewa da take yi suka addabi zuciyar Momi Najla.
Ta soma tunanin Allah ya sa ba kanjamau ta je ta debo a kanin mijin nata ba. Don haka yau da safe Momi ta sanya ta a gaba suka nufi asibiti.
Laila na jin sanda Momi ke ce da likitan ta kawo ta a yi mata gwajin kanjamau ne. Sai hankalinta ya kara tashi.
Ko numfashi da kyar ta shake shi. Wai me kowa ya dauke ta ne? Karuwa ko me?

(Kadan kenan daga irin bakin cikin da ‘ZINA’ ke haifarwa, domin ita ce karshen tozarci a rayuwa, musamman ga diya mace).
Ba ta shaki numfashi sosai ba sai da result ya iske su cewa Lailah lafiyarta kalau.
Lailah ta kasa jure mu’amalar doya da manjan da Momi da Isma’il ke mata, don haka ta soma tunanin kirkirarwa kanta abin da zai amfane ta.
Da farko ta soma neman aikin koyarwa a jami’ar da ta yi, ba ta sha wahalar samun aikin ba, musamman saboda ingancin masters dinta na Ingila.
Ta shigo gida rike da tulin takardu a hannunta da gani a masifar gajiye take. Sanah da Najat suka garzayo suka rungume ta.
Ta russuna dai-dai tsahonsu ta rungume su ta sumbace su daya bayan daya, ta tambaye su ina Momi? Suka nuna mata dakinta.
Ita da Isma’il ta samu suna magana da kasafce-kasafcen tulin kudi a gabansu. Ko dai na business dinsu ne ko na mene ne ba za ta ce ba. Domin Isma’il babban dan kasuwa ne. Ya kan je Dubai da America kawo kaya kasar Egypt, sam-sam ya ki aikin gwamnati, duk da kwalayensa na karatu masu inganci.
Nan da nan dukkaninsu suka yi fuska suka daina zancen da suke, suka bi ta da kallo kamar sun ga wata bakuwa.
A savule kuma kamar ta yi kuka ta zauna a gabansu, ta aje takardunta a gefe. Kadan ya rage ta fashe da kuka.
Wai Momin ta da Isma’il ke nuna mata yau ita bare ce a cikinsu, don kurum ta yi kuskure a rayuwarta?
Ta kai bayan hannunta tana share hawaye ta kasa cewa komai. Zuciyar UWA ta soma russuna, amma Isma’il sai ya hau fada.
“Lafiya za ki zo ki sa mutane a gaba kina yi musu kuka kamar su suka saki kije ki zama ‘yar iska ki ci amanar aure?”
Sai ta idasa rushewa da kukanta, ta ce,
“Na tuba Momi, na tuba na bi Allah na biku. Isma’il wane ne ba ya kuskure a rayuwarsa? Idan kun juya min baya ina za ni? Idan kun watsar dani wane ne zai tallafe ni? Dan uwana ka yi min aikin gafara kamar yadda nake nema a wurin wanda na yi wa laifin amma ba kai ba”.
Ya yi tsaki ya soma tattara kudin yana zubawa a jaka, ya ce da Momi
“Idan za su tafi kaiwa sai a gaya mani in raka su”.
Momi ta ce, “Babu laifi”. Ya sa kai ya yi ficewar sa.
Lailah wadda ke durkushe har zuwa lokacin a gabansu ba ta daina shesshekar kuka ba, kukan da ya tava zuciyar Momin, ko ta ki Allah.
Ta mika hannu ta kama tattausan tafin hannunta ta ce,
“Ya isa.......ya isa”. Tana goge mata idanu da gefen abayarta.
Da kyar ta tsaida kukan ta jawo ‘file’ din dake gabanta ta ciro takardar daukar aikin ta mika mata.
Momi ta sanya gilashinta tana dubawa, ta mika mata ta ce,
“Masha-Allah, yaushe za ki fara zuwa?”
Ta ce, “Sati mai zuwa”.
Ta ce, “Ga shi kuma za a yi auren Isma’il sati mai zuwan”.
Ta ce, “Wa zai aura?”

Ta ce, “Sujood”.
Sai Lailah ta vangale baki tana dariyar farin ciki.

Sujood diyar Yayar mominsu ce, tare suka taso da Lailan tun suna kanana. Ba za ta ce Sujood kawarta ce ba, don ita ba ta kawance, to amma ‘yar uwarta ce da suka san juna suka fahimci juna.
Sai da suka zo shiga jami’a ne suka rabu, inda Sujood ta tafi kasar ‘Syria’ ta yi karatu a kan likitanci, Lailah kuma ta yi a nan Al-Azhar din Alkahirah.
Biki sosai suka yi irin na al’adarsu, Lailah na kan gaba a kan komi. Aka kawo Sujood nan gidan su part din Isma’il, kasancewar gidansu katon gaske, mai sassa daban-daban.
Lailah ta shirya sassan sosai kai ka ce fadar wani gwamna ne kasancewar a al’adarsu miji shi yake yin komai na kayan daki.
Musamman suka fita Oman don sayayyar kayan da za a zuba a gidan ita da Momi. Ganin irin rawar jiki da wahalar da Lailah ta sha a shagalin auren sa ya sa ya soma sakar mata.
Amma ko an gode bai ce mata ba, duk da ya lura sayayyar da a kai ta zarta ta kudin da ya bayar.
Ita kanta amarya Sujood ta lura da basar da Lailah da Isma’il ke yi a ‘yan kwanakin da ta yi a gidan, amma ta ja bakinta ta yi shiru don ba ma’abociyar magana ba ce.
Bayan bikin ne Lailah ta mayar da hankali a kan aikinta. Wata rana idan ta fita tun takwas sai shida na yamma.
A karshen sati ne kawai take zaman gidan, kuma zuwa lokacin Isma’il ya saki ranshi da ita. Ya yarda ba wai sai mutum yana dan iska bane kawai yake yin iskanci ba, a’ah, dan kirki ma kaddara da yanayin rayuwa kan kai shi da aikata laifi, ko ba da son ran shi ba.
Sai dai mu yi ta addu’a Allah ya sa mu fi karfin zuciyoyinmu. Ya raba mu da son zuciya, ya nisanta mu da kaidin shaidan. Amin.
***
ko da jirgi ya sauke su Sa’eed da Hajiyarsa a garin Bauchi, basu kara ganin Mohd ba. Shi Sa’eed ne ya yi masu shatar mota suka nufo Jama’are, don ya lura a yadda Yayan ke tunzure da shi in aka ba shi wuka zai iya burma masa. Haka in yana da bindiga zai iya harbe shi har lahira. Don haka salin-alin ya wuce Jama’are shi da Hajiya.

Mohd. yana kwance a sofa na falon gidan shi yana busa hayakin ‘Marlboro’, idanunshi a rufe. Tiryan-tiryan yake tariyo rayuwarshi da Lailah, tun haduwarsu a babban filin jirgin saman Egypt, sun rako mahaifinsu zai tashi zuwa Nijeriya.
Ya tuno gwagwarmayar da ya sha wajen neman auren ta, domin Hajiyarshi sam ta ki amincewa, don a cewar ta ba ta son kwashe-kwashe da rore-rore.
Marigayi mahaifinshi shi ya tsaya mishi tsayin daka ya samu abin da ransa da zuciyarshi ke so.
Ya tuno irin soyayyar da suka gudanar a kwanakin amarcinsu. Wanda har gobe ba a samu macen da yake so ya kuma ke kauna ya amincewa irin Lailah ba.
Ya kuma tuna cewa, tun daga wancan lokacin Lailah ba ta kara yin zaman farin ciki a gidansa ba. Ta yi hakuri har ya kure ta domin ba shi da lokacin ta.
Idan har za a auna ne a mizani, to alhakin koma me Lailah da Sa’eed suka yi, to yana wuyansa. Kuma nashi laifin zai rinjaya. Bai san yana son Lailah ba sai yau da ta kuvuce masa, zuciya ta

kuma tunkudo shi ta ce ya je ya dan huce a kan Sa'eed kawai ko ya rage asara.
Daga baya kuma ya ce,
"To don na daki Sa'eed me na yi? Yaro mai tsoron Allah da harshe daya, dukan da ba zai rage komi daga suyar da zuciyarshi ke yi ba.
Ya tabbatar ya yi rashi tun da ya yi saken da ya rasa Lailah, mai kyautayi da hakuri da tausasawa a gare shi.
Ko daya ba za a hada Lailah da Aisha ba. Ta fannin komai, shi dai kawai ya karvi aurenta ne don ya faranta ran Hajiya.
Amma soyayyarta gaba daya in za a dora ta a sikeli ba ta wuce cikin cokali ba. Ai gaba da gabanta... wai aljani ya taka wuta.
Me zai yi ya huce abin da Sa'eed ya yi masa? Babu, ya riga ya cuce shi. In ma kotu ya kai shi karshe ma watakila shi zai je belinsa.
Idan ya doke shi bai huce ba, idan ya yi masa Allah Ya isa, idan alhaki ya lalata shi komai a kansa zai kare.....
Bai ankara ba ya ji wata irin azaba a 'yan yatsunsa, tuni tabar ta kare har ta soma cin yatsun hannunsa.
Ya jefata 'ash tray' na silver dake gabansa ya bude idon shi sakamakon tsayuwar mutum da ya ji a kanshi. A'isha ce.....
Ta ce,
"Majnoon na Lailah......!
Za ka iya tashi mu yi 'break' din ne ko Misra za ka koma a baka, tunda bikon bai yuwu ba?"
Ya valla mata harara ya ce,
"Idan komawar zan yi za ki iya hanawa ne?"
Ta kyave baki ta ce,
"A'a, ko bani da abin yi ba abin da zai kai ni inda ba'a so na....."
Ji kake fauu! Ya wanke mata fuska da yatsunshi biyar...har sai da ta ga wuta da taurari. Ta kama kuncinta duka biyu ta sunkuya tana neman kwayar idanunta da ta neme su ta rasa na wucin gadi.
Da kyar ta ce, "Ni ka mara daga magana Mohd.?"
Ya yi tsaki ya yi ball da 'center – table' din gabansa na gilashi tsantsa, a take ya ragargaje.  Ya yi sama fuuu! Kamar zai bi ta kanta, ta yi kwafa ta mike ta ce.
"Wallahi ka mari auren ka".
Ta yi dakinta tana kuka tana hada kaya. Azahar a Jama'are ta yi mata, ba ta nufi gidan Hajiya ba don ba sulhu take nema ba, gidan iyayenta ta nufa.
Kwananta biyu Hajiya ba ta san ta zo ba, sai mahaifinta ne Malam Adamu ya zo yake gayawa Hajiyar yadda aka yi.
Hajiya ta girgiza kai ta ba shi hakuri, ta ce, "Za ta dau mataki ita ma zata yarda da komai amma banda duka. Amma ya yi hakuri ya turo mata A'ishar ta zauna a wurin ta kafin ta kira shi".
Malam Adamu ya gyara zama ya ce, "Hajiya idan Muhammadu baya son auren nan ina ganin gara a raba shi cikin mutunci ba tare da zumunci ya lalace ba.
Don ta fadi abubuwa da yawa, wadanda abin dubawa ne a cikin aure. Ta ce sai ta yi watanni uku ba ta ganshi ba, kuma bai neme ta a waya ba.
Sannan in zai tafi ba ta isa ya yi mata sallama ba, sai dai ta ga kudi a kan tebur, haka in zai

dawo. Allah ya ga zuciyata ba don kudi na wanke A'isha na ba wa Mohammadu ba, sai zumunci da mutuncin da ke tsakani".
Hajiya kamar ta yi kuka, ta ce,
"Don Allah ya ba ta lokaci ta kira shi, in Allah Ya yarda za ta tsawatar".
Kwana uku kenan Hajiya na buga layinshi ana gaya mata a rufe yake. A lokacin ma shi yana 'Bangkok'. Daga can ya wuce 'Austria' yana yi wa jirgin Virgin Atlantic lodi.

Sai da ya kwashe watanni uku cur sannan ya yo Bauchi. Bayan motarshi fal da tsarabar Hajiya da Sa'eed din da ba shi da yadda zai yi da shi.
Hajiya na sallar walha ya daga asabarin dakinta kasancewar ana zabga sanyi, kamshin turarensa kawai da ta shaka ta san cewa shine.
Ya yi sallama ya shigo ya kwanta cikin kujera yana waya. Ba ta bi ta kansa ba sai da ta gama sallolinta da laziminta, sannan ta aje mayafi gefe ta juyo ta dube shi kawai ba ta ce da shi komai ba, don bakin cikin da yake shaka mata Allah ya yi yawa da shi.
Sai shine ya rufe wayar ya sauko kasa yana murmushi ya ce,
"Barkanku da safiya Hajiya, na same ku lafiya?'
Da da ne sanda yake yaro idan ya ba ta haushi irin haka carbinta za ta jawo ta tsutstsula masa, to yau ma tunanin da ta yi kenan.
Sai dai kuma da ta dubi girmansa da haibarsa hadi da kwarjinin da Allah yai masa, sai ta rasa ta ina za ta tsula mai carbin ya ji zafin shi a jikin shi?
Ko'ina guraye ne murdaddu na ingarman namiji, mai cikar halitta, ma'abocin haiba da kamala. Sai birkitaccen hali da babu macen da za ta jure shi.
Dole ta aje carbinta a gefe ta dube shi cikin ido ta ce.
"Barka kadai".
Ko a kwalar rigarsa, don shi ya manta ma da wata A'isha, ya soma ba ta labarin irin tafiye-tafiyen da ya yi a wannan tafiyar.
Ta gaji da soki-burutsun da yake mata ta ce,
"Duk na ji, ka samo kudi ko?"
Ya ce,
"Sosai kuwa Hajiya, don na yanke ma can gidana na Bauchi za ki koma, ni zan koma Old G.R.A".
Ta jinjina kai ta ce,
"To iyali fa?"
Ya yi dan duru-duru na rashin sanin abin cewa, don shi tun lokacinda A'isha ta sha mari bai kara tuno ta ba ya ce,
"Tana can Bauchi, don kai tsaye nan na yiwo ban je gidan ba".
Haushi ya kashe bakin Hajiya Baida'u, ta rasa me za ta ce masa. Ta girgiza kai ta ce.
"Na tabbata ba haka kwarorin nan suka barka ba. Yanzu abin da kake yi wa aurenka ka kyauta kenan?
Baka ma san takamaiman inda matarka take ba. Ka kama 'yar mutane kuma 'yar uwarka da duka kamar jaka aka aura maka?
Tun da ka yi mata dukan ka haure ka yi tafiyar ka ba tare da ka damu da halin da take ciki ba, balle ka binciki lafiyarta, wai sunan tana matarka...."

Ya katse ta da cewa, “Ni fa Hajiya ban doke ta ba, marin ta kawai na yi da na ga za ta kawo min rashin kunya, wato zuwa ta yi ta ce na dake ta kenan?”
Hajiya ta ce, “Ungo naka....”
Ta yi masa umbola. “Wato marin ma kawai ne. Ka fada da bakinka ka doketan kenan. To sam ba zan lamunci wannan rashin hankalin ba, ka je can gidansu ka ba ta hakuri ka sa matarka a gaba ku tafi, kada na kara ji ko da tsinke ka tsikare ta dashi balle mari. Idan ba haka ba wallahi zan dauke ta, in ya so ka koma in da ba a san darajarka ba ka je can ku karata, ni kuma in fidda hannuna a kanka”.
Ya sunkuyar da kai, “Duk me ya yi zafi Hajiya? Ki yi hakuri zan je in ga Baba Adamun, zan ba shi hakuri amma don Allah ki sa min albarka!”.
Ya ba ta tausayi matuka, Allah ya ba ta ‘ya’ya masu gudun zuciyarta, su biyu kacal amma kamar goma ta haifa. Zurfin ilimin zamaninsu bai sa sun kangare mata ba, komi ta ce ‘eh’ ne ko da bai yi masu ba.
Sai dai har yau ba ta kara tada zancen Sa’eed da Lailah ba, ga dukkan alamu ba ta son zancen kwata-kwata, duk da ta amincewa ranta gaskiya ne tun da har Sa’idun ya furta mata da bakinsa. Ya dai nemi gafararta ya kuma ce ta taya shi neman gafarar Ubangiji. In Allah ya yarda wani abu makamancin wannan ba zai kuma faruwa da shi ba, insha Allahu.
Ya sa aka fiddo jakunkunan da ya zo da su, sittiru ne dankare, ya ware na Sa’eed. Hajiya ta ji dadi sosai.
Sannan ya ce, “Sauran a rabawa dangi”.
Ta ce, “To, matarka fa?”
Ya ware wasu ya ce, “A kai gidansu ita zai ba ta nata daban”.  Bayan shi tun da ya tafi ma ko a mafarkan shi ba ta zo ba. Tunanin shi na LAILAH ne, sai dai ya ce Allah ya yaye masa.
Duk kawaicin Baba Adamu yau ya fitittike ya gwada masa shi ma yana son ‘yarsa. Bayan dogon kai ruwa rana da ban hakuri sannan da kafa sharudda sannan ya yarda ya kira A’ishan suka tafi, wadda ita kam kamar a kan kaya ta yi watanni ukun nan cike da nadamar fitowar ta, domin ta tabbatar kafin ta sake samun wannan daular da tsadadden miji irin nata a matsayi da ajin rayuwarta, abu ne mai matukar wuya. Ko ko a ce ba zai yiwu ba. Allah ne ya kashe ya ba ta, wautarta za ta kwace mata.
Don haka tun a mota ta soma zuba masa hira, tun yana share ta har ya biye mata. Suna yi wa Baba Adamu dariyar sharuddansa na duk ranar da ya kara dukan ta zagewa zai yi ya rama mata, don bai fi shi karfi ba.

****

Tun zuwa Sujood, Lailah ta samu abokiyar debe kewa, duk sanda ba ta da darasi tana sassan Sujood ko ita Sujood din na nasu vangaren. Ko su shiga gari idan Isma’il baya nan.
Cikin watanni biyar da suka biyo baya, account dinta ya yi nauyi, don ba ta tava komi cikin albashinta, Isma’il ya dauki nauyin rayuwarsu gaba daya.
Kuma Egypt ba kamar London ba, ba ta biyan kudin haya, gida ne nasu na kashin kansu. Duk da matsin tattalin arziki da kasar ke da shi wannan bai sa al’ummarta zama cikin talauci ba. Egypt kasa ce mai dadin zama da albarkar abinci, da suttura da wadatar ilimi, da kwararrun ma’aikata kiwon lafiya.
Kullum cikin kwanciyar hankali da wadata suke, ban da yanzu da suke fuskantar matsin

Amurka. Sai dai damuwar Lailah daya (ABBAS) ina za ta nemo shi?
KANO da girma, kai ita duk zamanta a Najeriya ma ba ta tava zuwa Kano ba, ba ta san ina take ba.
Tana dai ji ana fada Kano-Kano a bakin Sa'eed da Mohammad, amma ba ta ma tava tambayar su wani sharhi a kai ba. Ta kuma gwada nambobinshi na Britain an gaya mata ba a amfani dasu sam.
"Watakila Allah ya rubuta iyaka haduwarmu kenan???"
Ta tambayi kanta cikin sanyin murya.
"Haduwar kan hanya ce ta zamo haduwar ZUCIYA…., aminci, kyautayi da abota ne suka hadu suka yi gingimemen gini a ZUCIYA. Wanda hakan ya janyo ZUCIYAR take so, amma baki ya gaza furtawa...... Saidai sau tari fuska kan gaza boye zahirin abin da ke ZUCIYA, domin ZUCIYAR na ragaita....Sai dai kuma a rashin sani na ashe bani da 'yancin wannan al'amarin………
Ta tuno kalaman wasikarsa.

Idan ta yi wa wadannan kalaman fassara ta hankali....Abbas na son ta! Sai dai AUREN da ta ke da shi ya zama shinge. Ta yi murmushi ita kadai, ta juya ta rungumi filo.
...... "Kana da 'YANCIN Abbas, yanzu kana da 'YANCIN, dukkanmu muna da 'YANCIN. Allah ya hada fuskokinmu cikin gaggawa".
Idan ta ce tunanin Abbas da soyayyar shi da ta yi kane-kane a zuciyarta za ta dinga yi, lashakka za ta samu matsala a kan aikinta.
Don haka take rufe 'file' din zuciyarta a duk lokacin da take tare da dalibanta, wadanda suke kaunarta saboda karancin shekarunta da manyan kwalaye haka. Kuma a lokacin ne Jami'ar Al-Azhar ta tura ta karo Karatu (in service) a Jami'ar Ummul-Kura da ke Madinah.

Duk yadda ta yi don ta cogewa hakan abin ya faskara, domin tsarinsu ke nan. Dole ka mallaki kwalin PhD a matsayinka na 'staff'. Wannan ne zai baka damar zama Dr. A ilimi. Sai dai aure da iyali na sanyawa a barka a nan cikin Alkahira, wanda ba ta da ko daya.
Ta samu Momi da Isma'il take gaya musu batun tafiyarta Saudi-Arabia. Sujood sai ta hau kuka ita ba ta yarda ba.
Isma'il na dariya ya ce,
"Haba Sujood sai ka ce wata karamar yarinya? Abin da za ta dinga zuwa ko mu muje?"
Budar bakin Sujood sai cewa ta yi, "Ni sai dai mu tafi tare".
Lailah da Isma'il suka kwashe da dariya, Momi ba ta ce dasu komi ba.
Sai da Sujood da mijinta suka tashi Momi ta dubi Lailah sosai ta ce,
"Kina da yakinin cewa za ki iya rike kanki da mutuncinki tsayin wannan lokacin din?"
Kawai sai Lailah ta fashe da kuka. Ta rasa ranar da Momi da Isma'il za su daina yi mata kallon wata mara imani.
Wane irin tuba suke so ta yi a kan kuskurenta wanda ba ta yi ba? Shekara guda har da doriyar watanni sun kasa yi mata kyakkyawar shaida?
Momi ta saki baki tana kallon ikon Allah, ta ce,
"To mene ne abun kuka cikin maganata?"
Ta ce,

"Kun kasa yarda dani Momi. Da zinar halina ce da na yi ta inda babu mai ganin aibunta, kuma da ban fada maku ba balle ku san na aikata.
Momi ki yarda dani, wallahi-wallahi ba zan kara ba, kuskure ne wanda ba wanda ya fi karfin yinsa.
Ki yafe ni Momi, ki tayani rokon dan uwana ya yarda dani. Ku yi min kyakkyawan zato, kada na mutu ba tare da shaidar arziki daga bakin ku ba...." Ta ci gaba da kuka.
Momi ta dube ta sosai ta ce,
"Kina tunanin da shari'ah ake bi a wannan zamanin da ba a jefe ki ba?"
Ta fiddo ido kwalala! "Momi duk da sahihancin tuba na da nadamata?"
Momi ta ce,
"Wannan ne dai ban sani ba, sai dai ki tambayi malamai. Lailah kin bani tsoro sosai, duk tarbiyyar da na maki?"
Ta sa havar gyalenta tana share hawaye.

Hankalin Lailah ya kara tashi, ita ma ta kama kuka. Suna cikin kukan Sanah da Najat suka shigo aguje suna kokawa a kan 'yar tsana, dole suka share hawayen Lailah ta raba rigimar suka fita.
Lailah ta dago jajayen idanunta ta ce, "Momi me zan yi ki yi farin ciki dani?"
Ta ce,
"Aure".
Ta fyace hanci da 'tissue' ta ce,
"Insha Allahu Momi kamin in gama karatun nan na shekaru biyu zan kawo miki mijin aure na".
Momi ta ce, "Da dai kin yi wa rayuwarki gata, amma ba wannan neman duniyar ba".

Ranar litinin jirgin Egypt - Air ya sauke Lailah a birnin Jiddah, ta yi masauki a AL-JAMJOUM zuwa washegari ta bi bus ta wuce cikin Makkah da niyar aikin Umarah.
Kwanan ta uku a Mecca cikin aikin Dawafi da neman gafarar Ubangiji a kan komai ma, tun safe har dare ban da lalurar dan Adam ta ci da sha da shiga bayan gida ba abin da ke raba ta da dakin Allah.
Daga nan ta wuce Madinah, ta kai ziyara shabbaki da duk inda ya kamata. Kwananta biyar ta wuce Jami'ar Ummul-Kura.
Duk wasu cike-ciken takardu na 'registration' da ma an riga an gudanar da su ta computer, sai dan abin da ba a rasa ba.
Ta zavi zama cikin 'hostel' din dalibai don ya fi mata kwanciyar hankali, ta soma karatunta cike da himma da karfin zuciya.
Bayan tsayin watanni uku suna karatu suka samu hutun sallah break. Ta yi 'booking' jirgi sai Egypt. Inda shigowarta harabar gidansu kenan ta soma cin karo da taron yara sa'o'in su Sanah kowanne ya ci kwalliya kamar ranar ne sallah.
Sanah da Najat sun dora wuka kenan za su yanka 'cake' din 'Birthday' din su suka hango ta tana ratso mutane. Suka yi wancakali da wukaken hannunsu suka sheka suka rungume ta.
"marhaba biki Ya Ablah" (Ablah suna ne da suke kiranta da shi sau tari, wanda ke nufin Yaya)"
Dole sai tare da ita aka yanka 'cake' din suka daddanna mata a baki aka yi tafi, sannan kawayensu suka soma rero wakar 'happy birthday' cikin harshen Larabci, na cikar Sanah da

Najat shekaru goma-goma.
Don haka wunin ranar zungur hidimar da suka wuni yi kenan a gidan har magariba. Sujood na asibiti an ba ta 'bed-rest' tana laulayin ciki mai wahalarwa.
Ba su samu kevewa da Momi ba sai lokacin barci. Suna hirarsu a hankali irin na da da mahaifi. Lailah na ba ta labarin jami'ar Ummul-Kura da irin tsarinsu wanda ya bambanta da na Azhar. Momi ta ce
"Af! Kinga kuwa na manta mutumin nan da ya rako ki Bahaushe ya zo bakya nan".
Saura kadan Lailah ta fado daga gadonta, Momi ba ta yi aune ba sai ganinta ta yi durkushe a gabanta, kirjinta kamar ya fashe saboda bugu.
Ta ce, "ABBAS?"
Momi ta ce, "Kwarai haka Isma'il ya gaya min sunansa".
Ta ce, "Ya tafi?"
Momi ta ce, "Tun a ranar, domin daman a kan hanya yake zai wuce gida Najeriya daga London. Ya ce ya zo ne ya gaishemu kawai, bai yi tunanin kun rabu da Mohd ba, ya dauka kina Najeriya".
Lailah dai gaba daya ta bushe a zaune ne don gigicewa, don ma tana kokarin saisaita kanta kada Momi ta fahimci rikicewar ta.
To amma ai Momin ba karamar yarinya ba ce, ta fahimci akwai wani muhimmin al'amari tsakanin Lailah da abokin tafiyarta, tun ranar da ta kasa cin abinci don an sanar da ita ya tafi, ba tare da ya yi mata sallama ba.
Ta ce, "Hala saurayinki ne tun a Ingilar taku?"
Ta zaro ido kuru-kuru ta ce, "Wane irin saurayi Momi?"
Ta soma bai ma Momi labarin haduwarta da shi tun a filin jirgin saman Abuja ranar da za ta tashi zuwa Birtaniya, da yadda ya taimaika mata da rayuwarsu a makaranta da gida.
Ta kara da cewa, "Ko da kuskure mutumin nan bai tava sauya kallon da yake min na kanwarshi ba, ya taimake ni a kowanne fanni na rayuwata a can.
Ya kare min mutuncina domin da dama kallon mijina ake yi masa ko Yayana, don haka babu wani mahaluki da ya tava dosa ta da zancen banza har na baro Ingila".
Ta kare da cewa, "Momi shi ya yi min nasiha na dawo gida, shi ya hanani zub da ciki, Momi Abbas yana da kirki sosai, kuma wallahi Momi shine irin mijin da nake mafarkin samu a rayuwata".
Momi ta yi murmushi ta ce, "Har kin sa ina son shi".
Ta ce, "Kirkin shi ya wuce duk yadda kike zato Momi, ga tarin ilimi. Shi ma (Philosopher) ne, don da ya kare karatu a take makarantar ta dauke shi cikin sababbin malaman ta".
Ta ce, "Dan ina ne?"
Ta ce, "Kano-Nigeria".
Ta ce, "Garin su mahaifin ku...."
Lailah ta ce, "Yauwa Momi, wai Babanmu ba shi da wasu 'yan'uwa ne a can Najeriya?"
Ta ce, "Mahaifin ku maraya ne, amma akwai Baffanninsa guda biyu Kano a unguwar Kabara, ban sani ba ko suna raye".
Lailah ta ce, "Ya kamata mu neme su Momi, kinga dai yadda rashin dangin uba ya janyo min gori da rashin kima a gun Hajiyar Mohammed".
Ta ce, "Isma'il ya san inda suke, idan kun kara dawowa sai ku je, amma ni ba inda za ni".

Lailah ta saki wannan hirar ta ce,
"Momi bai ce zai sake dawowa ba?"
"Wa kenan?"
Cike da jin nauyi ta ce,
"Abbas".
Sai ta yi murmushi kawai ba ta ce mata komai ba.
Ko da Isma'il ya shigo daukar ma Sujood wasu kaya da za ta yi amfani dasu a asibiti bai ce da ita komi ba game da zuwan Abbas.
Ta kasa daurewa ta ce, "Zan iya binka muje wajen Sujood?"
Ba tare da ya juyo ba ya ce, "Basu barin aje dubiya kar a damu mara lafiya".
Ta ce cikin fargaba, "Ashe Abbas ya zo?"
Ya juyo yana kallon ta, shi kansa ya rasa dalilinsa na tsanarta, ya ce, "Eh, wani abune?"
Ta hadiye kukan da ya taho mata ta juya da gudu ta yi gidansu ba tare da ta ce da shi komi ba.
Ta kwanta rub da ciki a kan gado, tana kuka mara sauti, wanda ta toshe shi da bakin mayafin abayarta kada Momi ta jiyo sautin kukanta.
Ba ta ji murda kofa da rufe ta ba sai zaman mutum a gefen ta. Kamshin turaren shi a gefenta ya sanya ta dagowa da sauri, Isma'il ne.
Ya mika mata hankicif dinshi ya ce, "Share hawayen". Cikin sassanyan Larabci.
Ta karva ta share amma ba ta dube shi ba. Ya yi shiru sannan ya ce, "Ki gafarce ni, haka nan na samu kaina da daina ganin farin ki. Domin........"
Ta kai hannunta ta toshe masa baki don ba ta son jin abin da zai fada, zancen nan ne dai da ba ta so a kara tuna mata.
Ya sauke hannunta daga bakinshi ya ce, "To ki yi hakuri".
Ta ce, "Na yi".
"Abbas ya zo baki nan, ya yi mamaki kwarai jin cewa all these while kina gida. Amma baki neme shi ba, na gaya mishi ko waya baki rikewa. To amma zai dawo".
Ba ta so ya ga ta fiya ci-da-zuci. Da ta tambaye shi yaushe zai dawo din?
Ya mike ya fita yana cewa, "Sujood ta damu tana so ta ganki. So ki daure ki yi ko sati ne ta dawo ta ganki".
Ta ce, "Allah sarki Sujood, Allah ya raba su lafiya".
Ya amsa
"Ameen".

Washegari ta tashi da nishadi, don haka ta je aka yi mata kunshi da gyaran gashi, akaifa da wankin kafa. Ta wuce makaranta ta dawo.
Bakuwar mota ta gani a harabar gidansu, ta karasa ciki da sassarfa bayan ta rufe motar ta.
Mohammed ta fara yin tozali da shi, sannan Sa'eed da wasu kyawawan mata guda biyu da fara da baka.
Tana tafe cikin falon har hardewa take yi, ya yin da Isma'il ke ta wadata 'dining' da abinci da abin sha shi da Amatullahi mai aikin su.
Momi na gefe ita da A'isha suna ta hira, Momi na ta zuba shakakkiyar Hausarta kamar jakar Kano.
Kallo daya Lailah ta yi wa Sa'eedu ta ga yadda ya rame ya lalace kamar ba shi ba, ta dauke kai

kamar ba ta ganshi ba.
Za ta wuce ciki Momi ta riko hannunta ta ce,
“Baki ga bakin naki bane?”
Dole ta zauna gefen Momin tana kallon su kawai da idanu. Sa’eed na kuka bayan shigar su A’isha sassan baki, yake rokonta ta yafe masa, ta yafewa Mohd.
Don a dalilinta yanzu Mohd ya aje aiki, ya ce, tunda aikin ne ya raba shi da ita, yake kuma barazanar raba shi da duk matar da ya aura to ya barshi, zai gwada wata sana’ar.
Kuma anyi masa aiki, yanzu haka A’isha na da ciki wata biyar. Wannan kuma Zanira matarshi ce, ita ma ‘yar uwarsu ce. Shi kuma ba shi da lafiya suga ta kama shi sosai.
Shi yana kuka Lailah na yi. A da kam ta yi alkawarin ba za ta tava yafewa Sa’eed ba har karewar numfashinta, amma a yau ta tuna wani karin magana da Hausawa ke cewa.
“....... Idan vera da sata.....to daddawa ma da wari”.
Sai ta ce, “Allah ya yafe mana bakidaya”.

Ta zage sosai ta karvi su A’isha, karva ta karshen mutuntawa. Shi dai Mohd sai ido yake binta da shi ganin yadda ta kara komawa yarinya danya sharaf ba ‘yar shekaru talatin ba.
Soyayya gaskiya ce, kuma har abada ba ta gushewa. A haka yana ji yana gani ya baro Lailar da a da mallakinsa ce.
Ba ta koma Saudiyya ba sai da Sujood ta fito daga ‘bed-rest’. Har da ita aka yi mata rakiya ta tashi ranar Asabar.
Ta tarar da abokiyar zamanta a dakin (Dhuha) ta riga ta dawowa. Ta gyare masu dakin tsab. Balarabiyar Afghanistan ce.
Suka ci gaba da karatu, wanda duk rabi bincike ne cikin manyan littattafai wato (research).

Tana tsaye gaban book-shelf na main library din Ummul-Kura, tana kokarin zaro wani littafi. Dai-dai lokacin da agogon library din ya buga karfe goma sha daya na rana, ya yi dai-dai da bugawar zuciyarta da faduwar gabanta. Dai-dai lokacin ta hango wani ‘giant’ yana tahowa cikin fararen kaya, iska na kada shi, yana tafe yana waya, ba ta san lokacin da littafin ya suvuce, ya fadi daga hannun ta ba.
Ba ta yi wani motsi ba har ya karaso . Ya russuna ya dauko mata littafin ya mika mata, sannan ya kama hannunta suka fito daga library din. Ta zamo kamar mutum-mutumi, sai janta yake tana binshi ba uhm-ba-umh-uhm.
A al’adarta tunda ta zo Ummul-Kurah, kullum sai ta kai ziyara shabbaki, kamar ya san hakan, don kuwa da ya tare tasi shabbaki ya ce ya kai su.
Kasancewar masallacin maza daban da na mata, a nan harabar masallaci ya sata ta yi addu’o’inta, shi ma ya yi. Suka fito ashe tuni ya yi masu ‘booking’ din mota wadda za ta kai su har cikin Mecca.
A cikin mota Lailah ke bin shi da idanu, yadda ya damke hannunta kamar wata matarshi. Abbas dinta.....abokin kan hanya!
Ya kara kyau na misali, ya kara murjewa. Ta yadda har ba ta gajiya da kallon kyakkyawar fuskarsa.
Ta sunkuyar da kai cikin siririn sauti ta ce, “Amma ka san hannun nan da kake ta rikewa, haramun ne ko?”

Ba ta kai ga rufe bakinta ba sai ya sa dukkan hannuwa ya rungume ta.

Lailah ta samu numfashinta yana sassarfa a cikin kirjin Abbas da kafadun shi. Ta yi ta kici-kicin ta kwace amma ta kasa. Ta kuwa daga hannu ta kai mishi wani wawan mari ya goce, hucin marin ya wuce ta gefen kunnuwansa. Ta fashe da kuka ta ce,
"Saboda na baka labarina shine ka dauke ni 'yar iska ko?
To bari ka ji, ko na fi iblis iskanci ba zan yi a cikin garin da manzon mu ke kwance ba. Kai malam tsaya da motar nan in sauka....."
Ya yi dariya sosai, sannan ya sake ta. Ya nuna mata agogon RADO dake daure cikin kwantacciyar sumar hannun shi.
"Karfe sha daya na rana wanda ya yi dai-dai da karfe biyar na yamma agogon mu na gida Najeriya.
Baffanninki Malam Ado da Malam Ilyasu da waliyyinki Isma'il suka damka mani igiyar rayuwarki, suka shaida na zama mijinki har zuwa karshen numfashinmu".
Sai jikinta ya yi sanyi, ta rasa abin cewa, kuka za ta yi ko dariya? Bakin ciki za ta yi ko ko farin ciki? Bata sani ba.
Ya sake runtse hannunshi cikin nata sosai ya soma ba ta labarin yadda al'amarin ya faru. Ta tabbatar karfe sha daya na rana ta ji faduwar gaba da bugawar zuciya, ashe igiyoyin Abbas ne suka hau kanta.
Ya ce,
"Na je Egypt watanni biyu da suka wuce in gai da Momi da Isma'il. Yake gaya mani cewa kina nan Madina. Na tambaye shi Umrah kika je? Ya ce, a'a, karo karatu ne, don aiki kike yi. Ya ce kun rabu da mijinki tun wancan karon. Ban yi kauron baki ba ko A BARI YA HUCE.... na ce da Isma'il ya yi mani alfarma, ya aura min ke.
Ban san ya suka yi da Momi ba, ta ce, in ba ta lokaci za ta yi nazari tana so ta ji daga bakin ki. Sanda na sake komawa ta ce ta gama nazarinta in turo wakilaina wajen Baffanin ki a Kano su za su sake daura miki aure.
Don haka Isma'il ya taho Najeriya muka hadu, muka je Kabara aka daura auren, sadakinki yana hannun Isma'il
Ba yadda bai yi dani ba in bari za ki zo karshen watannan ban saurare shi ba, dole ya bani adireshin inda zan same ki wato jami'ar Ummul-Kura.
Ban sha wuya ba aka binciko min lambar dakin ki. Na tura a kira ki sai abokiyar zaman ki ta ce kina nan. To kin ji.
Nima ba dan iska bane. Da kuma dan iskan ne da ba yau zan fara ba......" Ya karasa da dariyar da ta cunkushe masa ciki.
Ita dai Lailah binshi take da ido, mamaki ya hanata magana. Hakika tana cikin mutane masu sa'ar samun duk abin da suke so a rayuwa. Da da hali da itama ta rungume shi ta yi kukan godiya ga Allah a kan kirjinsa.
Sai yamma lis suka shigo cikin Mecca, ko abinci basu nema ba sai da suka fara yin (Dawafi) suka yi sallar magariba da isha da nafiloli. Sannan suka je wani 'restaurant' suka ci abinci, daga nan suka taho Ka'aba suka ci gaba da gabatar da ibadodinsu.
Sai asuba suka koma masauki, wanka kawai suka yi ya shige ciki ya kwanta yana biyan bashin barcin da bai samu ya yi ba saboda godiya ga Allah da ya mallaka mishi abin da yake so, bai

kuma tava tsammanin samu ba, ya samu a bayan fidda rai.
Ita dai Lailah ko gezau, tana zaune dungurgur  a kan kujera tana kallon talabijin din da ke ta aiki ita kadai ba ta san me suke yi ba.
Kamar ka ce kyat.....! Ta arta a na kare. Don ita kwata-kwata yanzu kowanne namiji ma tsoron shi take ji balle ya kai hannu ya tava ta.
Bai tashi ba sai karfe goma na safe, shi ma din kiran Isma'il ne ya tashe shi, suna gaisawa ya mikawa Laila.
Bayan sun gaisa yake mata bayanin da Abbas ya yi mata, ta ce a sanyaye,
"Toh!"
Momi na karva sai ta valle da kukan kaunar da take mata. Tana so ma ta yi mata godiya amma ta kasa.
Momi ta ce,
"To kukan na mene ne?
Ke fa da bakin ki kika gaya mani kina son Abbas?"
Ta share hawaye tana murmushi ba ta ce komai ba. Ta ce, "A'a, in kin daina son nashi ne ki gaya mani sai in ba shi hakuri ya karvi sadakin shi, tun da dama bai zo hannun ki ba."
Ta yi saurin cewa, "A'a Momi".
Ta yi dariya ta ce, "To shi kenan, a sha amarci lafiya, ki kula da shan 'fresh milk' da cin dabino da shan zam-zam tare da inibi".
Kunya ta kama ta, don ta san sune abubuwan da take ba ta sanda za ta yi auren fari.
Abbas ya fito daga shi sai 'short – nicker' kanshi da tawul yana goge ruwan cikin sumar kanshi.
Kallo daya ta yi mishi ba ta kara ba ta kara takurewa a cikin kujera. Ya juya mata baya yana dariya ya zuba farar jallabiya mai santsi, ya fesa turaren shi (one-man-show), ya fesa turaren baki (mouth fresh), sannan ya iso gare ta.
Ya zauna a gefenta yana so ya ja ta jikinshi amma ya lura da yadda ta ke a tsorace da shi. Sai ya yi murmushi ya mike zuwa hammam (bayan gida) ya hada mata ruwan dumi cikin kwami, ya ce ta yi wanka ta ji dadin jikinta su fita su nemi abin karyawa.
Ba don ta so ba ta mike ta shiga wankan, amma fa ta kukkulle kofar bandakin da (jam-lock) sannan ta fara wankan, shi kuma ya sauka kasa ya samo musu abin karin kumallo.

****

Kwanansu uku suna Umrah, amma ya kasa gane kan hutsuwar amaryar tashi. Ba ta umh ba ta umh-umh, duk ta takura kanta.  Maganar duniyar nan idan zai yi sai dai ta bishi da 'eh' ko 'a'ah'. Har yana mamaki kamar ba Lailan shi ba.
Ya kuma soma tunanin ko dai ba ta son auren ne. Ta hana mashi amarcin har zuwa ranar da za su rabu, dama shi a kan hanya yake zai wuce London.
A daren ranar dai ya rantse yau sai ya gane abin da Lailah take nufi da shi, ba ta son shi ne ko iya shege ne? Ita ba yarinya ba balle a yi mata uzrin kuruciya.
Tana zaune cikin kujerar falon hotel din da suka sauka, hannunta remote ne tana canza channel ya kwankwasa kofar.
Ta tashi ta bude idanunshi cikin nata aka jefe shi da wani miskilin murmushi. Turata cikin dakin ya yi da kafadunshi ya aje ledojin dake hannun shi. Sannan ya juya ya karvo na hannun yaron hotel din da ke waje ya aje gefe ya rufe kofar.

Ba ta yi aune ba sai ji ta yi ya sunkuce ta ya yi sama da ita. Bai dire ta ko'ina ba sai cikin kwamin wanka, duk da kayan da ke jikinta.
Ta ce, “Haba Abbas, ya za ka jikani? Yanzu na yi wanka fa”.
Bai saurare ta ba ya saukaka kayan jikinta ya manne bakinta da nashi da wasu irin matsiyatan ‘kisses’ da ba ta tava sanin akwai irinsu a duniyarta ba.
Ya saki ‘shower’ a kansu, cikin wani sabon al'amari da Lailah ba ta tava tsintar kanta a kwatankwacin sa ba.
Ashe dai wannan ita ce soyayyar, na baya duk shirme ne? Wane Sa'idu wane Yayansa!?
Wadanan MANYAN MAZA ke magana…., wadanda basa furta SO ko I luv u a fatar baki, sai dai ZUCIYA da GANGAR jikinsu ya nuna.
Fatan alkhairi gare ku ABBAS DA LAILAH! -Takori

Washegari ta kama Lahadi, Abbas kam yau sallar asuba a gida aka yi ta, Lailah ta samu kanta da kasa hada ido da angon nata. Shi kuma hakan bai hana shi gudanar da amarcin shi ba, soyayyya ruwan zuma gangariya ake gunadarwa cikin kwanaki biyun da suka biyo baya.
Ya kasa amincewa wai ya tafi ya bar Lailah, har na tsayin watanni uku. Ga ayyuka ya bari masu dimbin yawa. Ita kanta Lailar ta baro nata ayyukan a makaranta don haka ta karfafe shi da su daure su tafi, lokaci kankani ya rage mata ta kammala gaba daya sai su tsara mai yiwuwa.
Sai da ya kaita har Madinah tamkar ba za su rabu ba, hakan dai aka daddaure aka ciccije aka rabun da alkawarirrika masu yawa da ma'ana.
Ya biyo Ajrah (tasi) ya dawo Jiddah, karfe goma na daren ranar ya bi British-Air zuwa London.

Tana canza kaya a dakin su Dhuha ta yi sallama ta shigo, kallon mamaki ta yi mata tare da tsoro, ta ce cikin harshen Larabci.
“Ke kuwa ina kika shiga Lailah har tsayin kwana biyar? Yanzu haka daga kai ‘report’ din vatanki nake ga ‘security’ din makaranta. Hankalina ya tashi sosai”.
Lailah ta yi dariya ta ce, “Kai Dhuha? Ana yankan kai ne a Saudi-Arabia?”
Ta ce, “Ina na sani, tun da na ga wani ya zo neman ki kuma tun daga ranar ne ban kara ganin ki ba, ba dole in yi zaton ya sace ki ba?”
Lailah ta kara yin dariya ta ce, “Sai ki koma ki gaya musu gani na dawo”. Ta juya tana cewa, “Yanzu kuwa”.
Lailah ta kwanta a gadonta ta lumshe lumsassun idanunta tana tariyo rayuwarta filla-filla tun daga kuruciya har girma.
Ta tuno Mohammed da rayuwar ta dashi, ta tuno Sa'idu. Sai ta samu kanta da yi musu addu'a. Ta kuma gode Allah da ya musanya mata da miji na gari dai-dai yadda take buri a rayuwarta ta duniya.

****

Bayan shudewar watanni uku suka samu hutu ta koma gida Egypt, ta tarar da haihuwar Sujood, ta haifi kyakkyawar yarinya mai kama da Momi Najla. Wannan ne ya sa take yanayi da ita Lailan, don duk cikinsu ta fi su kama da Momi. Duk yadda ta so ayi shagalin suna da ita hakan ya faskara, sakamakon rashin isasshiyar lafiya, komai ta ci sai ya dawo ba ta ko son ganin abinci ko kamshin sa.

Daga rowan lipton din ‘Tetley Tea’ sai gugguru, su kadai ne in ta ci ko ta sha ba ta amansu. A matsayin Sujood na cikakkiyar likita, a take ta gane abin da ke damun Antin tata, ciki ne na watanni biyu ko Momi ba ta gane ba.
Sujood ta rubuta magungunan da za su taimaka mata aman ya tsaya ta ba wa Isma’il ya siyo mata ba tare da ya san na wace ce a cikin su ba, tun da ba ranar ta fara aiken shi siyan magani ba.
Baby ta ci sunan Momi wato NAJLA, suke kiran ta Nawal. Sujood ta dage da kula da Lailah don duk hidimar Nawal Momi da su Najat ke yi, tsakanin ta da ita sai shan nono wanda sai ta wuni ba ta sha ba, saboda Momi tana ba ta madara.
Suna wajen motsa jiki Sujood ta dakata ta dubi Lailah ta ce,
“Antinmu ni fa kallon mai ciki nake miki, ki daina edcercise dinnan”.
Lailah ta jinjina kai ta ce,
“Nima na dade da zargin kaina, don watanni uku kenan rabona da al’adata.....”
Hawaye suka zubo mata na tunawa cewa; wannan dan HALAAL ne a jikinta, wanda kowa zai karva.
***
A yammacin ranar Abbas ya iso. Washegari suka wuce London. Ga mamakin Lailah Abbas ya tashi daga gidan hayarsu, gida guda Muslim College ta ba shi a cikin gidajen malamai. Aka koma rainon ciki, tattali da kulawa wurin Abbas wane na baya, wanda ake da shamaki a cikinsa.
Watan ta guda ta koma Ummul-Kura. Ta karasa rubutunta na (project) ta mika, ta amshi kwalin Dr. of Philosophy (PhD). Suka tattara suka koma Ingila.
Haka rayuwarsu ke garawa cikin nasara da ci gaba kala-kala. A NHS Lailah ta haifi ‘bouncing baby’ dinta mai kama da ubansa har duhun kalar.
Abbas ya ba shi sunan Isma’il, a cewar shi shine ya shige masa gaba ya ba shi Lailah a lokacin da ya riga ya fidda rai.

ABBAS da LAILAH, sun zamo manyan-manyan malaman Falsafa a kasar England, a babbar Jami’ar Musulunci (Muslim College) da ke birnin London.
Akai-akai kuma suna zuwa gida Najeriya gai da Baffaninsu, da yi musu hidima iyakar karfin aljihunsu. Balle Egypt kuma da ba sa yin watanni uku kwarara ba su zo ba.

MURFI

A'study’ ya same ta tana shirya litattafanta cikin kabinet, a gefe Isma’il ne (Sayyid) da Khalisa (Sayyidah) tare da autarsu Najwa suna wasansu cikin na’urar koyon karatu mai Alifun-Ba’aun. Ya yin da babban yaya wato Sayyid ke gefe yana ta rubuce-rubucen sa, dukkansu basu ankara da shigowar Daddyn ba, kasancewar kowannen su ya mai da kai ga abin da yake yi ko sallamar shi basu ji ba.
Ya karasa ga Momin ta bayanta ya rungume ta, kamshin turaren shi kawai ta shaka ta lumshe idonta tana murmushi.
Ya dora habarshi a kafadunta ya ce, “Momy fatawah nake nema”.
Ta ce, “A kan me Daddy?”
Ya ce, “A kan karin aure?”
Ta zumvura baki ta zame shi daga kafadunta ta ci gaba da shirya littattafanta tana cewa,

“Bani da sani a kan wannan sam!”.
Ya juyo ta ya ga yadda ta yi kicin-kicin da fuska sai ta ba shi dariya, ya ce, “At thirty five Momi kin girma fa, ki barni in dauki sweet sidteen, ta zo daga Muzambikue yin Diploma, shine nake neman fatawa a kai.
Shin wanda Allah ya yi wa baiwa da mace mai ilimi, kyautatawa, biyayya, tausayi da jin kai ga mijinta, tare da kular masa da tarbiyyar ‘ya’yansa da gamsuwar sa a shimfidar su, ta tsare masa mutunci da dukiya idan baya nan, ta zamo mai himma da kokari ga son faranta masa rai, ta cancanci ayi mata kishiya?”
Abin ma ita sai ya ba ta dariya, ba ta san sanda ta ce,
 “Idan mijin butulallen Allah ne, ba sai ya yi mata ba?”
Ya jinjina cikin dariya ya ce,
 “Kada fa ki manta, Ubangiji (S.W.T) cewa ya yi, “Ku auri abin da ya yi muku dadi daga daya-daya, biyu-biyu, uku-uku ko hur-hudu.....”
Ta zame cikin sanyin murya ta ce,
“Don Allah Abbas ka auri goma-goma.....” Sai hawaye suka zubo.
Ya kai hannu ya shafo hawayen yana murmushi ya ce,
 “Ni din me Lailah? Da za ki zub da hawaye a dalilina? Idan kin ga na hada rayuwa da wata, to sai a Aljannah, idan Allah ya yi min kyautar Hurul-eeni, sai in hada da ke ta zama kwarkwara........wannan alkawari ne Lailah. You are more than enough to me......and I’m only yours!” Ya kara rungume ta.
Ta yi murmushi wanda ya fito tun daga karkashin zuciyarta, kaunar mijinta ta kara  kwanciya cikin ranta kamar ta hadiye shi don so da kauna. Sai itama ta rungumeshi sosai. Sannan ta yi mishi nuni da Sayyid wanda ya aje rubutunshi ya zubo musu ido.
Ya sake ta ya koma gabansa ya zauna, ya kama hannun shi kafin ya yi magana yaron ya riga shi.
“Me ta yi maka ka sa ta kuka?”
Suka kyalkyale da dariya shi da Lailah. Ya dora hannun daman shi a kan yaron ya ce.
“Ban yi mata komai ba, tsokanarta na yi na ce zan kawo muku Aunty, shine take kuka”.
Ya ce,
“To Daddy ai mu muna son Auntyn”.
Ya ce,
“Ban isa ba Sayyid in yi abin da Momi ba ta so, ko ina so kuwa, balle ma wasa nake. Ba na son kowa sai Momi.....ni mijin ta-ce ne, ku kawai nake so..... I luv you all......” Ya hada su ya rungume gaba daya.

MASHA ALLAH LAKUWWATA ILLAH BILLAH![12/17/2019, 17:50] Takori: WASAN KANIN MIJI SHIMFIDA
1/MUHARRAM HIJIRIYYAH
HANYA MAI HADIN ZUMUNTAR DOLE!

Dare ne mai tsananin sanyi, cikin watan Nuwamba. Hazo ya lullube duhun daren ta yadda ya fidda launi mai haske kamar hadadden hadari, wanda ya takura da yawa-yawan al’ummar birnin

tarayyah.
Za a iya kimanta lokacin da misalin karfe goma dai-dai na daren ranar Alhamis. Dai-dai lokacin da LAILAH UMAR BALLAH, matashiya 'yar kimanin shekaru (25) ta iso filin jirgin saman Abuja. Laila tashe take da 'yar madaidaiciyar 'troller' dinta ruwan toka a hankali, kamar mai tsoron kada santsin tangaran din takawa (tile) ya tikar da ita.
Rataye a kafadunta na dama, jakar mata ce baka mai girma samfurin (vincci) data hadiye dukkan komatsanta masu muhimmanci.
Laila sanye take da doguwar abaya da mayafinta bakake wul! Kirar Oman, da takalmi rufaffe maras tsayin dunduniya. Ta karasa ciki a hankali ta hau kan layi domin mika kayanta ga masu binciken kwakkwafi na cikin gida (customs) kamin a auna su cikin jirgi. Tana daga cikin (boarding passengers), masu tashi zuwa kasar England, a wannan daren mai tsananin sanyi, mai kunshe da dimbin tarihi da kuma sabuwar rayuwa a gare ta.
Da ganin yadda Laila ke shige da ficenta,  kai tsaye, babu tsoro, babu dari-dari, wajen mika (passport) dinta mai dauke da Kambun Sarauniya (UK Visa) gami da katin  shaida (ID Card), a duk inda anka bukaci hakan kamar yadda ka'idar matafiya ta filin jirgin ta shimfida, ka san ba ta da duhun kai; wato dai ba yau ne ta soma keta hazo ba. Sai dai kuma kallo daya za ka yi wa kayatacciyar fuskar Lailah, ma'abociyar haske, zati da kamala, gami da kwarjini bayyananne daga sarkin halitta, ka karanto matsananciyar damuwa, tsoro da firgici, har ma da tashin hankali gami da matsananciyar nadama tattare cikin fararen kwayar idanunta.
Sai dai kuma ta kasance daya daga cikin irin mutanen nan da da wuya ka karanto damuwarsu a fuska farat daya, kasancewarta ma'abociyar fuskar murmushi. Duk da haka a yau, babu wannan murmushin, babu wannan annurin. Kamar yadda zuciyarta ke cunkushe da manyan al'amura masu girgiza zuciyar diya mace, tare da jefata cikin rayuwar ha'ula'i, haka dan kankanin bakinta ke tsuke tsam! Kamar ba ta tava murmushin ba a tsayin rayuwarta.
Ta daga kanta sama a hankali zuwa ga allon kwamfutar dake manne a saman kanta, mai dauke da (travel-routine) na ranar gaba daya. (LONDERS-HEATHROW 12:am), kenan akwai sauran mintuna talatin a gabanta, kafin su tashi.
Don haka ta bi layin sauran matafiya 'yan uwanta a sansanin da aka ware domin tsimayen lokacin tashin jirgi, ta samu kujera ta zauna. Ta bude jakarta ta dauko karamar gorar ruwan (Faro) mara sanyi, ta murde ta kai bakinta tana kwankwada, cikin wani irin yanayi mara fasaltuwa. Tsabar kishi ne ko ko gigicewa ce?
Tun da ta kafa ruwan a bakinta ba ta iya ta sauke ba, sai da ta zuke robar gaba daya. Gardin ruwan ya ratsa busashshen makoshinta da bakin cikin DA NAMIJI ya busar rayas! Ya saukar da 'yar kankanuwar nutsuwa a zuci da gangar jikinta. Ta dire robar a kas, ta aje dogon numfashi, kamin daga bisani ta sanya fuskarta cikin cinyoyinta ta fashe da kuka.
Wani irin kuka mai girgiza zuciya Laila ke yi, wanda ba ta tava yin shi a rayuwarta ba, kamar yadda tunaninta bai tava bata wai watarana irin haka na zuwa da za ta yi shi ba. Balle a kan MAZA, da ta raina ma wayau. Domin tana ganin ba ta daga cikin irin matan da ake cewa suna dandanar bakin cikin DA NAMIJI. Tun da babu ta inda Ubangijinta ya rage ta; tana da kyau, tana da gata, tana da gishirin rayuwa mai tsada (ilimi). Uwa uba nasabar mafi soyuwar jinsi, wato Arab.
In haka ne to mene ne silar wannan balaguron gare ta? Zuwa inda ba Uwa, ba Uba, ba masoyi balle dangi?

Har aka yi kiran (passengers) domin bincike na karshe wanda daga shi sai shigewa jirgi Lailah ba ta ji ba. A gefenta yake zaune, tun shigowar ta, yana nazarin wata takarda mai dauke da taswirar Birtaniya ciki da bai dinta.
Ya mike tsaye a yayin da kiran ya tsinkaye shi. Ya dauki jakarshi dake aje gefe mai dauke da kwamfutar (laptop) tare da shafa aljihun bayan shudin wandon 'jeans' dake jikinsa domin tabbatar da zaman tikitinsa da passport. Ya tabbatar suna nan. Don haka ya bi jerin-gwanon matafiyan dake shiga jirgi bayan an bincike su. Sai dai har zuwa lokacin sautin shesshekar kukan yarinyar mai taushi da raunana zuciya, ya kasa daina amo cikin kunnuwansa.
Ya yi taku a kalla biyar zuwa shida, amma ya kasa daurewa. Ya rage sassarfa, kana ya juyo. Ya kai idanunshi ga sashen da ya barta. Har zuwa lokacin tana nan inda ya barta, har zuwa lokacin kuma kukan take, kanta cikin cinyoyinta. Babu alamar tana da masaniyar cewa kowa ya tashi daga wajen ya barta, kai babu alama ma ta tsinkayi kiran da aka yi musu.

Wankan tarwada, dogo mai tsararren tsayi, ma'abocin ingarman jiki. Cikakkiyar fuska mai yalwar dara-daran idanu da wadatar dogon karan hanci zurr! Kai ka ce saita shi a kai a tsakanin idanunsa.
Ma'abocin yalwar girar idanu kwantacce, gami da gargasa na gashi a kowanne gava mai bukatar hakan a jikinsa. Dogo ne sosai mai nitsatstsen taku da wasu irin idanuwa masu sheki da daukar hankali, kai ka ce ruwan zaiba ne aka diga masu (oily-eyes). Fatar jikinshi shine bayyanannen sirrin kyawun da Allah yai mishi (fata ce irin mai taushin gani a ido). Sai ko wani irin haske (cool) mai nuni da gogayya cikin zuzzurfan ilimin boko, wanda dole ne ga duk wani bakin mutum mazaunin yankunan Birtaniya. Da gani babu tambaya, daga duba na farko, kaga Ba-kanon usuli.
A sannu cikin nutsatstsen takun shi ya karasa gare ta, ya tsaya dai-dai saitin kanta, ya dau kimanin mintina biyu a haka kamar mai nazarin, ya kamata yayi mata magana ne ko a'ah? Baya daga cikin halayyar sa shiga haular da ba tashi ba, kamin daga bisani yayi kundumbala ya yi mata sallama cikin murya mai taushi.
"Kina daga cikin masu tashi kuwa?"

A hankali Lailah ta cira kai, kamar a dan razane. Ta kai duban ta ga sashen da sautin ya fito, ba tare da duban fuskar mai maganar ba, idanuwan nan farare tas sun canja launi sunyi jawur tamkar an gumbuda musu barkono.
Ta mai da dubanta zuwa hagunta da damanta, wayam, babu kowa. Ita kadai ta rage, ta yi hanzarin mikewa ta rataya jakarta ba kuma tare da ta sake duban mai yi mata magana ba. Ta ce, "Na gode". Ta wuce babu ko waiwaye.

"Hakika Mallam Nasara kullum kara samun fasahar kirkire-kirkire yake…..". Laila ta ce a zuciyarta. "Wato jirgin ma yanzu sai dai kawai ka shige shi, ba tare da ka ganshi ba. Kafar shi kafar hanyar da ka fito, sai dai kawai ka ganka cikin wani daki wai shi jirgi mai fuka-fukai. Inama ace yadda yake da fasahar kirkire-kirkire, haka yake da fasahar rungumar kowanne jinsi da zuciya daya, ba tareda wariyar launin fata ba?
A bayyane yake bature bai tava son baki. Ko ya so shin, akwai voyayyen dalili. Muhimmi shine

idan har ya san zai samu amfana daga gareshi.
An ce an bamu ‘yancin kai amma ba’a daina bautar damu ba.  Turawan Ingila basa aiki, kwance suke a gida, mu din dai har yau mu ke yi musu bauta. Suna kara bunkasa suna kara havaka muna kara durkushewa. Masu fasahar mu sun tattare a gindinsu suna musu bauta. Suna kara bunkasa su. Sun ki suzo su gina al’ummar su. Sun kasa ganewa har yau cewa shi dinnan (nasara) makiyin su ne. Kansa kawai ya sani da al’ummar sa, su ‘bayi’ ya daukesu. A kullum kara like masa muke muna kara dakusar da kan mu. Bamu da abin koyi sai shi da akidojinsa na banza, alhalin halakar da kan mu kawai muke yi.

Ta juyar da idanunta ta wulwula cikin jirgin. Daga farkon shi har karshen shi bakaken fata kawai take hange, musamman kabilar Yarbawa. Suna tururuwar tafiya bauta ma bature. Sun baro iyaye da kakannin su cikin gonakin kauyuka suna noman Doya, Manja da Cocoa. Don samun abin kaiwa baki, basa ko tuno su. Jar fatar usli dake cikin jirgin ‘yan kalilan ne, wadanda yawanci aiki ne ya kawo su Najeriya. Lailah tayi tsaki tare da huci don karin bakin-ciki. To amma me zata iya a kai? Sai ido sai du’a’i.
Tunaninta ya dawo ga tata rayuwar, da dalilin nata balaguron. Tana da yakinin cewa ba bautawa Bature zata ba, kamar yadda mutanen mu suka raja’a a kai a UK. Neman ilmi zata. Domin ta yi wa kanta hukuncin da addini ya tanadar a kanta, wanda ita kanta ba ta sani ba,  a yanzun tana nan a musuluncinta ne? Koko ta fita ne?
Bata yarada da cikar imaninta ba….., bata yarda da kanta ba…..! Tana cikin rudani, tana neman mafita,….. tana cikin nadama, tana cikin tsoron rashin cikar imaninta, tana cikin tsoron mahaliccinta, tana cikin tsoron anya Ubangijinta zai yafe mata?
“Sa’eed!” Ta fada cikin rishin kuka. “Sa’idu!” Ta sake maimaitawa cikin karkarwar murya. A yayin da ta zauna a mazauninta na kujera mai lamba (22), hannun dama, na cikin jirgin (British Airways). Kafin wasu irin dumammun hawaye su kara wanke kyakkyawar fuskarta.
Ba kuma tare da ta yi wani kokari na sharewa ko voyewa ba ta ce a fili…..
“Allah ya isa tsakanina da kai Sa’eedu….Allah Ya isa!!!”
Ta sake mai da kai cikin cinyoyinta ta ci gaba da kuka.
Da a ce cikin al’ummar mu ne Lailah ke yin wannan sambatun, la-shakka da an tsaya kallon zararriya-mahaukaciya, amma ga wadanda ba halayyarmu daya ba, ko kallon ta ba su yi ba, kowa ta kansa yake, kowa kansa ya sani.
Babu wanda ya kula ya damu da halin da take ciki sai mutum guda, musulmi Bahaushe dan uwanta, wanda har zuwa lokacin ke bibiyarta da ido, da zuciya.
“…..Budurwa har budurwa…., kyakkyawa har kyakkyawa, mai kyau matuka. Amma Allah sarki! Watakila tana da ‘Psychological Problem”.
Ya raya cikin wasikar jakinsa.

Hakika duk inda musulmi yake, zuciyarshi ta sha baban da ta arne ko ya ya ne. Allah ya halicci dan musulmi da zumunci ga dan uwansa musulmi, ko da basu hada jini ba, wato ko da haduwar kan hanya ce. Musamman a inda suke sune ‘minority group’ wato a inda suke da karanci. To hakan ce ta faru da ABBAS. Ya kasa dauke hankalinshi daga Lailah, ya kasa daina jin  son taimaka mata. Ko ba da komai ba; da son gusar mata da wannan dimbin damuwar da take ciki ko ya ya ne, koda da fatar baki ne. He want to turn this sadness to joy…., he want to make

these tears- murmushi.

Jingine yake tuntuni a hanyar da ta raba first class seats da kujerun baya yana kallon ta, amma tsayuwar shi bai hana masu wucewa hanyar wucewa ba.
Ya duba lambar mazauninshi jikin tikitin hannun shi, ya mayar aljihun bayan wandonshi. Ya karaso inda take fuska cike da fara'a ya sake yi mata sallama a karo na biyu.
Kanta na fuskantar taga ne, tana kallon taurarin dake makale a sararin samaniyar subhana, ma'abota haske gami da hasken fitilun lantarki kala-kala da ya mamaye duhun daren, tana iya hangen gine-ginen gidaje, motoci da ma'aikatan birnin tarayya miri-miri kamar abebaden wasan yara, kamar a tafin hannunta.
Juyowa kawai ta yi fuska babu annuri, ba tare da nuna ya fuskanci halin da take ciki ba ya ce.
"Hello lady, can I've my seat here?"
Tare da nuna mata tikitinsa mai nuna cewa shine 'occupant'  na kujerar da ke manne da tata, wato mamallakin kujera ta (23).
Hannu kawai tasa ta dauke jakarta da ta dora a 'seat' din ta ajeta kasan kafafunta. Ta mai da kai inda take fuskanta tun farko, wato tagar jirgin, ba tare da ta ce da shi ci kanka ba......
"Taron tsinannu! Taron mugaye, taron mayaudara, macuta, maha'inta, 'yan tofin Allah tsine! Duk kune........ MAZA!!!"
Ta ce cikin zuciyarta. Tare da kai tausasan yatsunta ta yarfe wasu matsiyatan hawaye da suka kara shimfido mata.
"Iko sai Mai-Duka!"
Shi ma ya fadi cikin-cikinsa.
"Watakila bayan 'Psycho-disorder' Mamanta ko Babanta sun rasu, a wannan hutun da taje na 'summer'. Allah sarki! Gaskiya ba karamin rashi bane rasuwar iyaye. Karewa ma, it's the greatest loss of all losses! Shi zai gaya ma kowa ya ya rayuwar dan Adam take wakana babu iyaye? Ya ya dan Adam yake ji idan bashi da wanda zai zo ya rava, ya saki jiki da zuciya ya gaya mishi damuwar shi? Ya ya yake ji idan ba shi da mai daukar nauyin lalurorin rayuwarsa, har ya samu ya mike ya gina kansa?
Sai dai kuma Allah ya kawo mu wani zamani da (dutyn) Uwa ko Uba kawai shine su kawo ka duniyar, amma ko kai kadai za ka iya rayuwa, idan har ka san me rayuwar ke nufi, da inda ta sa gaba.
Sai ka fuskance ta a yadda ta zo, ka manta da komi, ka kasance mai binsu da addu'a.

Aka ba da shelar a daura 'belt' jirgi zai nausa. Kowa ya daura ban da Lailah. Sarkin sa-idon nata ya kuma cewa a ransa.
"To ko dai ba ta ji ne?
Amma kuwa a ganinsa da hakan bai sa ta kuka ba!.
Sai me don Allah ya rage ka ta wani fannin?
Ai dole ba zai hada maka komi 100% ba. Dole idan ya baka wannan ya hana maka wancan don ya jarrabi imaninka ya ga cewa, za ka gode da ni'imomin da yai maka ne ko a'ah?
Za ka butulce ta hanyar kuntatawa kanka? Idan ka gode sai ya karo maka da wata falalar daban ta inda baka zata ba.
Don haka a ganina in nine ke 'yammata ba zan yi kuka ba. A hakan zan daddage in jure in

fuskanci rayuwa. In shiga al'amuran duniya a dama dani domin babu maraya sai raggo. In kasance mai godewa Ubangijina (Yawaita Hamdala) wannan ba shine karshen rayuwar ba!! Kuma babu cutar da Allah ya saukar 'yammata ba tare da ya saukar da ita tare da maganinta ba, sai tsufa, sai mutuwa.
Sai in ci gaba da neman waraka. Sai dai hakan ba yana nufin zan dakatar da al'amuran ci gaban rayuwata bane, a'ah, ci gaba zan yi, har zuwa sanda (Arrahmanu) Sarkin Rahma ya ga damar yaye mini. Idan kuma ya fi son ganina a hakan? Ow.k! All it takes….!!!".
Shi kadai yake ta sake-sakensa, har da su watsa hannuwa gami da yarfar dasu tamkar wani zautacce sabon kamu.
Haka ita ma ba ta fasa kukanta ba, ba ta kuma da alamun dainawa. Sassanyan sautin kukan na kara ratsa kunnuwansa, tare da yamutsa tunaninsa a kanta. Yana kara raunana raunanniyar zuciyarsa, musamman kasancewarsa mutum mai matukar rauni a kan tausayin MACE.
Zuciyarshi ta gama lugwigwita, domin tun da yake bai tava jin irin wannan kukan ba, mai girgiza zuciya, mai ratsa kashi da vargo. Tsigar jikinshi ya soma tashi, bai san sanda ya rintse ido ba ya ce.
"Na hadaki da Allah kanwata ki daina wannan kukan!"
Da sauri ta cira kai ta dube shi da jajayen idanunta da suka rine kamar gauta. Yana son yin shisshigi a kan al'amarinta......
"Haka kuke da farko,… nuna tausayi da kulawa, har sai mace ta yi kuskuren fadawa a tarkon ku, sai ku cuce ta ku raba ta da farin cikinta……"
"Kuka na dinga yinshi kenan…. har karshen rayuwata!".
Magana take a zucci, ba ta san har ta suvuto ta fatar baki ta shiga kunnensa ba. Murmushi ya yi kamar bai ji abin da ta ce din ba.
Ya ce, " ki daura 'belt' din ki". Ba musu ta jawo ta makala a kugunta. Don kada ya sake damun ta da magana, ta sake mai da kanta cikin cinyoyinta.
Ya dauki 'earpiece' da aka ajiye a kowacce kujera ya manna ma kunnen shi, tare da murdo rediyon BBC harshen Hausa yana sauraro. Sai dai a zahiri ya yi hakan ne domin kare kunnuwansa da raunanniyar zuciyarshi daga sautin kukanta, mai lugwigwita zuciyarsa da kassara gavvan jikinsa. He donno why her cry weakens him…..(bai san meyasa kukanta yake raunana zuciyar shi ba). Mai raguwar zuciya ba zai iya daurewa ba sai ya tayata, and he don want 2 be among….. !(baya so hakan ta faru dashi). Jirgi ya mike sosai bayan ya gama ruguginsa mai gigitarwa, ya soma keta hazo ya naushi kasar Birtaniya.

Sai da ya kama hanya sosai ya zare 'earpiece' din tare da daukar karamin bargon 'British-Air' ya warware ya rufe jikinsa, daga kafadu zuwa cinyoyi saboda wani irin sanyi da ya soma keta vargon jikinsa. Wanda inda sabo to sun saba.
To haka da yawan al'ummar jirgin suka yi, aka yi light-up wasu suka soma barci. Wannan ma duka ban da Lailah.
Ya mika hannu aljihun bayan kujerar da ke gabansa ya dauki mujallar (TNT) ya soma buda shafukanta, ba don komi ba sai don kawar da hankalinshi daga kan wadda ba ta damu da shi ba, bare al'amarin sa.
Ba ta damu da kowa ba, ba ta san me yake yi ba. She's undoubtedly suffering a zuci, ruhi, fuska da gangar jiki, da al'amarin da duk tunanin mai tunani ba zai tava bashi ba.

A fuska she looks innocent…. A kwayar idanunta tsoro ne karara….. A shimfide kan fuskarta nadama ce tsantsa….. A karance kan siraran levvanta istigfari ne. Zuba suke tarara daga cikin idanunta, hawaye ne.
Baya iya banbance rubutun da hotonan da ke cikin mujallar, baya ganin komi a kansu face kyakkyawar fuskar Lailah, tare da sauraron zazzakan sautin kukanta.
'Yammatan jirgi zuka-zuka, farare kal cikin vingil-vingil din (minis) da rufaffen takalmi, bakaken 'suit' da shudin 'tie'.
"Looking so cool..........."
Ya fada ta hanyar motsi da tausasan levvansa. Sai dai kuma duk gyaran ku da kwalliyar ku you are not as good looking as she is,  (baku kaita kyan gani ba) duk da ita ba ta yi kwalliyar ba. Karewa ma hawaye ne sharkaf, jave-jave a idanunta. Haka ba ta nuna kowacce gava ta jikinta ba, in ka dauke shatin fuskarta.
Sai dai kana iya hango kwantaccen gashi baki wuluk mai sheki da walkiya daga saman goshinta, sakamakon mayafinta da ya dan zame baya cikin rashin saninta. Wanda ke nuni da ba bafullatana ba ce.
Wannan kyan ya kere na fulfulde, kyau ne da launin mutane biyu ya haifar, wato baki da fari (half - caste) da aka fi sani da ruwa biyu, daga uwa da uba.
'Yammatan suka iso layin da suke tare da dan tebirin su mai tayoyi (troller) mai dauke da duk wani nau'i na ababen jika makoshi, tun daga kan shayi, wine (giya), coffee, ruwa, jus da kwalayen taba nau'i-nau'i.
Cike da ni'imtaccen murmushinsu suke tambayar Lailah da ke kife da kai abin da take so.
Ko kallon su ba ta yi ba. Dan sa-idon nata, tuni ya ari bakinta ya ci mata albasa, ya ce a bata ruwa mai sanyi ta jika makoshinta.
Daya daga cikinsu ta ce,
"Hala amarya ce? Honey moon in the heart of England?"
Murmushi Abbas ya yi.
"Yap....... but we 've  a little misunderstanding (mun samu 'yar kankanuwar rashin fahimta) shine take fushi, irin na mata da miji, kin gane?"
Ta yi murmushi ita da abokin tafiyarta ta ce.
"Wannan ba wani abu bane, abu ne da ke faruwa a cikin SOYAYYAH. Idan babu irin wannan babu ingantacciyar soyayyar a zuci. Cool down my friend……".
Ta fadi tana mai dafa kafadun Lailah. Har da dan jijjigata.
Mamaki da haushi ne suka kashe mata baki ta kasa cewa uffan har suka wuce, bayan sun cika mata dan kofin su da ruwan abarba mai sanyi.
"Kulawa ma yabawa ce".
In ji Malam Bahaushe. Idan Abbas na tunanin irin shisshiginsa zai yi tasiri ya samu kulawar Lailah, wadda ke kallon dukkan maza  'naked' (tsirara) babu sauran mutunci babu sauran aminci da su a idanun ta ya yi kuskure. Har suka sauka a Heathrow  ba irin shisshigin da bai mata ba, amma uffan ba ta ce mishi ba. Hakanan bata kalleshi ba.
Da yawan ma'aikatan jirgin sun yi zaton da gasken mata da miji ne duk da yadda fuskarta da ma zuciyarta suke a jagule.
Don da za su fita jirgin ma'aikatan na ta yi musu fatan alkhairin 'honey moon' ne cikin kasar su (kamar yadda ya ce) yana amsawa a dokance. Yana binta kamar jela, kamar wani 'body guard' ,

ko ko mai take mata baya, da kula da al’amarinta.
Duk wannan na faruwa ne cikin Air-port din ‘Heathrow’ cikin dakikan da basu fice mintuna talatin ba.
Da suka zo kanta wato wajen tuhumar ingancin visa na karshe ga wadanda ba ‘yan kasa ba, wanda daga shi sai shigewa cikin garin London. Ya fahimci Lailah ba ta tava shigowa Ingila ba, domin daga ganinta ta fara tsorata daga tsabar binciken da ake yi mata, har ta zamo perpleded (rudaddiya).Ya ce sai ta tsallake wannan ‘inter-view’ din tukun shine na karshe. Tare da gaya mata cewa ta kula sosai wajen basu amsoshin tambayoyin duk da suka yi mata, ban da dadi ban da ragi, domin hakan na iya janyowa a hanata shiga.
Hankalin Lailah ya kai kololuwar tashi, idan da abin da yake na karshe da ba ta son ji a wannan lokacin, to komawa gida Najeriya ne. A dai wannan lokacin da ba ta san matsayin rayuwarta ba. Ta zo ne domin yin karatun da za ta yi wa kanta hukuncin da addini ya tanadar a kanta.
To amma why a Britain?
[12/17/2019, 17:50] Takori: Idan ilimin addinin musulunci ne ai yana kasar musulunci. Wannan kuma yana daga cikin dalilanta na son vatar da hankalin kowa nata daga tunanin inda take. Ta san nan ne kadai waje na karshe da iyayenta da shi kansa ba za su tava tunanin za ta zo ba, tunda ba ta tava zuwa ba. Kuma bata da kowa.
Sai dalilinta na biyu shine, tana da masaniyar cewa babu kasar turan da ke zaune da al’ummar musulmi lafiya irin Ingila. Kasa ce da ta bai wa kowa dake cikinta ‘yancin yin addininsa da walwalarsa, ba tsana ba tsangwama, idan har ka bi ka’idojin da ta shimfida maka. Wannan shine babban dalilin ta na zavar kasar Ingila a matsayin mafaka ga ruvavviyar rayuwarta.

Lailah ce tsaye can gefe a kanta tare da (UK Boarder Agency) masu binciken ingancin bisarta na karshe kamin su barta ta wuce. Tana amsa tambayoyi na karshe. A nutse take tsaf, cikin kamalarta da voye vacin ranta, tana mai amsa dukkan tambayoyin da a kai mata daki-daki da tsaftataccen turanci mara amo. Sun gamsu, sun yarda da zamanta cikin kasarsu baya nufin ha’inci ko vad-da-kama, ko kuma ci - da - gumin - wani. Saima su da za su kara bunkasa tattalin arzikinsu daga asusunta wanda ke cike taf da (sterling pounds).
To nan suka fi kauri, don haka suka daga mata kafa ta wuce. Ta fesar da ajiyar zuciya mai nauyi, domin ta riga ta tsorata da tambayoyin ka-ka uwar ki ta haife ki da suke antayo mata.
Ta yi tunanin idan aka ce ta koma gida a yanzu ina za ta dosa? Ba ta fata, sai ta yi wa kanta ilimin da zai tallafi gurvatacciyar rayuwarta.
Already shi har ya dau jakarshi. Ta dan yi mintuna kamin tata ta iso ta dauka. Suka jero gwanin ban sha’awa kamar mata da mijin gaske zuwa bakin titi.
Hadaddun Jeep-Jeep ‘yan gujif-gujif amma wai tadi ne (drop), su Laila ta fara yin tozali dasu a jere raras suna tsimayen mai hawa.
In kin san wani abu wai shi dacewa, wato (matching) na karshe, to Lailah da abokin tafiyarta ne, wanda har zuwa wannan lokacin ba ta yi mishi wani kyakkyawan kallo ba balle ta tantance kamanninsa.
Shi kuma haka nan ya bi ya nace ya manne kamar wani tsohon maye yana bibiyarta kamar bindi. Ba tare da damuwa da halin ko in kulan da take nuna masa ba.
Ya lura ba ta cikin cikakkiyar nutsuwa, haka nan ba ta san ko ‘ina ba. Sai dai kuma ba ta da duhun kai, don ba ta tambayi kowa ba. Ta san iliminta zai mata jagora a ko’ina.

Ta karanta adireshin makarantar da ta zo, (20 Creffield, Earling, London), ta maida takardun inda ta dauko su a jakarta, ta nufi daya daga cikin tasin.
Tun kan ta karasa wani dan motsattsen Bature ya iso gare ta ya amshi jakarta yana kokarin sanyawa a boot.
Hannuwanshi biyu ya sanya ya ciro jakar daga boot din tasin, ya ja Baturen gefe yana murmushi ya ce da shi cikin harshensa.
"Kyale ta fushi take, ka san amare abu kadan sai su hau, su yi fam!"
Baturen ya kyalkyale da dariya ya ce, "To ai kai ma abokina amare lallava su akeyi".
Ya ce, "Ina lallava ta tana kara hawa sai ka ce alkubus, ka gane rigima ce da Madam, ta fi son mu sauka a DUNDEE ni kuma na fi son London. Shin akwai inda ya kai London dadin 'honey moon' ne a Birtaniya?"
Da sauri Baturen ya girgiza kai ya ce, "A'ah, garin sarauniya ai babu kamar shi a duk fadin Ingila".
Ya juyo ga Lailah yana murmushi wadda tuni ta yi mutuwar tsaye.
"To kin ji sai ki daina fushi, ki daura aniyar zaman London da kin ki da kin so. Ina da 'oyster' (katin hawa jirgin kasa) har biyu, zan baki guda. Gara mu bi 'train' yafi saukin kudi.Wuce muje Ma sis.........."
Wannan karon da Hausa yake magana don kada mai tasi ya fahimce shi. Ya zaro fam ishirin cikin wallet dinshi ya mika ma mai tasi, amma ya ki amsa, su kai sallama ya yi gaba.
Ba ta da zavi ban da ta bi shi, domin da jakarta da nashi ya hada ya wuce.
Ba ta tava ganin mutum mai shisshigi irin wannan ba. Haka ba ta tava ganin mutum mara zuciya irin shi ba.
"Uffan ban ce maka ba, kallo  wannan baka ishe ni ba. Amma 'still' baka fasa naci ba".
Ta furta cikin takaici, tare da jan wani matsiyacin tsaki, "Tsuuut!"
Ya ji sautin tsakinta, amma bai san ko me ya sata yin tsakin ba. Ya murmusa har cikin ransa ya ce.
"haka nake kiyi hakuri dani, naci akan abinda na kwallafawa rai, nake kuma son sani. Wanda akafi sani da 'curiosity'. Am curious about you! Yanzu meke damunki? Yunwa ko gajiya?
Kada ki damu, I'll cook deliciously for you........ (zan miki girki mai dadi, ni gwani ne wajen girki, lokacinda matata ke raye).

A mamakance  Lailah ta cira kai ta dube shi, wannan karon cikin ido. Ta tsorata, ta mamakantu, haka ta firgita da abin da ta gani cikin kwayar idanunsa (Mohammed sak!).
Amma hakan bai kada ta ba kamar zallar kyau da haiba irin na wannan mai naci. Duk da cewa baki ne amma bakin shi mai kyau ne. Ta ko'ina ba ta inda Ubangiji ya rage sa.
Ba ta san yaushe murmushi ya suvuto daga bakinta ba. Karo na farko da ya ji sautin muryarta ba cikin kuka ba.
Ya lumshe ido yana bude su dukka a kanta, sun kada sun yi jawur. Wannan karon sautinshi ya yi kasa very cool! Ga dukkan alamu tunanin mutuwar matar ya tava zuciyarshi.
A hankali ta ce, "I'm sorry".
Ya ce, "Na gode".
A marairaice ya ce, "Ki yi hakuri ki karve ni LAILAH". (Ya ga sunan ne a jikin passport dinta). Ko da a matsayin abokin tafiya ne, bana nufin komai dake sai alheri Lailah. Lailah ina so na

taimaka miki ne, ta wani fannin in taimaki kaina. Kin amince dani Lailah?"
Ta karaya, amma bata son nuna karayar tata a kan MAZA. Tana da tabon su, tana da danyen mikin su cikin ranta, tana da mummunan kullaci a kan al'amarin su;
Sune suka rabo ta da iyayenta da basa hada kaunarta da ta kowa. Sune suka rabo ta da mijinta da aurenta. Sune suka rabo ta da 'yan uwanta da aminanta...... Sune.....sune.....sune suka yi wa zuciyarta gyambo da har abada ba zai warke ba.
Sune suka yi mata miki mai rudani, suka sanyata cikin rudanin rashin sanin sahihanci da ingancin addininta......
In haka ne ita wace irin wawuya ce da za ta amince ta sake fadawa a tarkon su haka 'so early?' (da wurwuri?)
Ta girgiza kai ta furta mishi da karfi, "Never! (Fau-fau). Babu ni babu Da Namiji!".

Ya yi saurin juyowa idanunshi sun kada sun yi jawur, yana son tantance sanadin wannan ANGER (fushin) da ke cikin muryarta.
"Why Lailah (me ya sa)?" Ya bukata.
"Ai ba duka muka taru muka zama daya ba. Kowa sunan shi yake amsawa. Kada kiyi mana jimilla a rashin kirkin, wannan rashin adalci ne!".
Ta soma kokarin kwatar jakarta tana magana, wannan karon cikin kuka.
"Am not your wife (ni ba matarka ba ce), so why the disturbance?  (meye dalilin wannan takurawar?)
Ka kyale ni in yi tafiyata, ka kama hanyarka in kama tawa, ka yi wa Allah ka rabu dani........"
Kuka ya ci karfinta.
Karfinta ya kare domin ta kasa kwatar jakar. Karfin mace, da karfin namiji. Balle zabgegen mutun irin ABBAS. Wadanda irin su tsiraru ne a cikin al'ummah.
Sai ta tsuguna a nan kan kafafunta ta sa mishi kuka mai gigitarwa, tana rokon shi Allah da Manzon shi ya ba ta jakarta ya yi tafiyarsa ya kyale ta.
Shi ma sulalewa ya yi nan a gabanta a kan gwiwoyinsa idanunshi a rikide, amma ba kukan yake ba.
Numfashinshi ke gwagwarmaya da sauri da sauri. Ji yake in duk duniyar nan za ta taru a kansa ba za ta raba shi da Lailah ba!.
"Hanya mai hadin zumuntar dole….", in ji 'yan Magana. Lailah ta gamu da gamonta. Ta ci kukanta ta koshi, ta tabbatar ba zai rabu da ita ba sai dai su kwana a nan. Ta yi tunanin hada shi da 'yan sanda kawai su yi masu katangar karfe. Daga baya wata zuciyar ta ce da ita, "A kul, shi din kin san wane ne?" Bai yi kama da irin mazan da mace za ta wulakanta ta kwan lafiya ba, bai yi kama da wulakantaccen mutum ba. Haka bai yi kama da wadanda 'yan sanda za su girgiza ba, tun da kasa ce da kowa ke da 'yancin kansa.
Ba ta da zavi ban da dangana, ta yi gaba tana huci ya bi ta a baya yana murmushin cin nasara. Suka gangara ta liftar kasa zuwa 'Rail-Station' na Heathrow, suka yi amfani da katunan Abbas na hawa jirgin kasa suka hau jirgi mai zuwa cikin 'Central-London'.

***

12/SAFAR HIJIRIYYAH
Cikin jerin gwanon masu saukowa daga matattakalar jirgin 'Royal Air Moroc' har da Engineer Mohammed Bauchi, fari sol da shi bafulatanin Jama'are, ga dukkan alamu babu tambaya, cikin

caftan na ‘ash colour’ shadda mai taushi da walkiya. Agogon (RADO) baki sai sheki yake cikin tattausar fatar hannunshi da bakin lallausar gashi ya baibaye.
A very serious person (wanda babu alamun wasa cikin al’amarinsa), wato irin mutanen nan masu wuyar sha’ani da rashin walwala. Sai dai fa in ka san wata kalma wai ita ‘aji’ na karshe, to Mohd. ya mallaki dukkanninta.
Dan kimanin shekaru 35, Mohammed, yana da tsayi sosai da lange-langen jiki na fulanin usli, wadanda suka jiku suka zurfafa suka gogu cikin ilimin addini da na boko.
Ga wanda duk ya san Mohammed Jama’are, ya  san shi da wannan halayyan nashi na (seriousness), watau daukar abinda ke gabanshi da muhimmanci a kan komi. Babu abin da yake bai ma lokaci kamar aikinsa da abubuwan da ke gaban shi, na ci gaban rayuwar shi.

Tun kan ya idasa saukowa daga matattakalar ya zura hannu cikin aljihun kaftaninshi ya fiddo wayarshi ya kunna, yana kiran kanin shi Sa’idu ya zo ya tarbe shi.
“Big Bro. isowa haka unexpected?”
Ya fada cikin kasalalliyar murya.
“Da tun jiya ka sanar damu, yanzu haka ina cikin Jama’are, Inna ba ta jin dadi”.
“Ow.k, ba matsala, bari in kira Lailah, ai tana gida ko……?”
Shuuuu...... ‘network’ ya katse, don haka bai ji amsar Sa’id ba.
Ya lalubo lambar ya kira, sunan ‘eclairs’ ya soma yawo a ‘screen’ din. Ta yi kara har ta gaji babu agaji.
A karo na biyu ya sake kira. Wannan karon ma ta yi ta vurarinta har ta gaji, ‘eclairs’ ba ta agaza mata ba.
Cike da kosawa ya sake kira a karo na uku, ta yi har ta gaji ta tsinke don kanta. A  serious person, abinki da dama ya ya lafiyar giwa? Nan da nan ya kufula, gaba daya ya kashe wayar don haushi, ya figo jakarshi zuwa harabar ‘air-port’ ya samu achava ya dane, mai machine ya rike jaka a gabansa, bai tambayi ba’asi ba ya figi babur, ga dukkan alamu wannan oga a kule yake, don haka bai tambayi inda za a ba sai da ya mula don kansa ya fada mishi.

Gidan na daga jerin farko-farko na gidajen unguwar (Fati Mu’azu Links) cikin Bauchin Yakubu, gida ne ‘flat’ karami hawa daya ma’abocin wadatar shuke-shuken furanni masu launi daban-daban da kamshi daban - daban.       Karamin gida ne da ya kunshi duk wasu nau’o’in abebaden jin dadin rayuwa cikin tsari da sanin ciwon naira.
Abin nufi, babu almubazzaranci, babu fariya, haka babu son nuna isa. Komi ka gani cikin gidan mai amfani ne, haka ba a yi dakuna rankatakaf ba adadi ba.
Kwata-kwata dakuna ciki uku ne da makeken falo, sai (boys quater) daga waje da (study room) mai kunshe da littattafan  da suka  shafi mazauna gidan.
Maigadi ya saki baki bude, ganin maigidansa na sauka daga kan dan achava da jakar kayansa. Ya ciro kudi ba tare da ya kirga ba ya mika mishi ya wuce yana godiya.
Malam Surajo bafullatanin garin Dambam ta jihar Bauchi, kuma amintaccen maigadin maigidan, ya karvi jakar uban gidansa ya yi ciki da ita ba tare da ya jira ubangidan ya gama kiraye-kirayen wayar da yake yi ba.
Ya yi matukar mamakin ganin motar matar gidan na nan. Rufe cikin tamfol, sai dai ga dukkan alamu an jima ba a yi amfani da ita ba, sakamakon kura da ta yi futuk ita da tamfol din.

Motoci uku ne dama a ma'adanar gasunan. Wanda ke nufi tana cikin gidan, tana ganin kiran wayarshi amma don iya shege irin nata ta ki amsawa da gangan.
Ya yi kwafa kana ya tura kai cikin gidan. Ko'ina a bude, ba a sanya makulli ko daya ba.
Sai dai fa ko'ina futuk yake da kura kamar babu halittar dan Adam a gidan. Tuni Malam Surajo ya aje jaka ya fice domin da alama ogan na cikin masifan nashi da ya saba.
Yana tsoron kada bai kar zomo ba a ba shi rataya, don haka ya yi hanzarin daukar buta ya zaga bayi domin gabatar da alwalar sallar azuhur.
Niyyarshi yau sai Allah kadai zai saukar da shi daga fushin shi, duk dadin bakin nan nata…, duk kissa da kisisinar nan nata….., duk lailaya da rarrashin nan nata……, duk taushin hannuwan nan nata........da tausasan levvan nan nata, masu mantar da da namiji duk wani jin kai, takama da mukaminsa. Yau sun yi kadan su sauke fushin takwaran Manzo.
To amma fa ko wajen zama bai gani ba a dai wadannan fututuk din 'leather' din masu kama da an yi wata ba a hau ba.
Babu motsin kowa, babu motsin komi balle 'yan wake-waken nan nata na zabiya 'Nancy Agram' idan tana 'yan girke-girke da kaye-kayenta cikin kitchin.
Jikinsa ya soma yin la'asar. Kai tsaye ya fada kitchin babu ita, ya banka dakin barcin su.... a nan ne idanuwanshi suka gano mai abin al'ajabi.
Kafatanin kayanta da ke cikin ma'adanar kaya gasu nan baza-baza a kan gado. Ga alama an kwashe wasu ne an bar wasu. Ya yi kira da murya mai karfi....
"LAILAH!"
Kiran ya dauki amon da ya karade ilahirin gidan. Ya sake bude iyakar muryar da Allah ya halitta masa.
"LAILAHHH! LAILAHHH!!!"
Shi kansa sai da amsa kuwwar ta hargitsa cikin kwanyarsa.
Davas! Ya sulale ya zauna da mazaunansa bisa carpet.
"Me ke faruwa ne? Ina ta tafi? Babu sallama balle neman izini? Wannan ba halayyarta ba ne, ba ta tava ba, ba ta da kowa a nan sai shi, sai iyayenshi da ke kauye wajen wa za ta je?"
A sukwane ya kara zaro waya ya kira dan'uwansa. Ta yi ruri har ta gaji, ta yi gunji ta yi vurari mamallakinta ya ki dagawa. Da ya sake kokarin kira a karo na biyar, mai abar ya kashe ta gaba daya.
Cike da mahaukacin mamaki ya tattara hankali da kuzarinshi wuri guda, ya mike tare da zuwa ga lokar gado ya dauko makullan motar sa.
Sai a lokacin tunanin Malam Surajo ya fado mishi. Da sassarfa ya fito ya nufi dakinsa, ya idar da sallar azuhur kenan bai kai ga mikewa daga sallayar sa ba.
Ya tsaya daga bakin kofa ya tokare cike da jarumtakar voye tashin hankalinsa da gigicewar sa.
"Malam Surajo ina matar gidan nan ne? Ko'ina a bude, kuma a hargitse. Kuma kura futuk, anya lafiya?"
Malam Surajo ya jinjina kai ya dubi ubangidansa a nutse ya ce.

"Yammacin ranar ta yi min alheri mai yawa, irin wanda ba ta tava yi min ba.
Ta ce, "Watakila Surajo wannan ita ce haduwar mu ta karshe. Na yi tafiya Surajo sai wata rana".
Ta dauko damin kudi ta bani, ta kuma bani wannan 'yar takarda ta ce in baka".

Tamkar wanda kwai ya fashewa a ciki, da kyar ya mika hannun daman shi Malam Surajo ya daga buzun sallarshi ya ba shi takarda nannade cikin ambulan.
Daga inda yake tsaye ya warware takardar idanunshi na ganinta dusu-dusu.

Mohammed Dina…..!
Na yi tunani iyaka tunani, bincike iya bincike, na kasa gano tsakanin ni da kai WANE NE MAI LAIFI?
Da na kasa ganowa sai na bai wa Allah zavi. A daren ne kuma na yardar ma kaina cewa rabuwar mu ita ce mafi ALHERI.
Domin ba za ka tava yafe min ba......nima kuma ba zan tava yafewa kaina ba.
Idan na yi wa kaina hukuncin da ya rataya ga kuskurena, watakila wata rana mu gana.
Ina rokonka idan ka kuma yin wani auren, Mohammed dina....ka yi kokari kada ka maimaita kurakuranka.....ka rage 'seriousness' din nan naka…. ka bai wa matarka kulawa da dukkan kaunar da take bukata daga gare ka......
-LAILAH BALLAH!

Kanshi ya daure tam, ya yi zafi rau. Ya kai yatsa baki ya ciza da karfi wai ko barci yake ya farka. Ya tabbatar idon shi biyu.
A karo na biyu ya sake bin kyakkyawan rubutun Laila ya karance tsaf.
"Me na yi miki Lailah? Wane kuskure na yi miki haka da zafi da kika zavi bari na?"
"Ka manta ne? Sarkin tsokanar? Ta saba 'trick' kala-kala, yanzu haka tsokana ce kawai take yi ba za ta wuce wurin mahaifiyarta ba".
Wani dan guntun sako daga zuciyarshi ya tunasar da shi.
Don haka cike da kwarin gwiwa ya linke takardar ya jefa a aljihu, ya bar dakin Malam Surajo yana tafe yana kiraye-kirayen waya domin nemawa kanshi tikitin zuwa Alkahira komi dare.
[12/17/2019, 17:50] Takori: ***
Tarba  ta musamman Momi Najla ta shiryawa surukinta cikin babban birnin Alkahira. Tun da ya yo waya cewa ga shi nan a filin jirgi a zo a tarve shi, ita da kanta da kannen Laila biyu Sanah da Najat da kuma babbabn Yayansu Isma'il suka zo taren shi. Isma'il na tuka motar. Autarsu Najat ta zo da gudu ta rungume shi da ta hango shi yana nufo su tana tambayar shi.
"Uncle Pilot za ka tuka ni a jirgi? Uncle Pilot AINA UKHT LAILAHHH?"
Hankalinshi in ya yi dubu to ya tashi, tsigar jikinshi ya mike, ya kidime ya razane. Wannan na nufin, Lailah ba ta wurin su.
Da wane ido zai dubi Momi Najla da ta danka mai amanar rayuwar marainiyar diyarta?
Gwiwoyi a sage, gavovi a kassare, ya zube a gaban Momi ya kasa ko gaishe ta. Isma'il ya kama kafadunsa ya mikar dashi, sai ya fashe musu da kuka.
Kan ka ce meye wannan Najat ta shiga taya shi, saboda tsabar haduwar jinin su, yana matukar son yarinyar ita ma tana matukar son shi. Ba don komi ba si don kwadayin ya tukata a jirgin sama, wanda shi ne babban burin rayuwarta.
Momi ta matso gabanshi a hankali, jikinta a sanyaye ainun.
"Haba Mohammad, kada ka yi min haka. Me ya faru da Lailah? Wannan ba girmanka bane......."
Isma'il ya kama kafadunshi, "Abokina Lailah rasuwa ta yi? Ka gaya mana ai mu musulmi ne, dukkaninmu sane muke da cewa ko ba dade ko ba jima rai zai koma ga Ubangijinsa!".

Ya girgiza kai, amma ya kasa magana. A karo na biyu Momi ta ce.
“Mohd. idan Laila mutuwa ta yi kwananta ne ya kare..........!”
Ya yi hanzarin tura hannu aljihu ya zaro takardar Laila cikin ambulan ya mika ma Isma’il, don baya son wannan kalma ta mutuwa da suke ambatawa Lailansa.
A nutse Isma’il yake karanto ma Momi wasikar Lailah, har ya dasa aya. Dukkaninsu suka yi zuru! Abin tausayi, ba ma ya Mohd. wanda yake jin kansa a victim na duk abin da ya samu diyarsu.
Kanshi ya yi zafi zau da tunanin wane kuskure ya aikatawa Lailah da har ta zavi barinsa? Abin da ko a mafarki bai tava kawowa ba.
Bai tava tunanin dai-dai da rana daya Laila za ta iya rabuwa da shi ba, saboda tubalan da suka gina soyayyar aurensu ba tubala ne da ake amfani dasu wurin yin aure a wannan zamanin ba......
Shi kuwa Isma’il dage kai sama kawai ya yi bai san me yake tunani ba.

***

Wani abin mamaki shine, Lailah da abokin tafiyarta duk makaranta daya suka zo, wato ‘Muslim College, London’.
A tsarin makarantar basa ba da accommodation wato muhalli da abinci, don haka bayan sun gama da registrer din makarantar (Aaliya Arnall), kai tsaye cikin gari suka fito. Suka yi ‘yan tsince-tsincen dan abin da za su ci, amma basu shiga ‘restaurant’ ba. ‘SAM CHICKEN, chips, da gwangwanin ‘pepsi’ suka samu suka ci. Suka koma cikin makaranta inda aka hada su da wanda zai taimaika masu wajen neman muhalli.

Abbas ya zo neman kwalin shi na Ph.D ne yayin da Lailah ta zo neman kwalin masters. Duka a cikin makarantar ‘Muslim College’.
Babu jimawa suka samu gidan zama na haya na wasu mutanen ‘Lahore’ a (Acton Town), kusa da makaranta, don daga nan ko basu hau ‘bus’ ba zasu iya zuwa makarantar a kafa. Dakuna ciki dai-dai, shi yana a saman bene ita tana kasa.
Kuma a washegari suka fara daukar lectures, maimakon biyan kudin haya duk sati sun dunkule sun bai wa maigidan (Landlord) kudin shekara daya.
Sai ya zamanto wata irin shakuwa na shiga tsakanin Lailah da Abbas, shakuwa mara fasaltuwa. Sannan tsaftatacciya, domin kowanne yana ganin mutuncin dan uwansa. Kuma kowannensu ya san ciwon kansa.
Idan shi ya rigata dawowa zai dafa musu abinci, haka idan ita ta riga dawowa. Tare suke zuwa ‘shopping’, tare suke zuwa cefane, ‘café’ da sauran su, rayuwar su gwanin ban sha’awa kai ka ce Yaya da kanwar shi ne.
A cikin gidan ba su kadai bane, akwai mutanen India da wata mata ‘yar kasar Somalia. Idan Abbas shi ya yi abinci sai ya kwankwasa mata kofa ta bude ya mika mata, haka idan ita ce ta yi.

Duk kokarinta na ta yakice Abbas ta kasa, domin mutum ne har mutum, mai tausayi da kyautayi mai yawan gaske.
Lokutan daukar lakcarsu ba daya ba, don haka a kullum daya ke riga daya dawowa gida.
Wanda ya riga dawowa gida shi zai dafa abinci.

Rayuwar London mai cike da abubuwan debe kewa, zaman lafiya da kwanciyar hankali, sai ta taimaka ainun wajen rage ma Lailah dimbin damuwar da take ciki mai neman janyo mata 'psychological depression'.
A wajenta Abbas (kawa) ne, wato (aboki) kuma mutumin da za ta iya tutiya da shi matsayin wanda ya taka muhimmiyar rawa wajen rage mata dimbin damuwar nadamar rayuwar da take ciki.
A hutu na farko da suka samu bayan share watanni uku suna daukar darasi, Abbas ya same ta a dakin ta bayan ya nemi izinin shigowa.
Suka yi wa juna kyar da ido kamin su sakar ma juna dariya. Ya ja kujera ya zauna yana mai fuskantar ta.
"Ko zan samu dan rakiya?"
A sanyaye ta ce, "Zuwa ina?"
"Zuwa 'Lake-Windermerre' a Cumbria, picnick nake bukata Lailah. Kwakwalwata tayi zafi, karatu yayi yawa a cikinta so, ina son samun 'peace of mind' (hutu) koda na yini daya ne.".
Cike da murmushi ta aje littafin da take nazari ta ce.
"Bani minti ashirin na kintsa".
Ya fita ya ja mata kofar ya ce,
"Plz… hurry".

Ta jirgin kasa suka bi zuwa 'Cumbria,' kauye ne awa ashirin da hudu (24 hours) daga London.
Ga alama hakanshi zai cimma ruwa ya samu Laila ta bayyana mishi tarihin rayuwarta da ta voye ko zancen, ba ta so.
Domin a ganinta ta riga ta tsere, ta yi nisa da rayuwarta ta baya. Wannan karon ma suka hau jirgin kasa ta hanyar amfani da 'oyster' dinsu. Rataye da 'picnic bags' dinsu. Mai dauke da abinda zasu ci, da wanda zasu sha, 'camera' da sauran su.
Lailah sanye take da bakar 'coat' wadda ta zo har gwiwoyinta da bakin wandon 'channel'. Ta yane fuskarta da kankanin gyale daga 'pashmina'. Ta saje tsaf da turawan Ingila, ta yadda in ba fada maka aka yi ba ba za ka iya tsince ta daga cikin su ba.
Yayin da Abbas ke sanye da shudiyar suwaita long sleeve da bakin 'jeans' shima, kai da ganinsu ka ga 'students' zaunannun Birnin Sarauniya.

Zaune suke a bakin 'Lake' din kafafunsu duka cikin ruwan. Abbas ya dube ta da kammalalliyar fuska, ta samu kanta da jin wannan mutum kamar Yayanta Isma'il, zuciyarta ta amince da shi.
Ita kanta bata san dalili ba.
Ya ce, "Lailah is high time in ji abin da ya rabo ki da gida, ko zancen wani da ya shafe ki baki tava yi min ba. Jikina ya bani ba haka kawai cikin dadin rai kika zo karatu kasar nan ba.  Is this friendship?"
Ta ce, "Zan gaya maka Abbas, duk da cewa ban san karvar da za ka yi wa labarin ba".

****

FARKON LABARIN

Haduwata da Mohammed, a babban filin jirgin saman Egypt  ne (Cairo International  Air-port), za mu raka mahaifinmu zai tashi zuwa kasar Najeriya. Mahaifinmu dan uslin kasar Najeriya ne, dan Kano, amma mazaunin Egypt, tun daga zuwa karatu ya samu aiki saboda kyawun takardunsa. Likita ne kwararre a 'general hospital'. Ya yin da mahaifiyarmu ta kasance 'yar usulin kasar Egypt. Ya aure ta tun auren saurayi da budurwa.

'Patient' dinsa ce tana da 'ulcer', ya kasance duk wani 'treatment' dinta a hannunsa yake.

Suka gina ma zuciyoyinsu wata irin soyayya wadda daga iyayenta basu samu wata matsala ba, wai don kasancewar shi ba dan kasa ba.

Shi daman maraya ne ba uwa ba uba. Sai Baffanninshi biyu a Kano. Suka yi aurensu a nan Egypt ya sayi babban gida a can suke zaune cikin soyayya da amana.

Isma'il shine babban dansu, sai ni, sai 'yan biyun Momi Sanah da Najat. Mohammed matukin jirgin sama ne, wannan shine babbar matsalar da muka fara cin karo da ita a rayuwar aurenmu. Shi Mohammed dan asalin garin Bauchi ne, wani gari Jama'are. Su biyu kacal iyayensu suka haifa daga shi sai kanin shi Sa'eed.

Akwai  rata sosai ta shekaru goma tsakanin Mohammed da Sa'idu. A lokacin da aka haifi Sa'id, girma sosai ya cimma mahaifinsu Malam Yahya, wannan ne dalilin da ya sa Sa'eed ya dawo hannun mu da zama lokacin yana karatu a Tafawa Valewa University Bauchi.

Mohammed ya ware ma Sa'eed dakin zama a boys kuaters, ya fara karatunsa cikin nasara. Inda yake karantar 'Geography'. Wankan tarwada ne mai kyakkyawar sura, yana da kazar-kazar da fara'a mai yawa, yana da kirki da ladabi ga dan uwansa, da ni da nake matsayin matar Yayansa.

Kirkin Sa'id ne ya sa muka zamo wasu irin aminai, duk abin da ke damuna kafin Mohd ya sani na fadawa Sa'id.

A ganina shine mai lokacina, saboda mijin bana jin dadin sa. Mohammed, wani irin mutum ne tough, serious, ba shi da lokacin iyalinsa ayyukanshi na tuki suna gaba da komai.

Sai ya yi watanni uku yana yawo a duniya. Da fari na uzurce shi da cewa yanayin aiki ne, amma a matsayina na mace mai jini a jika wannan aikin na Mohd. na ci min tuwo a kwarya.

Farkon auren mu ya zamanto ba haka bane, don a lokacin yana fafutukar neman aiki ne muka gamu. Da ya samu aikin ne abubuwa suka sauya, don haka zuwan Sa'id gidan mu ba karamin farin ciki hakan ya haifar min ba.

Digirina na farko na yi shi ne daga jami'ar Al-Azhar a kan Falsafa (Philosophy). Ina matukar son mijina kwatankwacin yadda yake so na. Domin a kan soyayya da kauna muka gina auren, tun mahaifina yana raye. Mohammed ya dauki son duniya ya dora a kaina, sai dai kuma abin takaicin ba shi da lokacin da kowacce mace take bukata tare da maigidanta, yana hadawa kanshi zafi da yawa kamar shi kadai ne matukin jirgi a duniya.

Daga baya ne Sa'id ke yi min bayanin ai bayan Virgin Atlantic da yake wa aiki wasu kamfunan daga ko'ina irin su MEA, KLM, Royal Air Moroc, da sauransu suna daukar shi haya saboda kwarewar sa.

Amma a matsayina na matarshi abokiyar rayuwarshi bashi da lokacin da zai zauna ya yi min

wannan bayanin, sai dai kullum ya ce bana yi mishi uzuri da yawan ayyukan da ke gabansa.
Sa'eed ya dawo makaranta a wani yammacin Litinin ya same ni a kitchen, yai sallama ya shigo, ya karve ni a firar dankalin da nake yi.
Ya ce, "Gaskiya Aunty Lailah ya kamata a samo miki yarinya mai aiki mace kina wahala fa, ke kadai a gidan nan".
Na ce, "Da hakan za ta faru da na yi murna".
Ya ce, "On weekend, (cikin karshen sati) zan je Jama'are zan fadawa Hajiya za a samu insha Allah".
Na ce, "Na gode".
"Yaya bai yo waya ba? Ina so in mishi zancen kudin 'registration' ne. Kin san an ce shekarar kwana gashi har shekara ta zagayo za mu shiga level 300".
Na ce, "Har nawa ne?"
Ya ce, "Bai kai 20 thousand ba".
Don haka a daren ranar na kirgo kudin registration na ba shi cikin kudin da Mohammed ke bar min.
Ban rasa ci ba, ban rasa sha ba, ban rasa suttura ba, amma na rasa soyayya da kulawar mijina.
Sai Sa'id ya zamo wani mutum mai kula da ni da debe min kewa, ta hanyar irin wasannin nan na kanin miji da barkwanci ga matar Yaya.
Shakuwar mu da Sa'eed din har ta zarta misali, saboda yadda yake nuna min kulawarshi a kan al'amura na da damuwarshi a kaina.
Idan ka ganmu a kanti muna sayayya ko a kasuwar wunti muna cefane sai ka dauka mata da miji ne.
A satin muka shirya tafiya Jama'are ni da Sa'eed gaida Hajiyar Mohd. Hajiya ta rasa inda za ta sani don murna, ta kuma rike ni sai na kwanan mata biyu. Don ita kanta wannan yanayin aikin na Mohd. na damun ta, don dai ba yadda za ta yi ne.
Da daddare mun yi shirin kwanciya Hajiya ke yi min nasiha cikin hikima na in kara hakuri da yanayin aikin Mohd. Ita kanta ta damu, to amma yaya zamuyi? Tunda dai hanyar abincinshi kenan, kowa da inda Allah Ya tsaga mishi hanyar abincinsa.
A raina na ce, "In ban yi hakurin ba ya ya zan yi? Ya riga ya rabani da uwata da 'yan uwana, kuma ba shi da lokacina.
Idan dai don kudi ake wannan aikin babu samar ma kai da zuciya, kwakwalwa hadi da gangar jiki hutu, sai in ce ban san inda Mohammad zai kai kudin da yake samowa ba".
A kan hanyarmu ta dawowa Sa'eed ya dukufa lallashina, don ko fuskata mutum ya kalla ya san ina cikin matukar damuwa.
Yake ce min, "wata rana sai labari Aunty Lailah, ki kara hakuri a kan naki na da, shi Yaya da kanshi zai gane wata rana ba ya kyautawa, ya ragewa kanshi aiki ya rungumi iyalinshi, in kuma kin amince in yi mishi magana to, duk da yana daga cikin irin mutanen da da wuya ka doshe su da irin hakan".
Ban ce komi ba, abin da na sani shine, auren Mohammed ya fice mini a rai, burina tunda ba shi da lokacina, to ya sallame ni in koma cikin 'yan uwana gaban mahaifiyata, duk da bai tava iyakance min zuwa ganin su ba.
Shakuwar mu da Sa'eed sai abin ya kara gaba. Ya zamanto girki ma wannan tare muke yin sa, kallon kwallon kafa da daddare duk tare muke yi, kamar wasu mata da miji.

Har na kan kissima a raina wani lokacin ni kam da ma Sa'eed aka aura min da na more. Duk da yake yaro dan shekaru ashirin da bakwai ya sn yadda zai yi ya tafiyar da mace da nuna mata abin da ta fi so a gidan aure, wato soyayya da kulawa.
Za ka so ganin mu muna kallon ball har da tafawa, saboda shi dan 'Arsenal' ne ni 'yar 'Real Madrid', mu takarkare mu yi ta musu kowa yana kare kungiyar sa.
Mu yi girke-girke mu ci, a karshen mako mu yi 'sanitary' mu gyare ko'ina na gidan mu.

Yana da yawan zama a 'study', musamman lokacin jarrabawa ba ya wasa. Yaro ne haziki mai kirkin gaske da saurin shiga rai.
A satin da su Sa'eed suka fara zangon karatunsu na farko a level 300, Mohd ya iso, kai ka ce ba mijina ba, ban yi wani doki ba balle in yi wasu shirye-shirye domin tarbarsa.
To shima din bai damu ba, don ya san shi din har kullum mai laifi ne a gare ni, bayan a ganin sa yana sauke duk wasu nauyi da Allah ya dora masa a kaina idan ya zo bayan kowanne watanni ukku.
Ya rage nawa in dubi yanayin aikinsa inyi mishi uzuri ko kar in yi, don shi kan ga yadda ya nuna ya gaji da kananan korafe-korafen da nake damun shi dasu a kan rashin sa cikin gidan, tun da dai ba dauka na zai yi ya goya ya dinga yawo dani cikin duniya ba. Bai kuma iyakance min zuwa ga 'yan uwana a duk sanda na so ba.
To amma mene ne auren? Ina da tambaya, 'yan uwana mata. Shin wannan shine ginshikin auren ko me? Ba na samun ginshikin aure, don haka am not satisfied with my husband.
Don haka Mohammed har ya gama kwanakin shi biyu ya koma bai samu wani edcellent welcome  daga gare ni ba, kamar yadda shi ma ya ke complaining(korafin) na hana shi hutawa, na dauki vacin ran banza da wofi na daurawa kaina.
Idan bai fita ya nemo min ba me zai ba ni? Ko nufina shine ya jive a gida kada ya yi amfani da damar da Allah ya ba shi na morar iliminsa? Mutane nawa ne suke neman 'chances' din (damar) da yake samu basu samu ba?"
"Su 'chances' ba a hakura da wasu don a huta, a kula da bukata da rayuwar iyali?" Na tambayeshi watarana.
Ya ce,
"Lailah you'll never understand me, (bazaki tava fahimtata ba), tunda kin riga kin damu kanki. Na gane ki, irin matan nan ne da suke so miji ya like musu kamar kaska, kin san da irin aikina kika aure ni, a kan me yanzu za ki uzzure ni?"

Don haka har ya koma bamu yi rabuwar arziki ba.

Ta duba agogon hannunta kana ta dubi Abbas.
"Ya kamata mu tafi gida haka yamma ta yi sosai".
Abbas ya zare kafafunshi daga cikin ruwan suka mike suna harhada kayansu.
Ya ce, "Ni dai na so ki karasa min labarin nan a yau".
Ta ce, "Some other tym, bana jin dadin jikina sosai, sannan ga yamma ta yi".
Suka jero suna tafiya cikin hirarraki kanana, sai ka rantse mata da miji ne".

****

Abbas ne a kitchen din gidan yana kiciniyar daura masu sanwar abinda za su ci da daddare. Ba komi bane ‘source’ ce da za a ci da biredin alkama.
Ya kammala y rufe komi ya gangara kantunan dake kasa ya mika ‘yan sisinsa (penny) ya sayo biredin ya dawo kitchen din, ya dauki na Lailah da nufin ya fara mika mata kafin ya dawo ya dauki nashi.
Ya iso jikin kofarta ya kwankwasa, shiru ba a amsa ba. Ya sake kwakwasawa a karo na biyu......
A wannan lokacin da ya dan saurara, sai ya jiyo tana kakarin amai kamar fitar rai.
Don haka ba tare da wani tunani ba ya murda kofar a sukwane ya isa gefen gadon da ta jike da amai, ya aje plates din da ke hannunsa a gefe.
Ya ce, “Lafiya Lailah?’
Cikin tsananin tashin hankali da firgici bayyananne, zane varo-varo a kyakkyawar fuskarsa.
Ta yi mai nuni da ya ba ta ruwa, ya dauko gorar ruwa a ‘bed-side fridge’ dinta ya valle hancin ya mika mata, ta kuskure baki ta wanke fuska. Ta koma jikin filo ta kwanta tana maida numfashi a galabaice.
Duk abin da ta saka ma cikinta a yinin ranar ta amayar da shi, har da wani kore-kore cikin aman. Sabida babu sauran abinda za’a amayar din.
Ya zage tukuru yana gyara wajen bayan ya tattara zanin gado ya jefa a bokiti.
Sai da ya gama aikin aman tas ya fesawa dakin ‘room-fresh’ mai dadin kamshi, zuwa lokacin Lailah ta fara rawar dari, hakoranta sun soma karo da junansu.
Ta ce, “Rufa min bargon nan, Abbas sanyi...”
Ya dauki lallausan bargon ya rufa mata, amma ba ta daina rawar darin ba sai ma abin da ya karu.
Don haka ya gangara kasa ya koma nashi dakin ya dauko nashi bargon ya kara mata. Ya koma kan kujera daya kwallin-kwal dake cikin dakin ya zauna cikin kulawa ya ce.
“Za ki iya kokartawa muje asibiti?”
Girgiza mishi kai ta yi alamar “A’a, ba za ta iya ba”.
Lallai lafiya… uwar jiki, lokaci daya ta rafke Lailah a daki, shima ta hana shi hidimomin gabansa, balle halartar ‘lectures’.
Ya je dai ya ba da edcuse a kan Lailah, amma shi ba shi da hujjar da zai bayar. Don haka ciwon Laila tsawon sati guda ya shafi karatun sa ba da wasa ba.
Wannan ba shine a gabansa ba, lafiyar kawarshi, abokiyarshi, aminiyarshi Lailah ne.

A rana ta bakwai ne dai ya takura mata ala dole ta mike, duk ta rame ta zaizaye dama jikin ba wani jiki ba.
Ya dauko jibgegiyar coat dinta ya jibga mata, ya manna mata bakar hula da socks na hannu.
A wannan lokacin na karshen watan January, lokacin da London ke fama da snow , har ya soma tunanin rashin sabo da yanayin ne ya haifar ma da Laila wannan mugun zazzavi da vomiting. Wato (amai)
To amma ina ruwan sanyi da vomiting (amai)? Haka dai suka gangara kasa, suka hau bus, ko da yake daga nan ma unguwar da suke (Acton Town) za su iya karasawa NHS da kafafunsu, sai dai don baya so ta jigata ne.
Abinki da dalibai ma’abota inshora, nan da nan su kai ‘booking’ ganin doctor, aka soma daura

Lailah a kan gwaje-gwaje, wanda ya kai su hard a su dibar fitsari, jinni, don binciken zahirin abin da ke dmaun ta.
“Congratulations!”.
Siririyar Baturiyar ta ce da shi tun kamin ta iso kujerar da suke zaune. A tsammaninta su din mamallakan juna ne (ma’aurata).
Ta sake cewa, “Congratulations, nan da watanni bakwai muna maka albishir din mallakar bouncing baby”.
Daga shi har Lailah ba su fahimce ta ba. Don haka ya kama hannun Laila kada ta fadi suka koma ofishin doctor.
Ya ce, “Meke faruwa ne doctor? Me ke damun Lailah?”
Ya washe baki shi ma cikin yi mishi albishir din cewa matar shi na dauke da juna biyu ne”.

Wata kara da Lailah ta saki ta kuma sulale a nan ta fadi sumammiya ta razana su. Abinka da wadanda suka san muhimmancin patient, nan da nan aka yi rubdugu a kan Lailah aka kuma umarce shi da ya fita.
Ya dawo bakin kofar dakin likitan ya jingina da bango, hankalinsa ya masifar tashi, ya rasa dalilin suman Lailah don anyi mata albishir din kasancewar ta mai juna biyu.
Ba da auren ta ba? Me zai dame ta don an ce tana da juna biyu? Duk da can a karkashin zuciyarsa wani dunkulallen abu ne ya tokare kirjinshi, tun sanda Lailah ta soma ba shi labarin rayuwarta, ya kuma fahimci tana da aure, ya soma canja tunanin shi a kanta, ya kuma yi dalilin da ya sa ya fara ja baya da ita, amma tun da ta fara ciwon ya samu kanshi da son taimaka mata.
Amma bai ga dalilin da don an ce tana da juna biyu za ta daga hankalinta ba. Al’amuran rayuwarshi gaba daya sun canja, tun haduwar shi da Lailah.
Yana fama da wani lamari mai girma cikin zuciyarshi a kanta, shi kadai ya san halin da yake ciki a kan Lailah, dare da rana, wuni da safiya. Tun a ranar da ya soma dora idanunshi a kanta. Hatta a marigayiyar matarshi bai tava tsintar kanshi a al’amarin dake faruwa da shi a yanzu game da Lailah ba.
Ba ya tantama soyayya ce mai girma, kuma mara adalci. Tun da dai wadda ake mawa matar aure ce ga wanin sa. Don haka ya san cewa al’amarin ba zai tava yiwuwa ba.

Kwanansu biyu a asibitin ana yi ma Lailah karin ruwa da kulawa ta musamman. Tunda Lailah ta dawo cikin hayyacinta kuka take, wanda bai san dalilin sa ba.
Rarrashin duniya Abbas da ‘nurses’ sun yi amma kamar kara izata suke, har aka sallamo su suka dawo gidan da suke zaune Lailah ba ta bar tsiyayar da hawaye ba.
Ya yi sallama a kofar dakinta dauke da plate na soyayyar ayaba (plaintain) da apple (tuffah) a cikin leda, da fresh milk har da ‘ya’yan inibi.
Ya ja tebir ya dora mata ya sanya ta a gaba a kan dole sai ta ci, ta soma ci kamar mai cin magani, ta rasa inda za ta sa kanta. Rabonta da abinci har ta manta.
Kuka take wurjanjan a lokacin da take rokonsa da ya taimaka mata a cire cikin da ke jikinta. Abbas ya sa mata ido yana kallon ta, a ladabce ya ce.
“Lailah”.
Ta saurara da kukan ta dube shi tana shessheka.

“Ke fa da bakin ki kika gaya min cewa kina da aure?”.
Ta daga mishi kai bayan ta sa havar kallabinta ta fyace wata matsiyaciyar majina.
“To ‘why’ (meyasa) za ki ce a kashe rai alhalin da ubansa?”
Maimakon ta ba shi amsa sai ta kara tsinkewa da kukan, na yau har ya fi na kullum, tamkar wadda aka yi wa bushara da rasuwar uwa da ubanta.
“Allah-kareem!”
Ya furta cikin zuciyarshi. Ji yake kamar ya dauko damuwar Lailah ya aza ma kanshi don ta huta. Shi bai ga dalilin da za a cire cikin da yake da uba ba. Koma babu uban shi a haife dan a ba shi yana so.
Babban burin shi kenan a duniya, ya ganshi da dan kanshi, wanda kuma gurin haihuwar ne Allah ya karvi ran matarsa.
“Lailah idan ba kya son dan ne ni ki haife ki bani, wallahi Lailah baki san yadda nake addu’ar Allah ya bani da ba.
Idan Ubangiji ya baka da ya yi maka kyautar komai, wadda wani ko wata bazasu tava baka ba. Ki tuna ke musulma ce, wadda ko ba dade ko bajima za ta tadda Ubangijinta.
Shin me za ki ce da Ubangiji a bisa wannan muhimmiyar kyauta da ya yi miki kika butulce? Baki da tabbacin cewa wannan shine kadai kwanki a duniya. Wasu suna nan suna nema ruwa a jallo koda zasu karar da  dukiyoyinsu, amma Allah bai basu ba
A matsayina na dan uwanki musulmi ina mai tunasar da ke cewa, idan kika zubar da ciki kamar kin kashe rai ne, kuma wallahi Allah ba zai barki haka ba.
Idan laifi uban dan ya yi miki za ki huce a kan dan tayin dake karkashin mahaifa kin yi babban kuskure, wanda ko ba dade ko ba jima wata rana za ki yi nadama.
Idan bakya so ina mai shawartarki ki daure ki haife, ni Abbas ina so, ki bani. Zan yi mishi uba, idan bakya son uban shi, ko idan wani laifi uban nashi ya yi miki har ta kai ki ga yin wannan gurvatacen tunani.”
Lailah ta juyar da kai cikin matse hawayen idanunta. Ga dukkan alamu ranta ya soma sanyi. Ya ci gaba da yi mata nasiha hadi da ba ta misalai kala-kala, har ta saddakar da tana son fayyacewa Abbas dalilinta na yin hakan.
A ganinta idan ya ji dalilinta shine mutum na farko da zai goya mata baya ta yi abin da take da nufin yi.
[12/17/2019, 17:51] Takori: ****
Matsala ta biyu da muka kara cin karo da ita ni da Mohammed, ita ce matsalar rashin haihuwa. Shekarun mu biyar tare amma haihuwa shiru, babu ita babu alamunta.
Daga baya ma Mohammed ya zo yana zargina da yin ‘planning’ a voye, bayan kuma a zahiri ba hakan bane.
Muka koma biye-biyen teburin likitoci suka yi ta zakule-zakulen su har suka tabbatar matsalar daga gare shi ne.
Idan har yana son haihuwa to yana bukatar ai mishi aiki, don haka daga ni har shi muka tattara maganar haihuwa muka yi watsi da ita. Sai dai duk inda Mohd ya ga ‘ya’ya sai ya karar da lokacinshi a kansu.
Na lura Mohd na matukar jin dadin yadda alakata take da Sa’eed, domin dan gaban goshinsa ne, su biyu kacal iyayensu suka haifa kuma mahaifinsu ya jima da rasuwa.
Yana so ya zo ya tadda mu a falo muna ta nishadi, tunda dai shi baya da lokacin mu.

A wani weekend Sa'eed yake yi min zancen yarinyar da zai aura Zaliha, ajinsu daya ne a makaranta, yana son in fadawa Mohd. don gidan su Zalihan sun takura idan ba zai fito ba za su bawa wani. Shi kuma yana son yarinyar sosai.
Na ce,
"Sa'eed da rigima kake, kana fafutukar kwalin karatun farko za ka hada ma kanka aure?"
Ya ce,
"Wallahi da gaske nake Antina, ina matukar son Zaliha, idan kuma ban same ta ba ban san ya ya rayuwata za ta kasance ba, ku taimaka mani".
Na ce, "Ni don ta ni ai mai sauki ce, amma Yayanka ka fi kowa sanin shi".

Ko da Mohammed ya zo, bayan wasu watanni kamar yadda ya saba, na yi mishi zancen, bai wani ba zancen muhimmanci ba, don haka ya koma ta vangaren Hajiya.
Na ke jin ita ce ta tusa Mohammed din a gaba sai da ya amince aka yi ma Sa'eed baiko da Zaliha, amma aka ja lokacin sosai zuwa sanda za su kammala karatun su.
Sa'eed ya dauko Zaliha har gida ya kawo min ita, yarinyar kyakkyawa amma ta waye da yawa. Na yi mishi maganar hasashe na ya ce "haka nan nake son abata".
Gab da kamawar watan bikinsu muka samu wani mummunan labari, wato hatsarin Zaliha da iyayenta a kan titin Abuja, duka babu wanda ya tsira.

Hakika Sa'eed ya shiga matsanancin tashin hankali wanda ta kai shi da furucin babu shi babu aure a duniya.
Shekarun mu biyar da aure Sa'eed ya tafi NYSC jihar Cross-river. Don haka sai na kasance cikin kadaici da kewa. Da dai kadaici ya isheni sai na tattara na tafi Egypt wajen mahaifiyata, bayan na nemi izinin Mohammed ta waya.
Zamana da 'yan uwana sai ya zamo magani ga dimbin damuwar da nake ciki. Momi ta kasa daurewa don ganin muguwar ramar da nake yi. Ta sani a daki a wani maraice tana tambaya ta. Ban voye mata komi ba na zayyane mata matsala ta. Momi ta ce,
"Tun farko ke kika kawo yaron nan Lailah kika ce kina son shi, alhalin kin san yanayin aikinsa, ban ga dalilin da za ki daura ma kanki damuwa yanzun ba.
Idan har kina ganin ba za ki iya ba, to tun wuri ki nemi da ya sauwake miki".
Na yi jim! Ina tauna maganar Momi, in ce Mohammed ya sake ni? Abune da ba zan tava iyawa ba, domin dai auren soyayya muka yi, duk da halayen sa na rashin kulawa da soyayya a gare ni 'still' ina son kaya na.
Don haka har na koma Bauchi ban yankewa kaina shawarar komi ba, tunda dai 100% na yarje ma zuciyata ina son mijina.
Ginshikin aure kam ba na samu, wato auratayya. A hankali dai na fahimci jinsin mu ba daya bane, yana cikin jinsin mutanen da seduality wato auratayya bai dama ba, ya yin da ni kuma nake a rukuni akasin hakan.
Dole haka na daure ina ci gaba da cin dan uban hakuri. Da dadi ba dadi muna zaune a hakan. Rashin Sa'eed sai ya zamo min kamar rashin babbar aminiya. Ya shiga jikina sosai, mun amincewa juna, duk wata matsalar junanmu da junanmu muke shawara, na kuma lura sosai Mohd ba karamin jin dadin hakan yake ba.

Ta duba agogon ‘swatch’ dake daure a fatar hannun ta, ta dubi Abbas, “lokacin sallah yayi, mu je mu sauke farali”. Ya sauke tagumin da yayi da hannayenshi biyu yana sauraronta, ya mike yana duba nashi agogon shima.
****

Kwance yake a mike bisa doguwar kujerar da ke karamin falonshi yana nazarin jaridar ‘Daily-Trust’, sai dai da ganin irin kwanciyar da ya yi ka san ba ta lafiya ba ce, alal hakika yana cikin matsananciyar damuwa.
A karo na wajen dari da hamsin kenan, ya sake ‘dialling no Lailah, kamar yadda computer ta saba yi mai vavatu yau ma vavatun ta shiga yi mishi, cikin sanar da shi layin a rufe yake.
Kararrawar shigowa falon ta yi kara, da kamar ba zai kula ba, ya dai daure ya mike ya isa ga kofar ya bude.
Ya bayyana a falon cikin kyakkyawar shiga ta caftan na farar shadda mirrow, suka yi ido hudu da dan uwansa da baya da ya shi a duniyar baki dayanta.
Ya matsa kadan ya ba shi hanyar wucewa suka zauna a tare cikin kujeru masu fuskantar juna.
A saluve Sa’eed yake kamar wanda ya sha duka, ya ce, “Yaya har yau ba labari?”
Bai saurari amsar shi ba ya ci gaba da cewa.
“Ni ina ganin a kai zancen cigiya kafafen yada labarai”.
Mohammed bai amsa ba, illa ya mike ya isa ga kitchen ya fiddo ma dan uwanshi abin sha mai sanyi na’ya’yan itacen ‘tropical juice’ hade da tambulan, don ga dukkan alamun shi a gajiye yake da uwar tafiyar da ya niko tun daga jihar Cross-river.
Hakika yana tausaya ma dan uwanshi halin da ya shiga a dalilin vatan matarshi, wanda kuma shi ne sila.
Anya idan Mohd ya ji irin cin amanar da ya yi mishi zai tava yafe mishi? Idanuwansa suka kada jajir, amma sun kasa tsiyayar da hawaye.
Ya tashi tsamo-tsamo da shi ya nufi hanyar baskwata, don ganin ga dukkan alamu Mohd din bai son damu yanzu cikin halin da yake ciki.
Wayar shi dake gefe ta yi ruri, ya mika hannu a kasalance ya dauka. Isma’il ne yayan Lailah. Bayan sun gaisa ya ce,
“Babu labari a nan Bauchin har yanzu? Mu ma nan mun baza cigiya har a sauran kasashen da ke makotaka damu wadanda take da kawaye a can, ba amo ba labari”.
Mohammed ya ce
“Nan din ma babu, amma yanzun nan Sa’eed ya kawo min wata shawara a kan na baza cigiyar a nan gida Najeriya”.
Suka yi sallama kowannen su zuciyar kamar-kamar me.

A iyaka tunaninsa, bai san laifin da ya yi ma Lailah takamaimai ba, lafiya kalau suka rabu. Sai dai da ya yi nazarin wasikarta ya fahimci a kan halayyar da yake mata ne ta gwammace ta yi nisa da shi, tun da ta kasa magantawa kanta, shima ya kasa maganta mata.
To a yau ga shi a dalilin halayensa aikin ma gaba daya ya kasa a dalilin rashin ta.
Daman an ce baka sanin muhimmanci da amfanin mutum sai ranar da ya suvuce maka. Ya rasa inda zai sa kansa a dalilin rashin Lailah, ya yi nadama matuka da irin halayen da yake yi mata

wanda ba sau daya ba, ba sau biyu ba ta sha gaya mishi cewa ba ta so, ya daina.
Amma bai dainan ba, sai sanda ya rasa ta. Shi da dan uwanshi suka shiga kafafen yada labarai na garin Bauchi suka sa cigiyar Lailah har da hotunanta.
Amma har kwanaki suka tura shiru kamar an shuka dusa. To ina ga mahaifiyarta da ta tsugunna ta haife abarta?

****

Ya kwankwasa kofar dakin a hankali rike da karamin 'tray' da ya dauro karamin 'tea flask' da kayan shayi.
Ta zo ta bude cikin nutsuwa ta yi wani irin fari ta rame ta zuge duk a lokaci daya. Ya aza 'tray' din a kan wani dan karamin tebir da ke dakin, ya ja kujera ya zauna ya soma hada mata shayin, ya kammala ya shiga firfitawa.
Kallon shi take cike da tausayin kulawa da taimakon da yake yi mata a matsayinshi na wani mutum da basu hada dangantakar komi da shi ba, face abokin kan hanya kadai.
"Abokin kan hanya?"
Ta kalubalanci furucinta. A gare ta zuwa yanzu matsayin Abbas ya zarta wannan. He is someone she respect most!.
Ya shiga zuciyarta da yawa, ta yadda har tunaninta ke canzawa a kanshi, zuciyarta na gayyatar shi da wani matsayi mai girma. To ita kanta ba ta da 'standing', abin nufi. Ba ta san matsayinta ba balle ta soma tunanin irin wannan, tana da aure ko babu? Ba ta sani ba.
Har ya kammala firfita shayin ya miko mata ba ta farga ba, ta yi nisa a tunanin ta.
Ya ce, "Lailah!"
Ta yi firgigit ta ankara. Ya mika mata shayin wanda ba ko tantama tana sha za ta amayar da shi.
Ya kan ce, "Ya fi babu dai tun da ko ya ya ne wani zai zauna a cikin hanjin cikinta".

Abbas gwanin jinya da karfafa gwiwa, Abbas mai kyau, Abbas mai kirki…ya kan nuna mata wannan ba komi bane, babu wanda baya fuskantar challange (kalubale) a rayuwa. And is up to us to accept such challenges mu bita da duk fuskar da rayuwa ta zo mana.
Ya ce,

"Ni tashi na yi ba Uwa ba Uba Lailahhh. Haka nai ta gararramba a gidan wan mahaifina, sai dai na kasance daga cikin hazikan yara, duk da gararramba ta.
Da na kare karatun sakandire gwamnati ta dauki nauyin karatuna a nan Ingila, kin ji abin da ya rabo ni da gida.
Duk karshen shekara ina zuwa in gai da wan mahaifina. Da na kare karatun digiri na farko ya yi min aure da diyarshi Hasina, muka taho nan tare, inda ta rasu a ya yin haihuwa.
Na zo gida Najeriya ne gai da Baffan nawa, na hadu da ke a filin jirgi". Wannan shine takaitaccen tarihi na.

Ba ta san me ya sa ba hankalinta ya kwanta da Abbas sosai ba, har take jin shine mutum na farko da za ta kwaye ma cikinta, a kalla ko ba komi zai ba ta shawarar da za ta amfane ta, da

kuma yadda za ta yi ta gyara kurakurenta.
Ya ce,
“Uhm? Ina sauraron ki...?”

****

“A kullum ina tausar Sa’eed a kan rasuwar Zaliha, ina nuna mishi ya yi hakuri haka Allah ya rubuta musu cewar ba mamallaka juna bane a gidan duniya.
Ya hakura ya nemi wata da ya kare NYSC ya yi auren shi. Duk da ina jin wani dan kishi-kishin abin a raina.
Shakuwata da Sa’eed har ta kai matsayin da zuciyoyinmu suka soma karkacewa, al’amarin da bamu tsammana ba (sha’awa). Na fahimci hakan ne daga yanayin kallon da Sa’eed ke min, da wanda nima nake mayar mishi.
Ya zamanto ko abu Sa’eed zai karva a hannuna sai ya san yadda ya yi hannun shi ya gogi fatan hannuna.
Muka soma wata irin rayuwa ta daban har ya zamanto Sa’eed babu inda ba ya shiga a dakuna na ba tare da la’akari da halin da zai iya samuna a ciki ba.
Muka sake muka shantake muna abin da muka ga dama, sai dai bamu tava yin babban aiki ba, wannan kam muna kula muna jin tsoro. Bamu tava yi ba, kuma bamu da niyya. Amma ‘yan ‘romances’ dinnan bamu dauke su komi ba.
Har ya kammala hutun zangon shi na farko na NYSC ya koma cike muke da kewar juna. Kamar mu tafi tare.

Wasu watanni uku ris Mohammed ya kara a kan wadanda ya saba, suka zama shida ris kafin ya waiwaye ni.
Bai san zuwa wannan lokacin ni tuni na rufe babinshi na daina kewar shi ba, don haka ya yi mamakin yadda har ya yi ‘yan kwanakin da zai yi ya kare zai koma bai ji na yi ‘complain (korafi) ba.
Bai sani ba ni tuni na samu madadin sa ba. Don haka lafiya-lafiya muka rabu wannan karon yana ta sa min albarka.
Wata ranar lahadi Sa’eed ya zo har kofar dakina ya yi sallama, sanye nake da kayan barci masu laushi ina shirin kwanciya barci.
Sai ya tsaya kallona galala, shi kadai ya san abin da yake kissimawa a ranshi. Ya kare ya ce.
“Aron wayarki nake so ki bani zan kira Hajiya wayata babu chaji”.
Na dauko waya na taso zan miko mishi ya hada dani ya rungume cikin wata irin rikitacciyar siga.
Na samu kaina da biye mashi, domin nima cike nake da kishirwar abin.
Cikin dan lokaci mune har a kan gado cikin al’amarin da ba zan iya fassarawa ba. Ban tava samun ‘satisfaction’ (biyan bukata) da Mohammed irin yadda na samu a Sa’eed a ranar ba.
Wannan shine babban kuskuren da na tafka a rayuwata, ya kuma yi dalilin barowa ta gida, don ban ga sauran amfani na a cikin gidan ba.
Da muka dawo hayyacin mu ne na fahimci aika-aikar da na tafka, ko in ce muka tafka.....”
Ta dakata ta share hawayen da ke kwaranyo mata, ko motsi Abbas bai yi ba, yawun bakinshi ya dauke, ya kuma rasa wa zai bai ma laifin a cikin su duka ukun.

......Tsoron abin da muka aikata ya shige ni. Tsoron ingancin addinina da aurena ya addabe ni. Tsoron mahaliccina da abin da za ya tambaye ni ranar da na gamu da shi ya shiga girgiza zuciyata.
Mohammed kam bai sani ba, amma Ubangijina Ya sani, kuma ni da na aikata na sani. Sai dai duk na dauki laifin na aza ga Sa'eedu, wanda kuma daga baya da na yi kyakkyawan tunani sai na ga cewa dukkanin mu muna da laifi.

Na jima da neman gurbin karatu a wannan makarantar ta yanar-gizo ba tare da sanin Mohammed ba, kuma 'admission' bai zo mini ba sai a dai-dai wannan lokacin.
Na duba gabas na duba yamma, kudu zuwa arewa, ban ga inda zan kai nadamata ba, baya ga tafiya in barsu baki daya.
Don bani da bayanin da zan yi ma Mohd. Bani da bakin da zan fuskanci Ubangijina idan na cigaba da zama dashi zaman zina. Amma shi din ai mai afuwa ne ga bayinsa. Don haka na taho, har kuma hakan ya yi sanadiyyar haduwata da kai a filin jirgi.

Sai kuma ga wani sabon al'amarin.... 'ciki'?"  Ta furta cikin tashin hankali.
Bana tantama ciki na Sa'eed ne, don kamar yadda lissafin asibitin ya nuna, ya yi dai-dai da ranar faruwar al'amarin Abbas........"  Ta ci gaba da kuka.

Da da hali, da ya rungume ta ya rarrashe ta, shi kam tun da uwarshi ta kawo shi duniya bai tava jin irin wannan kwamacalar ba, kuma iya amfani da hankalinsa da tunaninsa ya kasa rarrabe wane ne mai laifi?
Ya gyara murya idanunshi sunyi jawur, ya zamo daga cikin kujerar da yake zaune, ya durkusa ya zauna a gabanta, ya mika hannuwa kamar zai kamo hannuwanta sai ya fasa.
Cikin muryar lallashi ya ce, "Lailah! Ni dai shawarar da zan baki kada ki kashe rai. Ki ji tsoron mahaliccinki, ki bar masa kudura da iradarsa.
Ni Abbas na ji nine uban dan da za ki haifa, ki haife ki bani zan yi mishi uba har karshen rayuwata.
Babu wanda ba ya yi wa Ubangiji savo, dukkanin mu masu savo ne ta wannan hanyar  ko ta waccan.
Abin bukata shine, tsarkakken tuba da tabbacin ba za a sake komawa izuwa zunubin ba.
Sannan a ganina bai kamata ki yiwa Momin ki da 'yan uwanki haka ba, yanzu gashi kin barsu cikin tashin hankali.
Gara da a ce mutuwa ki kai sun san kin mutu, amma vatan dan mutum ba karamin tashin hankali bane ga iyaye.
Ina mai shawartar ki da ki sassautawa zuciyarki, duk wani tsanani yana tare da sauki, kuma babu wanda ba ya yi wa Ubangiji savo a bisa rashin sani ne ko akasi. Sai in ce ke kuma wannan ita ce kaddarar ki".
Hankalinta ya kwanta da nasihohinsa, amma a duk lokacin da ta yi tunanin wai dan kanin miji za ta haifa, da aurenta, tana ji tana gani, zuciyarta kara dimaucewa take.
Ya ci gaba da tausarta da kalamai kala-kala, yana nuna mata wannan ba shi ne karshen rayuwar ba. Ta ci gaba da istigfari ta fuskanci rayuwar dake gabanta.
[12/17/2019, 18:28] Takori: ****

Ya kwanta a hankali bisa madaidaicin gadonsa, ya rasa abin da ke damun sa. Wani al'amari ne da bai tava faruwa da shi ba ke cin ransa.
Duk wani tunani nasa da ya mallaka ya dunkule ya warware a kan LAILAH. Bai tava tunanin Lailan matar aure ba ce yake kauna, yana da burin ta zamo uwar 'ya'yansa, ashe dukkanin su basu da 'yancin wannan al'amarin.

Ya yi parkin din motarshi kirar 'Ferrari' a kofar gida mai malalen siminti, irin gidajen nan na masu kudin da can wani lokaci da ya shude cikin garin Jama'are.
Ya fito ya rufe kofar ya bude boot din motar ya yafito yaran da ke ta wasa a gida mai kallon su, suka zo ya sanyasu suka kwashe kwandunan doya da dankali su kai cikin gidan.
Ya yi sallama a kofar dakin mahaifiyarsa, daga can ciki Hajiya Baida'u ta amsa tare da yi mishi kallon kauna, kafin ta amsa sallamar shi. Ya zare takalman shi ya sanya kai cikin dakin.
Ya samu kujera mai fuskantar mahaifiyarsa ya zauna, kai da ganinsa da kuma irin zaman da ya yi rigija…. ka ga wanda kwanciyar hankali ya yi wa karanci.
Ta tura mishi kwanon gurjiyar dake gabanta kamin ta mike ta je kitchen ta shiryo masa abinci mai rai da motsi.
Sai da ya ci abincin ya sha ruwa kafin da ta yi masa wani irin kallo ta girgiza kai.
"Anya Mamman! Kana nemawa kanka sauki cikin tunanin yarinyar nan? Na rantse da Allah ba ta sonka, da tana sonka da ba ta yi maka wannan abun da ta yi ba, data tabbatar zai daga maka hankali, tunda tana sane ta yi tafiyarta ba shi ke nan ba?
Kiri-kiri ta nuna maka ta gaji da zama da kai ne don baka haihuwa, shi ya sa ta yi tafiyarta amma ka bi ka kwazzabi kanka banza da wofi, sai ka ce dan kankanin yaro ne ya vata. Kana ta asarar kudinka a cigiyar banza.
Tsiyar auren 'kwara' kenan, don ba za su zauna ba. To yaran yanzu ne idan kun so auren mace kamar da ya so fitowa cikin mahaifiyarshi, ba za ku yi aure a gida ba inda a ka san mace, aka san asalinta, a'ah, ku sai kyal-kyal banza".

Maganar Hajiya ta shige shi ainun, da gaske Lailah ba ta sonsa! Ko ta so shi a baya, yanzu ta daina!! Da tana sonsa da ba za ta tava gajiya da zama da shi ba, kowanne irin hali ne da shi kuwa.
Balle kuma yana iya kokarin sa wajen fita hakkin ta. Da gaske ne Lailah gajiya ta yi da zama da shi don rashin haihuwa shi ya sa tai tafiyar ta?
Zai so ya ganta a wannan lokacin, ko don ya yi mata wannan tambayar.
Hajiya ta gyara zamanta ta ce,
"Ban da abinku na 'ya'yan zamani da ba a yi muku gwaninta, da sai in ce mai zai hana ka yi auren ka ka huta?
Ga nan 'yar kanin mahaifinka A'isha, ta gama karatun digirinta na farko a jami'ar Bayero, mai zai hana ka tuntuve ta?"
Ya yi ajiyar zuciya abin tausayi, ya ce, "Hajiya duk yadda kika ce dai-dai ne".
Ta ji dadi, ta shiga sanya mishi albarka.

A ranar ya soma zuwa wajen A'ishar, doguwa, baka, mai kyakkyawar sura. Ya yaba da hankalinta da nutsuwar ta, don haka ya sakarwa Hajiyar shi bakin aljihu ta soma shirye-shiryen

aure.
A karshen satin Sa'eed ya zo, nan ya tsinkayi labarin auren. Ya samu dan uwanshi a gidansa da yammacin ranar asabar.
"Yanzu daga Jama'are nake, Hajiya ke gaya min wai ka amince ka auri A'isha".
Ya ce, "Eh, haka ne, Lailah ta yaudare ni Sa'eed, ta yadda har ban san ba ta kauna ta ba sai yanzu, da tana kauna ta da ba ta yi min abin da ta yi min din nan ba".
Sa'eed ya ce,
"Ba yaudara ba ce Yaya! Idan ka dubi wasikarta da kyau, za ka fahimci halayyarka ne ba ta so. Sai dai nima na yi mamakin dalilin da ya sa ta zavi tafiya, fiye da ta nemi saki".
Ya ce,
"Koma dai mene ne ni aurena zan yi, tukuicin kaunata gareta kenan, to ta je, Allah ya ba ta sa'a".
Sa'eed ya ce,
"To idan kuma ta dawo fa?"
Ya ce,
"Bana jin Lailah za ta taba dawowa gare ni. Da za ta dawo, da zuwa wannan lokacin koma mene ne in ta yi don ta hora ni ko don na gyara kuskuren da nake mata da tuni ta dawo".
Sa'eed dai ya rasa abin cewa, can karkashin zuciyarsa kuwa nadama ce fal, don ya san shine silar wannan al'amarin.
A wani bangaren tunanin ranar da Allah zai tona asirin cin amanar da ya yi wa dan uwansa mai kaunarsa yake yi, don ya san ba shi da fuskar da zai dube shi daga ranar, ya kuma tabbata ko ba dade ko ba jima wata rana Allah zai bayyana al'amarin.

****

Ya kwankwasa kofar ta taso a hankali ta bude, sanye da bakar jallabiya kirar Oman a jikinta. Ya shigo rike da ledar magunguna a hannunshi na dama, ya yin da hagun ke rike da wata ledar cike taf da 'ya'yan inibi.
Suka yi ma juna murmushi a takaice, ya ja kujera ya zauna ita kuma ta koma bakin gadon tana fuskantar sa.
Ya ciro magunguna a leda ya valla ya mika mata tare da dauko mata gorar ruwa mara sanyi a firinjinta.
Ta amsa ta soma hadiya, ya ce,
"Lailah, yau dai ki daure ki shirya muje makaranta, don na ga jikin da sauki. An kafe maku time-table din edam tun shekaranjiya".
Hanadi, mutuniyar Somalia wadda dakinta ke kallon na Lailah ta yi masu sallama ta shigo, ta samu gefen gadon da Lailah ke zaune ta zauna suka gaisa.
Ta ce,
"Kwana biyu bana ganin ki kin fito ko kin shiga kitchen, shine na ce bari in zo in ga ko lafiya?"
Tana maganar ne cikin harshen Turanci. Cikin jin dadin kulawar da ta nuna a gare ta ta ce.
"Wallahi kuwa, ina fama da zazzavi ne".
Ta ce,
"Ayya! Ga shi nan duk ya ramar da ke, Allah ya kawo sauki".
Su duka suka ce,

“Ameen”.
Suka dan tava hira Abbas bai tofa musu ba, sannan ta tashi ta yi musu sallama ta fita.
Shi ma fita ya yi don ya ba ta dama ta shirya. Ta dauko farar suwaita ta sanya, ta kawo doguwar ‘coat’ har gwiwarta ta sanya tare da dogon wandon ‘cherokee jeans’, ta sanya socks na hannu da na kafa da rufaffen bakin takalmi maras dunduniya.
Ta dauki katuwar jakarta mai dauke da littattafanta ta rataya, ta janyo kofar dakinta ta sa makulli ta rufe.
Ta gangara kasa dakin Abbas, ta kwankwasa ya fito shi ma a shirye cikin DKNY, (trouser and shirt), da bakar suwaita a kai. Ya yi matukar yin kyau, suka jera suka fita. Suka tsaya a ATM na bankin ‘Lioyds’ ta dauki kudi suka karasa makaranta da kafafun su.
Da suka dawo suka tsaya a kantin ‘Morrisons’ dake nan cikin unguwar su (Acton) suka yi ‘shopping’ suka dawo gida.

Haka Lailah ta ci gaba da rainon cikinta da taimakon Abbas, tun tana damuwa da bakin ciki har ta daina.
Yau da lafiya gobe babu, haka ta daure tana karatun ta. Sai da cikin ya shiga watanni biyar sannan ta samu lafiya, kai in ka ganta a wannan lokacin ba za ka ce ciki gare ta ba, saboda yanayin shigar ta na kaya masu kauri.
Allah sarki Abbas, tun daga wannan lokaci ya soma sayan kayan jarirai yana tarawa (unisex). Lailah dai ba ta tava sayen komai ba, ita dai ta mika wuya ga duk yadda rayuwa ta zo mata, don ba ta da tsimi ba ta da dabara.
Abbas ya samu aikin koyarwa (temporary) a wata makarantar sakandire (private), ya zamanto Lailah ta daina tava ajiyarta ta banki, ya tsaya mata a kan komi, itada jaririnta dake ciki.
Katon na locozade, katon na fresh milk, cret din kwai, kwalin apple da kwalin inibi, duk haka yake ajiye mata ba ta kuma isa ta yi godiya ba, yanzun nan zai hau fushi da ita.
Ya hanata yava ajiyarta ta banki sam, tana mamakin wannan al’amari, kulawar da yake nuna mata da kwarin gwiwar da yake ba ta ya wanke duk wani bakin ciki da ke zuciyarta, sai fatan Allah ya raba ta da cikin da ke jikinta lafiya.
Cikinta ya shiga watanni na tara, ranar wata alhamis sun dawo daga awo a NHS. Abbas ya mika mata waya ya ce lallai ta kira Mominta su gaisa.
Atleast ko ba ta fadi mata inda take ba, ta sanar da ita tana nan lafiya don hankalinta ya kwanta. Yana mai nuna mata mace mai haihuwa a kan gava take, baya fata, amma in ta  mutu a ya yin haihuwa me za ta ce da Ubangijinta a kan mahaifiyarta?
Jikinta ya yi matukar sanyi da nasihohin sa, jiki a sanyaye ta soma dialling number Momin, wadanda suke kamar karatun sallah a cikin kanta.
Bugawa daya- biyu Momin ta dauka, ganin bakuwar lambar ta kasar Ingila. Lailah ta yi sallama Momin ta amsa, sai dai ba ta gane mai maganar ba.
Lailah ta kai hannu ta share hawayen da suka zubo mata ta ce,
“Momi nice Lailah.....”
Momi ta ce,
“Hasbunallahu wa ni’imal wakil! Lailah!! Ashe kina raye kika tafi da gangan kika barmu cikin tashin hankali?”
Ta soma kuka. Ta ce,

"Wallahi ba da son raina bane Momi".
Ta ce,
"Koma me ke damun ki Lailah da har ya sa ki barinmu na dauka kafin kowa ya ji ni za ki fara nema ki fada min damuwar ki, amma ba ki tsallake ni ki barni cikin tashin hankali ba.
Da auren ki Lailah…….. ki tsallake mijinki ki tafi wata uwa duniya, kin san hakkin aure kuwa? Amma tun da hakan kika zavarwa kanki ai shi kenan".
Ta kashe wayar ba tare da ta sake sauraron ta ba.
Hankalin Lailah duk inda yake to ya yi kololuwar tashi, ta tabbata Momi ta yi fushi da ita, fushi kuwa mai tsanani tun da har ta ki sauraron ta.
Ta mika ma Abbas wayar tana kuka sosai. Ya barta ta yi abunta mai isarta, bai katse ta ba. A karshe tashi ya yi ya bar mata dakin don ta ji dadin yin kukan sosai.
Ya kuma cire layin ya sanya wani don shi ma yana ganin ba yanzu ne ya dace lokacin da Lailah za ta koma gida ba.

A can Alkahira Momi zugum ta yi cikin kwanciyar hankali, ko ba komi yanzu hankalinta ya dan kwanta tun da ta tabbatar Lailanta na raye, kuma cikin koshin lafiya.
Tun da har ta fara tunanin neman ta wata rana za ta yi tunanin dawowa. Ko da Isma'il ya shigo ta gaya mishi Lailan ta yo waya cewa ya yi ta ba shi lambar.
Ya gane lambar ta kasar Ingila ce, amma bai san wane yanki bane. Yayi-yayi ya kama layin ya kasa dole ya hakura.
A ranar Lailah ba ta yi barci ba, tausayin Mominta ya hanata barci na abin kunyar da ta jawo mata da kuma tunanin yadda za su karvi abinda za ta haifa.
Don ba za ta voye ba gaskiya za ta fadi duk ranar da Allah ya mai da ita gida, don ta san aurenta vatacce ne a addini.
Ga rashin Babansu ga rashinta, ta san abun ya yi wa Momin yawa, musamman yadda  take sonta fiye da sauran 'yan'uwanta, take kuma nunawa karara.
Suka smu hutun makaranta har na tsayin watanni uku. A irin wannan lokacin yawancin dalibai kowa kasarsu yake tafiya.
Ban da Lailah da Abbas, a wannan lokacin cikin ya yi katoto ya kuma yi kasa sosai, don haka suka sa rainon cikinsu a gaba, baya awa biyu cikakku bai san halin da take ciki ba.
Yana kuma yawan jaddada mata cewa duk wani motsi da ta ji ba dai-dai ba ta kira wayar shi. Ita har tausayi yake ba ta, ba shi ya kar zomon ba amma ya dauki rataya ya dora a kafadunsa.
Ranar litinin da daddare misalin karfe goma sha biyu na dare. Lailah na barci ta tashi da wani irin azababben ciwon baya, kafin ta ce meye wannan ta ji ta sharkaf cikin wani abu da ke bin kafafunta.
Ta soma salati nan da nan ta yi kokarin daukar wayarta a kan 'bed-side lamp' ta yi dialling no Abbas, ba wani vata lokaci ya ce
"ya ya ne? Haihuwar ta zo ne?
Ta ce, "I think so....."
Ya kashe wayar ya jefar da bargon da yake ciki ya kira hospital van, cikin 'yan mintuna ta iso da nurses ya yi masu jagora suka fito da Laila sai NHS.
Kwana daya, biyu Laila na cikin matsananciyar nakuda amma ta kasa, in ka ga kai komon Abbas a wannan lokacin sai ya baka tausayi.

A kwanaki biyun nan kaf ba abin da ya sanya a cikinsa sai ruwa, kamar shine mai nakudar.
A karshe aka sanya mata ruwan nakuda har leda biyar amma duk a banza. Don haka suka nemi shi mijinta (kamar yadda suke tsammani) da ya saka hannu ayi mata CS don ceton ta da yaron gaba daya.
Ba tare da wani tunani ba Abbas ya rattaba hannu, nan da nan likitoci suka fara aikin ceton rai. Ya samu 'waiter chair' ya zauna yana yi wa Lailah addu'ar fatan alheri.
Awanni biyu cur aka dauka ana aikin kamin wata nurse ta fito daga dakin da aka shigar da Lailah.
Da sassarfar shi ya mike ya cimmata. Ta dube shi cikin tausayi ta ce,
"Am sorry, yaron bai zo da rai ba. Ya dade da mutuwa a cikinta".
Ya yi ajiyar zuciya mai karfi ya ce, "Lailan fa?"
Ta ce,
"Komi lafiya tare da ita".
Ba ta rufe bakinta ba aka turo Lailan a kan gadon marassa lafiya zuwa dakin kwana.
Ya ja kujera dai-dai kan Lailah ya zauna, ba a jima ba ta bude ido sannu a hankali tana kallon shi.
Ya dora sassanyan hannunsa a goshinta, abinda bai tava yi ba, yanzun ma bai san yayi ba, rudewa ce. Ya ce,
"Are you alright Lailah?"
Ta girgiza mishi kai. Sannan ne ya samu nutsuwar zuciyarsa.

Kwanansu uku, wajen da aka yi wa Lailah 'operation' har ya fara kamewa, aka sallame su a rana ta hudu. Bayan asibitin ta hadata da nurse da za ta dinga zuwa gida tana taimaka mata har kwana goma sha hudu.
A kwanakin nan duka ba ta bar tsiyayar da hawaye ba, na asarar jaririnta. Hakannan Allah Ya dauki kaunar yaron Ya sanya mata. To haka shi ma Abbas da ya dauki rai ya dora a kan abin da Lailah za ta haifa. Ya gama yin duk shirye-shiryen tarvarsa.
Da ta murmure ta koma makaranta, kowa da suka sani tsammani yake ita da Abbas mata da miji ne, daga su sai Allah suka sani.
Jegon Lailah a kasar England, ya zamo wani abin tarihi a rayuwarta da ba za ta manta ba. Haka babynta da ya koma ga Mahaliccinsa har abada ba za ta daina tunaninsa ba.
Abbas ya ce, "Yana da kyau ta fara istigfari tun daga yanzu, domin yana ganin lokaci ya karato da ya kamata ta soma shirin komawa gida, tunda karatun ya zo karshe.
Ba tare da musu ba ta bi shawarar Abbas, sai dai har yau ba ta san da fuskar da za ta dubi Mohammed ba.

****

Watanni uku bayan nan suka karvi kwalin masters din su, shi kuma Abbas saura shekara daya ya karvi na PhD. Jikin Lailah a sanyaye suka soma shirye-shiryen tahowa Egypt.

A ranar wata litinin Momi ba ta zata ba ba ta tsammana ba, kararrawar kofar shigowa ta kada, mai sanar da su cewa akwai bakon d ake son a bude masa kofa.

Budewar nan da za ta yi suka yi arba da diyarta Lailah. Lailah ta rungume mahaifiyarta tana kuka mai tsanani.
Sanah da Najat, suka taso cikin al'ajabi suka rungume 'yar uwarsu. Tare suka rankaya falon cikin yi ma Allah godiya maras iyaka.
Sai da murnar ganin Lailah ta lafa, take sanar dasu tana da bako, don haka Momin ta ba wa Najat makullin sashen baki ta ce ta bude ma bakon Lailah. Akai masa ruwa da abinci.
Momi ta fiddo waya ta kira Isma'il daga wajen aiki ta ce ya zo yanzu-yanzu ya ga abin mamaki, addu'arsu ta kwana da kwanaki farat daya yau Allah Ya karva.
Isma'il ya iso gidansu a sukwane, amma maimakon ya yi murna si ya rufe ido ya soma balbale Lailah da fada, ta inda yake shiga ba ta nan yake fita ba a kan tashin hankalin da ta jefa su a ciki har tsayin shekaru biyu cur.
In ban da sharar hawaye ba abin da Lailah da Mominta ke yi. Daga baya shi ma sai ya rungume 'yar uwarshi ya fashe da kuka.
Suka yi kukan su mai isar su, kamin da Isma'il ya fiddo waya ya kira Mohammed, wanda already ya yi aure.
Hakan bai hana shi tsallake aiyukan gabansa ba ya yi landing a Egypt. Suka tsaya cirko-cirko shi da Lailah sai kallon-kallo, the one that is always hunting his dream….

A hankali jama'ar dake katon falon suka shiga zamewa, ya zamo daga Lailah sai Mohammad dinta, wadanda suka yi cirko-cirko suka ci gaba da kallon juna kamar yau suka fara ganin juna.
Tsohuwar soyayya ta motsawa Mohammed, ya mika hannu ya kamo hannun Lailah, sannu a hankali ya hadata da jikinsa ya kankame ta ya rungume, a hankali ya kama sakin wata irin sassanyar ajiyar zuciya.
Wasu irin dumammun hawaye suke kwaranyo daga idanuwan Lailah, hawayen da ita kanta ba ta san ko na mene ne ba, na nadama ne? Na tunanin gurvataccen auren ta ne? Ko ko na tunanin da wane harshe, da wace fuska za ta fuskanci Mohammed?
A hankali ta soma zamewa daga jikinsa, ta durkushe a kasa kan gwiwoyinta ta soma girzar kuka mai cin rai.
Shi ma binta ya yi ya zauna dirshan a gabanta, ya ce,
"Lailah duk kukan nan na mene ne? Kin tafi a bisa na yi miki laifi, ko ko don ni ba na haihuwa? Kin kuma yi tunanin dawowa wanda mun yi farin ciki da hakan.
Don haka ban ga me zai saki kuka ba, illa mu yi tunanin matsalolinmu da neman hanyar warwaresu domin cimma rayuwa mai amfani.
Sai dai ban sani ba ko za ki iya ci gaba da zama dani duk da rashin haihuwata ko a'a?"
Ta yi saurin cira kai ta dube shi, cikin muryar kuka ta ce,
"Ban tava tunanin in guje ka ba wai don ba mu haihu ba, illa don hujjoji nan da na ambata maka cikin wasikar da na bar maka.
Sannan ni din wata mai babban laifi ce a gare ka da Ubangijina. Sai dai nima ban san me ya kai ni ga aikatawa ba. Amma ina da tabbacin cewa na yi tsarkakakken tuba wanda Allah (S.W.T) ya yi alkawarin karvar sa, wato tuba da tabbacin ba za a sake komawa izuwa zunubin ba".
A hankali ya ce,
"Laifin me kika yi min Lailah? Gaya min komin girmansa......."
Ta mike daga jikinshi ta ba shi baya, ta isa ga taga tana kallon harabar gidansu inda ruwan

sama ke sauka a kan korran ciyayin da suka yi wa gidan kawanya.
Ta vata shiru na lokaci mai tsawo, tana hango girman laifinta, hoton ranar da ta kira “bakar rana” na gilmawa a idanunta.
Hawayen idanunta na tsiyaya duk da ta amince da tubanta. Ganin ba ta da niyyar cewa komi, ya kara taku ya isa bayanta, ya dora hannu a hankali bisa kafadunta.
Ta juyo suka yi ‘facing’ juna idanunta sharkaf da hawaye, kafin ta mika hannu ta share su, sannan cikin karyayyar murya ta ce.
“Za ka iya yafe min idan na fada maka cewa har haihuwa na yi da Sa’eed?”
Idandunan shi ne suka yo waje tamkar an busa masu barkono, ya kasa furta komai, kai kamar ma bai ji dai-dai ba.
Ta share ambaliyar hawayen da suka shimfido mata ta ce,
“Aure tsakanina da kai ya haramta Mohammed.... shaidan ya rinjaye mu mun aikata cin amana a gare ka.
Ni kaina ban san ya aka yi ba, sai da mai afkuwa ta afku. Ina cikin kunyar ka, ina cikin kunyar Mahaliccina………
Ka yi afuwa a gare ni Mohammed, ko na samu sassauci wurin Ubangijina.
Na tafi domin ina ganin zaman nawa ba shi da amfani, aurenmu ya riga ya gurvata, na yi asara kuma na ci amanarka, duk da kai ma kana da naka kamashon.
Tun da an tambayi Manzon Allah (S.A.W) cewa, “Kwana nawa ne mace mai aure za ta iya yi ba tare da namiji ba?”
Ya ce, “Kwanaki arba’in”. To ni casa’in nake yi ban ganka ba.
Sai ya nuna shi yana da lokaci na, yana kula dani tamkar matarsa, yana kyautata min tare da bin duk wata hanya don ya sama min farin ciki.
Sannan ka dauko baligi ka hada da matarka wacce ke cikin shekaru na kuruciya,  alhalin kai din baka nan. Ta ya ya varna ba za ta faru ba......?”

Tun da ta soma magana bai yi magana ba binta yake da ido, da zuciya. Jin al’amarin yake kamar almara ko mafarki.
Idan ma Lailah ta kullawa dan uwanshi wannan sharrin ne don ta rabu da shi, wanda tuni ya fahimci take-taken ta kenan, ko don ta hada shi da marayan dan uwansa da baya da ya shi a duniya, to, ta yi karya, ta kuma yaudari kanta”.
Ta dai tafi ta yi gantalinta ta yi shegenta, ba zai tava yarda da wannan tozarci ga dan uwansa ba.
Ya daga rinannun idanun shi da suka kada suka yi jawur suka kankance ya ce,
“LAILAH!”
Dagowa ta yi a hankali ta dube shi, har yanzu kuka take.
Ya ce,
“Mece ce hujjah? Ko shaidar da zan yarda da ke, wadda shari’a za ta yarda da shi ta gurvata/haramta auren namu?”
A mamakance ta dube shi, wato duk irin bayanin da ta yi mishi bai yarda da ita ba. Ta ce, “Na dubi Allah ne na fallasa maka sirrina da yake voye.
Wanda babu wanda ya sani daga ni sai dan uwanka, don in samu afuwa da yafiyar ka ko na samu saukin hukuncin da Ubangiji zai yi min idan na ha’ince ka muka ci gaba da zaman

ZINA....”
Tare ta ya yi.......
“ZINA? Ai kin je kin yi abarki, wannan ke da Ubangijinki. Amma AURE NA yana nan ba abin da ya same shi, ba kuma wanda ya isa ya sheganta min shi tun da ban gani ba.
Wace mace mai mutumci ce za ta tafi turai tsayin shekaru biyu ba tare da muharraminta ba, ta ce wai wani wanda ke Najeriya ne uban shegen nata?
Kin ganni nan duk son da nake yi wa mace ba ta isa ta tozarta ‘yan uwana in kyale ta ba. Don haka ki nemo uban shegen ki a inda kika baro shi, ba cikin zuri’ata ba”.
Lailah ta soma hasala, zuciya ta harzuko ta.
Ta ce,
“To me ya yi zafi Mohammed? Ka yar da kwallon mangwaro ka huta da kuda mana?”
Ya yi mata wani irin kallo wanda ta kasa fassarawa, domin kallo ne na kiyayya da rashin kauna, wanda ba ta tava gani cikin kwayar idanunshi ba.
Ya yi wani irin miskilin murmushi ya ce.
“Ai hakan kike so. Na kuma ramfo ki yarinya. Sai ki sake dabara wadda kowa zai yarda dake ba sai kin tozarta dan uwana ba. Don hakan ba karamar illa ba ce ga mutuncinki a idon duniya. Aurenmu babu rabuwa.
Ba shege daya ba, ko dari ne zan karve su tunda ni musulunci ya baiwa. Don haka ki shirya gobe mu wuce gida kawai cikin mutuncin ki.
Na yi alkawarin ba mai jin wannan katovarar taki daga bakina, sai idan ke kika sake furtawa. Zan yi kokarin in gyara kuskurena kamar yadda kike so Lailah. Amma wannan magana, ki barta.
Ki yi haka ki binne ta tunda baki da hujja ko shaida ko kotu ba za ta karve ta ba.......”
Ta katse shi,
“Allah shine shaida ta, kuma ba zan yi zama na zina ba. Da din ma soyayya ta rufe min ido nake zaune da kai Mohd. Kana kwara ta, nake jure bakin cikinka har na kai kaina ga halaka.
Ba don Ubangijina ya yi gaggawar farkar dani ba, na san da har yanzu ina cikin halaka. Ka tambayi duk malaman da ka sani.... babu aure tsakanina da kai, tunda na kwanta da shakikinka, alhalin kana raye.
Mohammed na soka, na soka da zuciya daya, kuma har gobe ina sonka, ba zan iya komawa aurenka ba muddin ina cikin hankalina.
Amma tun da ka ce sharri na yi wa Sa’eed, to muje a hakan, wata rana gaskiya za ta yi halinta.....”
Da sauri ya katse ta,
“Ban sake ki ba Lailah.....ki kwana da sanin wannan. Ba kuma zan tava yin hakan ba, in dai sunana “Mohammad!”.
Don haka na baki kwanaki uku ki yanke mai fissheki, za ki bini mu koma ne, koko zan ji sammaci daga kotu........?”
Fuuu! Ya fita ya banko kofar har sai da Lailah ta razana, mamaki kam yau ta sha shi kamar ya kashe ta, ta yadda mutum mai ilimi kamar Mohammed ya mai da kanshi katoton jahili cikin addini, saboda soyayya da ta rufe mishi ido.
Ta dade tana sake-sake ita kadai, ko dai ita ma ta bar maganar ne kamar yadda ya ce a barta ba tare da ta tozarta kanta ba?

Idan ta ce kotu za ta kai shi a kwatar mata sakin aure kanta za ta tozarta. Duniya ta ji abin da WASA DA KANIN MIJI ya janyo mata.
Asirinta ya bankadu har Momi da sauran 'yan uwanta su ji, ta kuma san har 'ya'ya da jikoki ta barma kanta abin gori.
Abu mafi a'ala dai shine a bar maganar, amma kuwa idan ta ci gaba da zaman auren da Mohammed din da har gobe zuciya ba ta hutawa da kaunar sa, zaman ZINA, tana sane, wane hukunci Allah zai yi mata?
Ta fashe da kuka sosai tana yi a hankali kada wani ya jiyo ta, kuka mai cin rai da soya zuciya.
Ta yi tunanin bari kawai ta je ta nemi shawarar Abbas a dakin baki, domin kuwa shi babba ne da ya fi ta kaifin hankali da kaifin tunani.
Sannan shi ne mutum na farko da idan ta bi shawarar shi take ganin alfanunta. Bata nadama a cikin duk shawarwarin da yake bata.
Ta fada toilet ta wanke fuskarta da sabulu, ta sauya abayar da ke jikinta ta murda kofar ta fito.
A babban falo su Momi ne da su Najat sun yi shimfidar leda suna cin abincin dare, sai lokacin ne ma ta tuna rabon ta da abinci tun na daren shekaranjiya.
Amma wannan ba shine a gabanta ba, fita ta yi harabar gidan ta doshi dakin baki. Ta yi sallama har sau hudu ba' a amsa ba, sai ta murda kyauren ta shiga.
Babu Abbas babu ko jakar kayan shi. A kidime ta dawo falon tana tambayar Isma'il ina Abbas? Hannu ya tura cikin aljihu ya fiddo ambulan fara tas ya mika mata. Ya kara da cewa.
"Ai tun zuwan Mohammed, da na gaya mishi shine mijinki ya tafi. Ya ce 4 o'clock flight zai bi zuwa London.
Dama burinsa shine ya rako ki ya kawo ki gida, sauran bayanan za ki ji a cikin wasikar".
Cikin sanyin jiki da kasala ta mika hannu ta karvi ambulan din.
Sanah ta cika plate da shawarmah ta mika mata, hannunta har rawa yake saboda yunwa. Ga wata kewa da ta lulluve zuciyarta, irin wadda ta dade bata ji ba a rayuwarta, tun bayan rashin mahaifinta.
Abbas wani mutum ne mai muhimmanci da kima a gare ta da ba za ta tava mantawa da shi ba. Hanya ce ta hada su, amma tana jin shi da wani muhimmin matsayi a zuciyarta da ba za ta iya tantance wanne irin, matsayi ne ba.
Ga dai mahaifiya ga 'yan uwanta, ga kanne da yayye musamman Isma'il wanda a yanzu yake matsayin tamkar mahaifi a gare su, amma jin ta take kamar ita kadai ta rage a duk fadin duniyar.
Haka nan take caccakar abincin ba don dadi ko dadin rai ba, illa don ta faranta wa 'yan uwanta da mahaifiyarsu da suka zubo mata ido don ganin sauyawar da jiki da fuskarta suka yi da jin cewa bakon ta ya tafi.
Ba ma kamar Isma'il dake kare mata kallo cikin nazari. Gaba daya ta susuce ta zama kamar wata firgitacciya.
Tun dawowar ta ya fahimci da abin da ke damun ta, tana kokarin voyewa. Ganin cewa juriyarta ta kare kada ta fashe da kuka a gaban su, sai ta aje cokalin a hankali ta mike ta yi dakinta.
Isma'il da Momi Najla suka bi ta da idanu masu cike da damuwa.
Ba ta bude wasikar Abbas ba sai da ta yi sallar isha'i, ta kara da shafa'i da wutri. Ta daga hannuwanta sama tana hawaye tana rokon Allah ya yafe mata, ya kawo masalaha cikin rikitacciyar  rayuwarta.

Sannan ne ta bude wasikar Abbas, ga abin da ke rubuce:

LAILAH!
Haduwar kan hanya ce ta zamo haduwar zuciya...aminci, kyautayi da abota ne suka hadu suka yi gingimemen gini a zuciya..., wanda hakan ya janyo zuciyar ta ke so, amma baki ya gaza furtawa.....
Sai dai kuma sau tari fuska kan gaza boye zahirin abin da ke zuciya…… domin zuciyar na ragaita, a rashin sani na ashe bani da 'yancin wannan al'amarin....
Don haka na wuce London, a duk lokacin da kika tuna ni Lailah..... ki sanya ni cikin kyawawan addu'o'inki. Ina yi miki fatan ALHERI.....

Ta dade tana maimaita wasikar Abbas, amma ta kasa fahimtar ta, ta karanta ya fi sau hamsin amma ba ta fahimci sakon da yake son isarwa gare ta ba.
Wane al'amari ne ba shi da 'yancinsa? Zuciyarta ta halarto mata da amsoshi da dama, ciki kuwa har da mai cewa.
"BA SHI DA 'YANCIN AURENKI TUNDA KE MATAR AURE CE......!"
Sai ta kwantar da kanta a kan dardumarta, tana hawaye. Abbas shine irin mijin da take so, take fata, take kuma addu'a, Allah Ya bata, miji wanda ya san hakkokinta, ya ke wanzar da lokacin shi da hidimomin rayuwar shi wajen kulawa da mace. Yake ririta ta tare da tattalin ta. Sai ta samu kanta da kewar Abbas, kewa mai yawa kuwa.
Yayin da daya vangaren na zuciyarta ya ki kewar Mohammed Jama'are, wanda ke son su koma su yi zaman zina, da son ranta ko babu.
Ta alkawartawa ranta da dai ta komawa auran Mohammed, gara ta karasa rayuwarta babu aure, don ba ta ga so da kauna da aminci a cikin shi ba.
A wani vangaren kuma idan ta ki Mohammed shi Abbas a ina za ta nemo shi? Ya ga mijinta ya dawo ya yi tafiyarsa ba tare da ya yi mata sallama ba, balle su fuskanci juna su shawarta mafita ga rayuwarsu.
Ina za ta nemo shi? Kano da girma, ina za ta nemo shi ba ta san komi a kan garin da yake ba balle mazauninsa....
Ta kifa kanta cikin tafukanta ta soma kuka mai cin rai, kuka irin wanda ta dade ba ta yi a rayuwarta ba. Kukan sabo, soyayya da kewa, soyayya mai laushi da taushi, da ba ta tava tsintar kanta a ciki ba.
Daga karshe barci ya sace ta cike da mafarkai barkatai marasa kan gado, duk a kan Mohammed da Abbas.
Don haka da kyar ta samu ta yi sallar asuba a kurarren lokaci. Ta koma ta kwanta, ba ita ta tashi ba sai karfe goma na safe da Momi ta kwankwasa mata kofa.
Ta yi mika ta yi salati sannan ta zo ta bude kofar.
Kallo daya Momi ta yi mata ta ga fuskarta a kumbure, idanunta sun yi luhu-luhu sun yi jawur. Ta kama hannunta, har bakin gadonta sannan ta rungume ta. Ajiyar zuciya mai nauyi ta suvucewa Lailah.
Hawayenta suka kwaranyo a bayan mahaifiyarta, ta yi kukan ta ma'ishi, Momi Najla ba ta dakatar da ita ba.
Ta tabbatar akwai abin da ke damun diyarta wanda zurfin ciki irin nata ba zai bari ta bude baki

ta fada ba.
Ta kai hannu tana shafar bayanta tana lallashin ta. Ta ce.
“Idan baki gaya min abin da ke damun ki ba Lailah wa za ki gaya mawa? Ni mahaifiyarki ce, da ta tsuguna ta haife ki, nice farko da ya kamata in san damuwar ki, in yi kokarin da zan iya in warware miki ita.
Jiya na ga Mohammed ya fito cikin fushi, sannan tun da aka gaya miki tafiyar wanda kuka zo tare kin kasa ko cin abinci. Kar dai ki ce dani aure kika yi a kan aure Lailah?”
Magana take cikin sanyi, da zuciya irin ta UWA, sannan ta kakkafe ta da idanu. Lailah na girgiza kai tana cewa.
“Lala-lala Ummi......”
A hankali ta soma zayyana mata komai. Ta kare da cewa.
“Kwanaki uku kacal ya bani in bishi mu koma a bar maganar, ko in kai shi kotu in kwaci takardar saki.
Duk yadda na so in nusar da shi rashin ingancin aurenmu ya ki sauraro na. Har yana zargina da yiwa kaninshi sharri. Ummi ina cikin wani hali na kuncin zuciya da rashin yarda da kaina......
Me zan yi Ubangijina ya yafe mani ya kawo mani maslaha cikin rayuwa ta? WASAN KANIN MIJI bai kare ni da komai ba sai jefa ni a halaka da wanzar dani cikin bakin ciki da nadama....”
Ta ci gaba da kuka a kan cinyoyin mahaifiyarta.
Momi ta rasa abin cewa, sai LA’ILAHA ILLALLAHU….. Allah ya kawo mu wani zamani gurvatacce..... zina ta zama ba komai ba, daga wajen marasa auren da masu auren ma.

Ba ta tava jin irin wannan kwamacalar a cikin aure ba, sai dai al’amarin da ya riga ya faru ba abin da za a iya yi a kai sai dai ayi kokarin gyarawa, don a guji gaba.
Ta dago fuskar Lailah daga cikin cinyoyinta ta ce.
“Kema kina da laifi Lailah, me ya sa a lokacin da ya bijiro miki da bukatarsa baki yi wani kokari na kare kanki ba?
Me ya sa kika zavi yin nisa damu fiye da ki gaya mana a yiwa tufkar hanci? Ayi abin da ya dace tun a lokacin?
Laifuffukan ki suna da yawa Lailah. Kin tafi zuwa wata duniya ba tare da yardar mijin da ke auren ki ba, kin kulla alaka da wani da namiji da ba muharramin ki ba. Me zai hana soyayya ba za ta gitta a tsakani ba? Da aurenki Lailah?”
Lailah dai ba baki sai kuka. Ta yarda ita ma da laifinta. Ta kama hannun Momin ta rike cikin nata.
Cikin rishin kuka ta ce,
“Na yarda nima ina da laifi Momi.....sai dai na tuba, na dade ina tuba ga Ubangijina.....tuba irin wanda Ubangiji ya yi alkawarin karbar sa.... wato tuban da aka tabbatar ba za a sake komawa izuwa zunubin ba”.
Sai Momi ta rungume ta,
“To yanzu me kike so da rayuwarki? Kin shirya zama mutuniyar kirki ko za ki ci gaba da yin alakar kusanci da mazan da ba muharramanki ba?”
Ta yi saurin katse Momi da cewa,
“Na shirya zama ‘yar kirki Momi a gaba dayan sauran rayuwata......”
Momi ta ce,

“Aurenki da Mohammed ya riga ya lalace, sai dai dukkaninku ku yi hakuri da shi.
Maganar zuwa kotu domin karvar takarda a hannun Mohd. ma ba ta taso ba. Domin kanki za ki tozarta. Za mu nemi sulhu da shi, jibin zan ganku tare. Amma ki yi dauriya, dole Isma’il ya ji zancen nan, don shine waliyyinki.....”
Lailah ta zaro ido,
“Zai tsane ni Momi, zai yi Allah wadai dani Momi”.
Ta ce,
“Shirmen banza kenan, an ce da ke hannunka na rubewa ka yanke ka yar ne? Baki yi tunanin hakan ba a lokacin da kike hutawar haram da kanin mijinki? Tashi ki bani wuri tun nima din ban tsane ki ba”.
Mikewa ta yi tana goge hawayen idanunta. Ta shiga ‘toilet’ ta sakar ma kanta ‘shower’ ko ta ji sanyi a zuciyarta.

****
[12/17/2019, 18:28] Takori: An zauna a falon marigayi mahaifin su Lailah a ranar (26) ga watan Maris na shekarar 2000.
A gefen Mohammed Jama’are kanin shi ne Sa’eed Jama’are, wanda tun da ya shigo falon kanshi ke sunkuye bai dago ba.
Sai Isma’il Yayan Lailah, kusa da shi Lailah ce cikin abayat da Momi a gefenta. Sai Hajiyar su Mohammad a gefe wadda fuskarta babu alamun rahma, kada ma su ce sulhun a mayar da Lailah gidan danta za’a yi, don a cewar ta Lailah karuwanci ta tafi Turai ba wani karatu ba.
To sai kuma kallo ya koma sama, a inda ta ji sulhun da Balarabiya Najla ta nema, wato a warware auren Lailah da dan nata sakamakon kazantar da auren da suka yi da WASAN KANIN MIJI.
Ta dube su tsaf, a ranta ta ce ‘yan kundun uba.
Sannan ta mike ta bugi kirjinta ta dubi Momi ta ce, “Ni Baida’u ban haifi dan iska ba, ‘ya’yan nan biyu su Allah ya bani ban taba ji an ce an gansu suna aikata wani aiki na assha ba.
Balle Sa’idu ya nemi matar Yayansa da yake mutuntawa fiye da ni, yake kaunarta da zuciya daya.
Ta je can ta nemi abokin shaidancin can a inda ta je karuwanci....Takarda kuwa ko baku ce ba dama za a ba ta, don tuni na aurawa dana mace ‘yar usli wadda na san asalinta. Don haka.......”
“A’a, Hajiya ki yi hakuri ki zauna ayi maganar nan a tsanake..........” Sa’eed wanda ke sunkuye da kai ya fadi cikin sanyin murya....
Ya kara da cewa,
“Don Allah Hajiya ki zauna....”
Ta koma ta zauna tana hararar sa..... Shi kuwa Mohammed jifanshi ya yi da wani kallo mai tarin ma’anoni da dama.
Amma Sa’eed ya maida kanshi kasa, ba tare da ya sake hada ido da kowannen su ba ya ce.
“Hajiya da Yaya ku gafarce ni, tabbas abin da Lailah ta fada cewa mun aikata gaske ne. Mun tava kusantar juna amma sau daya ne cikin ribatar shaidan.
Zancen haihuwa ne ban san da shi ba, don ina jin tun a ranar da al’amarin ya faru ta bar gidan, nima ban kara ganinta ba ko ji daga gare ta ba sai yau.
Don haka Yaya ka yi hakuri, ka kuma yi min duk hukuncin da ka so.......kasancewa ta wanda ya

yi maka cin amanar da baka tava zato ba, na raba ka da abin da kake so, ba don ka daina son shi ba.
Yaya daga ni har Lailah ta wani vangaran bamu da laifi, ko me muka yi kai ka bamu damar mu yi shi.....”
Kafin ya karasa Mohammed ya kai masa wani wawan mari, ya bishi ya shake da kyar Isma’il ya kwace shi. Ya galabaita yana haki abin tausayi.
Hajiya ta ce,
“Rufe min baki tun ban tsine maka ba, kai kuma Mamman rubuta takardar sakin ka basu idan ka haifu cikin iyayenka......rubuta musu yanzun nan ka bani, ko in daga maka nono wallahi…….”.
Ya sunkuyar da kai hawaye fal idonsa. Isma’il ya bashi biro da takarda.
Yana rubutun hawaye na jika takardar, ya rubuta saki daya jallin-jal, ya mikawa Isma’il, ba tare da ya damu ya goge hawayen da ke zuba tarara daga idanunshi ba.
Cikin macewar jiki Lailah ta daga ido ta dube shi, anyi sa’a a lokacin shi ma ya dago sashen da take. Sai ta ji hawaye sun tsinke mata na tausayin Mohammed, tsohowar soyayyar dake zuciyarta ta motsa. Da gudu ta bar falon ta yi cikin gidansu ta fada bisa gadon Momi tana kuka, mai fita daga karkashin zuciya.

****

Kwata-kwata rayuwar Lailah ta sauya, domin duk inda macen da ta san ciwon kanta take, wannan kalmar ta ‘saki’ ba karamin tashin hankali bane a gare ta, ko da auren kiyayya ne kuwa, balle auren da aka gina a kan turbar so da kauna.
Gaba daya ta susuce ta fita hayyacinta, tsakaninta da mahaifiyarta sai gaisuwa, don tun ranar da su Mohammad suka daga gida Najeriya ba ta kara ganin hakorin Momi Najla ba.
Ta ce sai ranar da ta ganta a dakin aure, sun daina jera kafada, sannan ita dai ba ta tava ZINA a tsayin rayuwar ‘yammatancin ta ba, balle da auren ta.
Isma’il ko kallon ta ba ya yi balle ta ga hakoransa. Duniyar ta yi mata kunci ta buwaye ta. A wajen kannenta su Najat kawai take jin sanyi, wadanda basa rabo da dakinta suna yi mata hira, suna wasanninsu.
Aka kwashe sati biyu a haka, rama da zugewa da take yi suka addabi zuciyar Momi Najla.
Ta soma tunanin Allah ya sa ba kanjamau ta je ta debo a kanin mijin nata ba. Don haka yau da safe Momi ta sanya ta a gaba suka nufi asibiti.
Laila na jin sanda Momi ke ce da likitan ta kawo ta a yi mata gwajin kanjamau ne. Sai hankalinta ya kara tashi.
Ko numfashi da kyar ta shake shi. Wai me kowa ya dauke ta ne? Karuwa ko me?
(Kadan kenan daga irin bakin cikin da ‘ZINA’ ke haifarwa, domin ita ce karshen tozarci a rayuwa, musamman ga diya mace).
Ba ta shaki numfashi sosai ba sai da result ya iske su cewa Lailah lafiyarta kalau.
Lailah ta kasa jure mu’amalar doya da manjan da Momi da Isma’il ke mata, don haka ta soma tunanin kirkirarwa kanta abin da zai amfane ta.
Da farko ta soma neman aikin koyarwa a jami’ar da ta yi, ba ta sha wahalar samun aikin ba, musamman saboda ingancin masters  dinta na Ingila.
Ta shigo gida rike da tulin takardu a hannunta da gani a masifar gajiye take. Sanah da Najat

suka garzayo suka rungume ta.
Ta russuna dai-dai tsahonsu ta rungume su ta sumbace su daya bayan daya, ta tambaye su ina Momi? Suka nuna mata dakinta.
Ita da Isma'il ta samu suna magana da kasafce-kasafcen tulin kudi a gabansu. Ko dai na business dinsu ne ko na mene ne ba za ta ce ba. Domin Isma'il babban dan kasuwa ne. Ya kan je Dubai da America kawo kaya kasar Egypt, sam-sam ya ki aikin gwamnati, duk da kwalayensa na karatu masu inganci.
Nan da nan dukkaninsu suka yi fuska suka daina zancen da suke, suka bi ta da kallo kamar sun ga wata bakuwa.
A savule kuma kamar ta yi kuka ta zauna a gabansu, ta aje takardunta a gefe. Kadan ya rage ta fashe da kuka.
Wai Momin ta da Isma'il ke nuna mata yau ita bare ce a cikinsu, don kurum ta yi kuskure a rayuwarta?
Ta kai bayan hannunta tana share hawaye ta kasa cewa komai. Zuciyar UWA ta soma russuna, amma Isma'il sai ya hau fada.
"Lafiya za ki zo ki sa mutane a gaba kina yi musu kuka kamar su suka saki kije ki zama 'yar iska ki ci amanar aure?"
Sai ta idasa rushewa da kukanta, ta ce,
"Na tuba Momi, na tuba na bi Allah na biku. Isma'il wane ne ba ya kuskure a rayuwarsa? Idan kun juya min baya ina za ni? Idan kun watsar dani wane ne zai tallafe ni? Dan uwana ka yi min aikin gafara kamar yadda nake nema a wurin wanda na yi wa laifin amma ba kai ba".
Ya yi tsaki ya soma tattara kudin yana zubawa a jaka, ya ce da Momi
"Idan za su tafi kaiwa sai a gaya mani in raka su".
Momi ta ce, "Babu laifi". Ya sa kai ya yi ficewar sa.
Lailah wadda ke durkushe har zuwa lokacin a gabansu ba ta daina shesshekar kuka ba, kukan da ya tava zuciyar Momin, ko ta ki Allah.
Ta mika hannu ta kama tattausan tafin hannunta ta ce,
"Ya isa.......ya isa". Tana goge mata idanu da gefen abayarta.
Da kyar ta tsaida kukan ta jawo 'file' din dake gabanta ta ciro takardar daukar aikin ta mika mata.
Momi ta sanya gilashinta tana dubawa, ta mika mata ta ce,
"Masha-Allah, yaushe za ki fara zuwa?"
Ta ce, "Sati mai zuwa".
Ta ce, "Ga shi kuma za a yi auren Isma'il sati mai zuwan".
Ta ce, "Wa zai aura?"
Ta ce, "Sujood".
Sai Lailah ta vangale baki tana dariyar farin ciki.

Sujood diyar Yayar mominsu ce, tare suka taso da Lailan tun suna kanana. Ba za ta ce Sujood kawarta ce ba, don ita ba ta kawance, to amma 'yar uwarta ce da suka san juna suka fahimci juna.
Sai da suka zo shiga jami'a ne suka rabu, inda Sujood ta tafi kasar 'Syria' ta yi karatu a kan likitanci, Lailah kuma ta yi a nan Al-Azhar din Alkahirah.

Biki sosai suka yi irin na al'adarsu, Lailah na kan gaba a kan komi. Aka kawo Sujood nan gidan su part din Isma'il, kasancewar gidansu katon gaske, mai sassa daban-daban.
Lailah ta shirya sassan sosai kai ka ce fadar wani gwamna ne kasancewar a al'adarsu miji shi yake yin komai na kayan daki.
Musamman suka fita Oman don sayayyar kayan da za a zuba a gidan ita da Momi. Ganin irin rawar jiki da wahalar da Lailah ta sha a shagalin auren sa ya sa ya soma sakar mata.
Amma ko an gode bai ce mata ba, duk da ya lura sayayyar da a kai ta zarta ta kudin da ya bayar.
Ita kanta amarya Sujood ta lura da basar da Lailah da Isma'il ke yi a 'yan kwanakin da ta yi a gidan, amma ta ja bakinta ta yi shiru don ba ma'abociyar magana ba ce.
Bayan bikin ne Lailah ta mayar da hankali a kan aikinta. Wata rana idan ta fita tun takwas sai shida na yamma.
A karshen sati ne kawai take zaman gidan, kuma zuwa lokacin Isma'il ya saki ranshi da ita. Ya yarda ba wai sai mutum yana dan iska bane kawai yake yin iskanci ba, a'ah, dan kirki ma kaddara da yanayin rayuwa kan kai shi da aikata laifi, ko ba da son ran shi ba.
Sai dai mu yi ta addu'a Allah ya sa mu fi karfin zuciyoyinmu. Ya raba mu da son zuciya, ya nisanta mu da kaidin shaidan. Amin.
***
ko da jirgi ya sauke su Sa'eed da Hajiyarsa a garin Bauchi, basu kara ganin Mohd ba. Shi Sa'eed ne ya yi masu shatar mota suka nufo Jama'are, don ya lura a yadda Yayan ke tunzure da shi in aka ba shi wuka zai iya burma masa. Haka in yana da bindiga zai iya harbe shi har lahira. Don haka salin-alin ya wuce Jama'are shi da Hajiya.

Mohd. yana kwance a sofa na falon gidan shi yana busa hayakin 'Marlboro', idanunshi a rufe. Tiryan-tiryan yake tariyo rayuwarshi da Lailah, tun haduwarsu a babban filin jirgin saman Egypt, sun rako mahaifinsu zai tashi zuwa Nijeriya.
Ya tuno gwagwarmayar da ya sha wajen neman auren ta, domin Hajiyarshi sam ta ki amincewa, don a cewar ta ba ta son kwashe-kwashe da rore-rore.
Marigayi mahaifinshi shi ya tsaya mishi tsayin daka ya samu abin da ransa da zuciyarshi ke so. Ya tuno irin soyayyar da suka gudanar a kwanakin amarcinsu. Wanda har gobe ba a samu macen da yake so ya kuma ke kauna ya amincewa irin Lailah ba.
Ya kuma tuna cewa, tun daga wancan lokacin Lailah ba ta kara yin zaman farin ciki a gidansa ba. Ta yi hakuri har ya kure ta domin ba shi da lokacin ta.
Idan har za a auna ne a mizani, to alhakin koma me Lailah da Sa'eed suka yi, to yana wuyansa. Kuma nashi laifin zai rinjaya. Bai san yana son Lailah ba sai yau da ta kuvuce masa, zuciya ta kuma tunkudo shi ta ce ya je ya dan huce a kan Sa'eed kawai ko ya rage asara.
Daga baya kuma ya ce,
"To don na daki Sa'eed me na yi? Yaro mai tsoron Allah da harshe daya, dukan da ba zai rage komi daga suyar da zuciyarshi ke yi ba.
Ya tabbatar ya yi rashi tun da ya yi saken da ya rasa Lailah, mai kyautayi da hakuri da tausasawa a gare shi.
Ko daya ba za a hada Lailah da Aisha ba. Ta fannin komai, shi dai kawai ya karvi aurenta ne don ya faranta ran Hajiya.

Amma soyayyarta gaba daya in za a dora ta a sikeli ba ta wuce cikin cokali ba. Ai gaba da gabanta... wai aljani ya taka wuta.
Me zai yi ya huce abin da Sa'eed ya yi masa? Babu, ya riga ya cuce shi. In ma kotu ya kai shi karshe ma watakila shi zai je belinsa.
Idan ya doke shi bai huce ba, idan ya yi masa Allah Ya isa, idan alhaki ya lalata shi komai a kansa zai kare.....
Bai ankara ba ya ji wata irin azaba a 'yan yatsunsa, tuni tabar ta kare har ta soma cin yatsun hannunsa.
Ya jefata 'ash tray' na silver dake gabansa ya bude idon shi sakamakon tsayuwar mutum da ya ji a kanshi. A'isha ce.....
Ta ce,
"Majnoon na Lailah......!
Za ka iya tashi mu yi 'break' din ne ko Misra za ka koma a baka, tunda bikon bai yuwu ba?"
Ya valla mata harara ya ce,
"Idan komawar zan yi za ki iya hanawa ne?"
Ta kyave baki ta ce,
"A'a, ko bani da abin yi ba abin da zai kai ni inda ba'a so na....."
Ji kake fauu! Ya wanke mata fuska da yatsunshi biyar...har sai da ta ga wuta da taurari. Ta kama kuncinta duka biyu ta sunkuya tana neman kwayar idanunta da ta neme su ta rasa na wucin gadi.
Da kyar ta ce, "Ni ka mara daga magana Mohd.?"
Ya yi tsaki ya yi ball da 'center – table' din gabansa na gilashi tsantsa, a take ya ragargaje. Ya yi sama fuuu! Kamar zai bi ta kanta, ta yi kwafa ta mike ta ce.
"Wallahi ka mari auren ka".
Ta yi dakinta tana kuka tana hada kaya. Azahar a Jama'are ta yi mata, ba ta nufi gidan Hajiya ba don ba sulhu take nema ba, gidan iyayenta ta nufa.
Kwananta biyu Hajiya ba ta san ta zo ba, sai mahaifinta ne Malam Adamu ya zo yake gayawa Hajiyar yadda aka yi.
Hajiya ta girgiza kai ta ba shi hakuri, ta ce, "Za ta dau mataki ita ma zata yarda da komai amma banda duka. Amma ya yi hakuri ya turo mata A'ishar ta zauna a wurin ta kafin ta kira shi".
Malam Adamu ya gyara zama ya ce, "Hajiya idan Muhammadu baya son auren nan ina ganin gara a raba shi cikin mutunci ba tare da zumunci ya lalace ba.
Don ta fadi abubuwa da yawa, wadanda abin dubawa ne a cikin aure. Ta ce sai ta yi watanni uku ba ta ganshi ba, kuma bai neme ta a waya ba.
Sannan in zai tafi ba ta isa ya yi mata sallama ba, sai dai ta ga kudi a kan tebur, haka in zai dawo. Allah ya ga zuciyata ba don kudi na wanke A'isha na ba wa Mohammadu ba, sai zumunci da mutuncin da ke tsakani".
Hajiya kamar ta yi kuka, ta ce,
"Don Allah ya ba ta lokaci ta kira shi, in Allah Ya yarda za ta tsawatar".
Kwana uku kenan Hajiya na buga layinshi ana gaya mata a rufe yake. A lokacin ma shi yana 'Bangkok'. Daga can ya wuce 'Austria' yana yi wa jirgin Virgin Atlantic lodi.

Sai da ya kwashe watanni uku cur sannan ya yo Bauchi. Bayan motarshi fal da tsarabar Hajiya

da Sa'eed din da ba shi da yadda zai yi da shi.
Hajiya na sallar walha ya daga asabarin dakinta kasancewar ana zabga sanyi, kamshin turarensa kawai da ta shaka ta san cewa shine.
Ya yi sallama ya shigo ya kwanta cikin kujera yana waya. Ba ta bi ta kansa ba sai da ta gama sallolinta da laziminta, sannan ta aje mayafi gefe ta juyo ta dube shi kawai ba ta ce da shi komai ba, don bakin cikin da yake shaka mata Allah ya yi yawa da shi.
Sai shine ya rufe wayar ya sauko kasa yana murmushi ya ce,
"Barkanku da safiya Hajiya, na same ku lafiya?'
Da da ne sanda yake yaro idan ya ba ta haushi irin haka carbinta za ta jawo ta tsutstsula masa, to yau ma tunanin da ta yi kenan.
Sai dai kuma da ta dubi girmansa da haibarsa hadi da kwarjinin da Allah yai masa, sai ta rasa ta ina za ta tsula mai carbin ya ji zafin shi a jikin shi?
Ko'ina guraye ne murdaddu na ingarman namiji, mai cikar halitta, ma'abocin haiba da kamala.
Sai birkitaccen hali da babu macen da za ta jure shi.
Dole ta aje carbinta a gefe ta dube shi cikin ido ta ce.
"Barka kadai".
Ko a kwalar rigarsa, don shi ya manta ma da wata A'isha, ya soma ba ta labarin irin tafiye-tafiyen da ya yi a wannan tafiyar.
Ta gaji da soki-burutsun da yake mata ta ce,
"Duk na ji, ka samo kudi ko?"
Ya ce,
"Sosai kuwa Hajiya, don na yanke ma can gidana na Bauchi za ki koma, ni zan koma Old G.R.A".
Ta jinjina kai ta ce,
"To iyali fa?"
Ya yi dan duru-duru na rashin sanin abin cewa, don shi tun lokacinda A'isha ta sha mari bai kara tuno ta ba ya ce,
"Tana can Bauchi, don kai tsaye nan na yiwo ban je gidan ba".
Haushi ya kashe bakin Hajiya Baida'u, ta rasa me za ta ce masa. Ta girgiza kai ta ce.
"Na tabbata ba haka kwarorin nan suka barka ba. Yanzu abin da kake yi wa aurenka ka kyauta kenan?
Baka ma san takamaiman inda matarka take ba. Ka kama 'yar mutane kuma 'yar uwarka da duka kamar jaka aka aura maka?
Tun da ka yi mata dukan ka haure ka yi tafiyar ka ba tare da ka damu da halin da take ciki ba, balle ka binciki lafiyarta, wai sunan tana matarka...."
Ya katse ta da cewa, "Ni fa Hajiya ban doke ta ba, marin ta kawai na yi da na ga za ta kawo min rashin kunya, wato zuwa ta yi ta ce na dake ta kenan?"
Hajiya ta ce, "Ungo naka...."
Ta yi masa umbola. "Wato marin ma kawai ne. Ka fada da bakinka ka doketan kenan. To sam ba zan lamunci wannan rashin hankalin ba, ka je can gidansu ka ba ta hakuri ka sa matarka a gaba ku tafi, kada na kara ji ko da tsinke ka tsikare ta dashi balle mari. Idan ba haka ba wallahi zan dauke ta, in ya so ka koma in da ba a san darajarka ba ka je can ku karata, ni kuma in fidda hannuna a kanka".

Ya sunkuyar da kai, “Duk me ya yi zafi Hajiya? Ki yi hakuri zan je in ga Baba Adamun, zan ba shi hakuri amma don Allah ki sa min albarka!”.
Ya ba ta tausayi matuka, Allah ya ba ta ‘ya’ya masu gudun zuciyarta, su biyu kacal amma kamar goma ta haifa. Zurfin ilimin zamaninsu bai sa sun kangare mata ba, komi ta ce ‘eh’ ne ko da bai yi masu ba.
Sai dai har yau ba ta kara tada zancen Sa’eed da Lailah ba, ga dukkan alamu ba ta son zancen kwata-kwata, duk da ta amincewa ranta gaskiya ne tun da har Sa’idun ya furta mata da bakinsa. Ya dai nemi gafararta ya kuma ce ta taya shi neman gafarar Ubangiji. In Allah ya yarda wani abu makamancin wannan ba zai kuma faruwa da shi ba, insha Allahu.
Ya sa aka fiddo jakunkunan da ya zo da su, sittiru ne dankare, ya ware na Sa’eed. Hajiya ta ji dadi sosai.
Sannan ya ce, “Sauran a rabawa dangi”.
Ta ce, “To, matarka fa?”
Ya ware wasu ya ce, “A kai gidansu ita zai ba ta nata daban”.  Bayan shi tun da ya tafi ma ko a mafarkan shi ba ta zo ba. Tunanin shi na LAILAH ne, sai dai ya ce Allah ya yaye masa.
Duk kawaicin Baba Adamu yau ya fitittike ya gwada masa shi ma yana son ‘yarsa. Bayan dogon kai ruwa rana da ban hakuri sannan da kafa sharudda sannan ya yarda ya kira A’ishan suka tafi, wadda ita kam kamar a kan kaya ta yi watanni ukun nan cike da nadamar fitowar ta, domin ta tabbatar kafin ta sake samun wannan daular da tsadadden miji irin nata a matsayi da ajin rayuwarta, abu ne mai matukar wuya. Ko ko a ce ba zai yiwu ba. Allah ne ya kashe ya ba ta, wautarta za ta kwace mata.
Don haka tun a mota ta soma zuba masa hira, tun yana share ta har ya biye mata. Suna yi wa Baba Adamu dariyar sharuddansa na duk ranar da ya kara dukan ta zagewa zai yi ya rama mata, don bai fi shi karfi ba.

****

Tun zuwa Sujood, Lailah ta samu abokiyar debe kewa, duk sanda ba ta da darasi tana sassan Sujood ko ita Sujood din na nasu vangaren. Ko su shiga gari idan Isma’il baya nan.
Cikin watanni biyar da suka biyo baya, account dinta ya yi nauyi, don ba ta tava komi cikin albashinta, Isma’il ya dauki nauyin rayuwarsu gaba daya.
Kuma Egypt ba kamar London ba, ba ta biyan kudin haya, gida ne nasu na kashin kansu. Duk da matsin tattalin arziki da kasar ke da shi wannan bai sa al’ummarta zama cikin talauci ba. Egypt kasa ce mai dadin zama da albarkar abinci, da suttura da wadatar ilimi, da kwararrun ma’aikata kiwon lafiya.
Kullum cikin kwanciyar hankali da wadata suke, ban da yanzu da suke fuskantar matsin Amurka. Sai dai damuwar Lailah daya (ABBAS) ina za ta nemo shi?
KANO da girma, kai ita duk zamanta a Najeriya ma ba ta tava zuwa Kano ba, ba ta san ina take ba.
Tana dai ji ana fada Kano-Kano a bakin Sa’eed da Mohammad, amma ba ta ma tava tambayar su wani sharhi a kai ba. Ta kuma gwada nambobinshi na Britain an gaya mata ba a amfani dasu sam.
“Watakila Allah ya rubuta iyaka haduwarmu kenan???”
Ta tambayi kanta cikin sanyin murya.

“Haduwar kan hanya ce ta zamo haduwar ZUCIYA…., aminci, kyautayi da abota ne suka hadu suka yi gingimemen gini a ZUCIYA. Wanda hakan ya janyo ZUCIYAR take so, amma baki ya gaza furtawa...... Saidai  sau tari fuska kan gaza boye zahirin abin da ke ZUCIYA, domin ZUCIYAR na ragaita....Sai dai kuma a rashin sani na ashe bani da ‘yancin wannan al’amarin………
Ta tuno kalaman wasikarsa.

Idan ta yi wa wadannan kalaman fassara ta hankali....Abbas na son ta! Sai dai AUREN da ta ke da shi ya zama shinge. Ta yi murmushi ita kadai, ta juya ta rungumi filo.
...... “Kana da ‘YANCIN Abbas, yanzu kana da ‘YANCIN, dukkanmu muna da ‘YANCIN. Allah ya hada fuskokinmu cikin gaggawa”.
Idan ta ce tunanin Abbas da soyayyar shi da ta yi kane-kane a zuciyarta za ta dinga yi, lashakka za ta samu matsala a kan aikinta.
Don haka take rufe ‘file’ din zuciyarta a duk lokacin da take tare da dalibanta, wadanda suke kaunarta saboda karancin shekarunta da manyan kwalaye haka. Kuma a lokacin ne Jami’ar Al-Azhar ta tura ta karo Karatu (in service) a Jami’ar Ummul-Kura da ke Madinah.

Duk yadda ta yi don ta cogewa hakan abin ya faskara, domin tsarinsu ke nan. Dole ka mallaki kwalin PhD a matsayinka na ‘staff’. Wannan ne zai baka damar zama Dr. A ilimi. Sai dai aure da iyali na sanyawa a barka a nan cikin Alkahira, wanda ba ta da ko daya.
Ta samu Momi da Isma’il take gaya musu batun tafiyarta Saudi-Arabia. Sujood sai ta hau kuka ita ba ta yarda ba.
Isma’il na dariya ya ce,
 “Haba Sujood sai ka ce wata karamar yarinya? Abin da za ta dinga zuwa ko mu muje?”
Budar bakin Sujood sai cewa ta yi, “Ni sai dai mu tafi tare”.
Lailah da Isma’il suka kwashe da dariya, Momi ba ta ce dasu komi ba.
Sai da Sujood da mijinta suka tashi Momi ta dubi Lailah sosai ta ce,
“Kina da yakinin cewa za ki iya rike kanki da mutuncinki tsayin wannan lokacin din?”
Kawai sai Lailah ta fashe da kuka. Ta rasa ranar da Momi da Isma’il za su daina yi mata kallon wata mara imani.
Wane irin tuba suke so ta yi a kan kuskurenta wanda ba ta yi ba? Shekara guda har da doriyar watanni sun kasa yi mata kyakkyawar shaida?
Momi ta saki baki tana kallon ikon Allah, ta ce,
 “To mene ne abun kuka cikin maganata?”
Ta ce,
 “Kun kasa yarda dani Momi. Da zinar halina ce da na yi ta inda babu mai ganin aibunta, kuma da ban fada maku ba balle ku san na aikata.
Momi ki yarda dani, wallahi-wallahi ba zan kara ba, kuskure ne wanda ba wanda ya fi karfin yinsa.
Ki yafe ni Momi, ki tayani rokon dan uwana ya yarda dani. Ku yi min kyakkyawan zato, kada na mutu ba tare da shaidar arziki daga bakin ku ba....” Ta ci gaba da kuka.
Momi ta dube ta sosai ta ce,
“Kina tunanin da shari’ah ake bi a wannan zamanin da ba a jefe ki ba?”

Ta fiddo ido kwalala! “Momi duk da sahihancin tuba na da nadamata?”
Momi ta ce,
“Wannan ne dai ban sani ba, sai dai ki tambayi malamai. Lailah kin bani tsoro sosai, duk tarbiyyar da na maki?”
Ta sa havar gyalenta tana share hawaye.

Hankalin Lailah ya kara tashi, ita ma ta kama kuka. Suna cikin kukan Sanah da Najat suka shigo aguje suna kokawa a kan ‘yar tsana, dole suka share hawayen Lailah ta raba rigimar suka fita.
Lailah ta dago jajayen idanunta ta ce, “Momi me zan yi ki yi farin ciki dani?”
Ta ce,
“Aure”.
Ta fyace hanci da ‘tissue’ ta ce,
“Insha Allahu Momi kamin in gama karatun nan na shekaru biyu zan kawo miki mijin aure na”.
Momi ta ce, “Da dai kin yi wa rayuwarki gata, amma ba wannan neman duniyar ba”.

Ranar litinin jirgin Egypt - Air ya sauke Lailah a birnin Jiddah, ta yi masauki a AL-JAMJOUM zuwa washegari ta bi bus ta wuce cikin Makkah da niyar aikin Umarah.
Kwanan ta uku a Mecca cikin aikin Dawafi da neman gafarar Ubangiji a kan komai ma, tun safe har dare ban da lalurar dan Adam ta ci da sha da shiga bayan gida ba abin da ke raba ta da dakin Allah.
Daga nan ta wuce Madinah, ta kai ziyara shabbaki da duk inda ya kamata. Kwananta biyar ta wuce Jami’ar Ummul-Kura.
Duk wasu cike-ciken takardu na ‘registration’ da ma an riga an gudanar da su ta computer, sai dan abin da ba a rasa ba.
Ta zavi zama cikin ‘hostel’ din dalibai don ya fi mata kwanciyar hankali, ta soma karatunta cike da himma da karfin zuciya.
Bayan tsayin watanni uku suna karatu suka samu hutun sallah break. Ta yi ‘booking’ jirgi sai Egypt. Inda shigowarta harabar gidansu kenan ta soma cin karo da taron yara sa’o’in su Sanah kowanne ya ci kwalliya kamar ranar ne sallah.
Sanah da Najat sun dora wuka kenan za su yanka ‘cake’ din ‘Birthday’ din su suka hango ta tana ratso mutane. Suka yi wancakali da wukaken hannunsu suka sheka suka rungume ta.
“marhaba biki Ya Ablah” (Ablah suna ne da suke kiranta da shi sau tari, wanda ke nufin Yaya)”
Dole sai tare da ita aka yanka ‘cake’ din suka daddanna mata a baki aka yi tafi, sannan kawayensu suka soma rero wakar ‘happy birthday’ cikin harshen Larabci, na cikar Sanah da Najat shekaru goma-goma.
Don haka wunin ranar zungur hidimar da suka wuni yi kenan a gidan har magariba. Sujood na asibiti an ba ta ‘bed-rest’ tana laulayin ciki mai wahalarwa.
Ba su samu kevewa da Momi ba sai lokacin barci. Suna hirarsu a hankali irin na da da mahaifi. Lailah na ba ta labarin jami’ar Ummul-Kura da irin tsarinsu wanda ya bambanta da na Azhar.
Momi ta ce
“Af! Kinga kuwa na manta mutumin nan da ya rako ki Bahaushe ya zo bakya nan”.
Saura kadan Lailah ta fado daga gadonta, Momi ba ta yi aune ba sai ganinta ta yi durkushe a

gabanta, kirjinta kamar ya fashe saboda bugu.
Ta ce, “ABBAS?”
Momi ta ce, “Kwarai haka Isma’il ya gaya min sunansa”.
Ta ce, “Ya tafi?”
Momi ta ce, “Tun a ranar, domin daman a kan hanya yake zai wuce gida Najeriya daga London. Ya ce ya zo ne ya gaishemu kawai, bai yi tunanin kun rabu da Mohd ba, ya dauka kina Najeriya”.
Lailah dai gaba daya ta bushe a zaune ne don gigicewa, don ma tana kokarin saisaita kanta kada Momi ta fahimci rikicewar ta.
To amma ai Momin ba karamar yarinya ba ce, ta fahimci akwai wani muhimmin al’amari tsakanin Lailah da abokin tafiyarta, tun ranar da ta kasa cin abinci don an sanar da ita ya tafi, ba tare da ya yi mata sallama ba.
Ta ce, “Hala saurayinki ne tun a Ingilar taku?”
Ta zaro ido kuru-kuru ta ce, “Wane irin saurayi Momi?”
Ta soma bai ma Momi labarin haduwarta da shi tun a filin jirgin saman Abuja ranar da za ta tashi zuwa Birtaniya, da yadda ya taimaika mata da rayuwarsu a makaranta da gida.
Ta kara da cewa, “Ko da kuskure mutumin nan bai tava sauya kallon da yake min na kanwarshi ba, ya taimake ni a kowanne fanni na rayuwata a can.
Ya kare min mutuncina domin da dama kallon mijina ake yi masa ko Yayana, don haka babu wani mahaluki da ya tava dosa ta da zancen banza har na baro Ingila”.
Ta kare da cewa, “Momi shi ya yi min nasiha na dawo gida, shi ya hanani zub da ciki, Momi Abbas yana da kirki sosai, kuma wallahi Momi shine irin mijin da nake mafarkin samu a rayuwata”.
Momi ta yi murmushi ta ce, “Har kin sa ina son shi”.
Ta ce, “Kirkin shi ya wuce duk yadda kike zato Momi, ga tarin ilimi. Shi ma (Philosopher) ne, don da ya kare karatu a take makarantar ta dauke shi cikin sababbin malaman ta”.
Ta ce, “Dan ina ne?”
Ta ce, “Kano-Nigeria”.
Ta ce, “Garin su mahaifin ku....”
Lailah ta ce, “Yauwa Momi, wai Babanmu ba shi da wasu ‘yan’uwa ne a can Najeriya?”
Ta ce, “Mahaifin ku maraya ne, amma akwai Baffanninsa guda biyu Kano a unguwar Kabara, ban sani ba ko suna raye”.
Lailah ta ce, “Ya kamata mu neme su Momi, kinga dai yadda rashin dangin uba ya janyo min gori da rashin kima a gun Hajiyar Mohammed”.
Ta ce, “Isma’il ya san inda suke, idan kun kara dawowa sai ku je, amma ni ba inda za ni”.
Lailah ta saki wannan hirar ta ce,
“Momi bai ce zai sake dawowa ba?”
“Wa kenan?”
Cike da jin nauyi ta ce,
“Abbas”.
Sai ta yi murmushi kawai ba ta ce mata komai ba.
Ko da Isma’il ya shigo daukar ma Sujood wasu kaya da za ta yi amfani dasu a asibiti bai ce da ita komi ba game da zuwan Abbas.

Ta kasa daurewa ta ce, “Zan iya binka muje wajen Sujood?”
Ba tare da ya juyo ba ya ce, “Basu barin aje dubiya kar a damu mara lafiya”.
Ta ce cikin fargaba, “Ashe Abbas ya zo?”
Ya juyo yana kallon ta, shi kansa ya rasa dalilinsa na tsanarta, ya ce, “Eh, wani abune?”
Ta hadiye kukan da ya taho mata ta juya da gudu ta yi gidansu ba tare da ta ce da shi komi ba.
Ta kwanta rub da ciki a kan gado, tana kuka mara sauti, wanda ta toshe shi da bakin mayafin abayarta kada Momi ta jiyo sautin kukanta.
Ba ta ji murda kofa da rufe ta ba sai zaman mutum a gefen ta. Kamshin turaren shi a gefenta ya sanya ta dagowa da sauri, Isma’il ne.
Ya mika mata hankicif dinshi ya ce, “Share hawayen”. Cikin sassanyan Larabci.
Ta karva ta share amma ba ta dube shi ba. Ya yi shiru sannan ya ce, “Ki gafarce ni, haka nan na samu kaina da daina ganin farin ki. Domin........”
Ta kai hannunta ta toshe masa baki don ba ta son jin abin da zai fada, zancen nan ne dai da ba ta so a kara tuna mata.
Ya sauke hannunta daga bakinshi ya ce, “To ki yi hakuri”.
Ta ce, “Na yi”.
“Abbas ya zo baki nan, ya yi mamaki kwarai jin cewa all these while  kina gida. Amma baki neme shi ba, na gaya mishi ko waya baki rikewa. To amma zai dawo”.
Ba ta so ya ga ta fiya ci-da-zuci. Da ta tambaye shi yaushe zai dawo din?
Ya mike ya fita yana cewa, “Sujood ta damu tana so ta ganki. So ki daure ki yi ko sati ne ta dawo ta ganki”.
Ta ce, “Allah sarki Sujood, Allah ya raba su lafiya”.
Ya amsa
“Ameen”.

Washegari ta tashi da nishadi, don haka ta je aka yi mata kunshi da gyaran gashi, akaifa da wankin kafa. Ta wuce makaranta ta dawo.
Bakuwar mota ta gani a harabar gidansu, ta karasa ciki da sassarfa bayan ta rufe motar ta. Mohammed ta fara yin tozali da shi, sannan Sa’eed da wasu kyawawan mata guda biyu da fara da baka.
Tana tafe cikin falon har hardewa take yi, ya yin da Isma’il ke ta wadata ‘dining’ da abinci da abin sha shi da Amatullahi mai aikin su.
Momi na gefe ita da A’isha suna ta hira, Momi na ta zuba shakakkiyar Hausarta kamar jakar Kano.
Kallo daya Lailah ta yi wa Sa’eedu ta ga yadda ya rame ya lalace kamar ba shi ba, ta dauke kai kamar ba ta ganshi ba.
Za ta wuce ciki Momi ta riko hannunta ta ce,
“Baki ga bakin naki bane?”
Dole ta zauna gefen Momin tana kallon su kawai da idanu. Sa’eed na kuka bayan shigar su A’isha sassan baki, yake rokonta ta yafe masa, ta yafewa Mohd.
Don a dalilinta yanzu Mohd ya aje aiki, ya ce, tunda aikin ne ya raba shi da ita, yake kuma barazanar raba shi da duk matar da ya aura to ya barshi, zai gwada wata sana’ar.
Kuma anyi masa aiki, yanzu haka A’isha na da ciki wata biyar. Wannan kuma Zanira matarshi

ce, ita ma ‘yar uwarsu ce. Shi kuma ba shi da lafiya suga ta kama shi sosai.
Shi yana kuka Lailah na yi. A da kam ta yi alkawarin ba za ta tava yafewa Sa’eed ba har karewar numfashinta, amma a yau ta tuna wani karin magana da Hausawa ke cewa.
“....... Idan vera da sata.....to daddawa ma da wari”.
Sai ta ce, “Allah ya yafe mana bakidaya”.

Ta zage sosai ta karvi su A’isha, karva ta karshen mutuntawa. Shi dai Mohd sai ido yake binta da shi ganin yadda ta kara komawa yarinya danya sharaf ba ‘yar shekaru talatin ba.
Soyayya gaskiya ce, kuma har abada ba ta gushewa. A haka yana ji yana gani ya baro Lailar da a da mallakinsa ce.
Ba ta koma Saudiyya ba sai da Sujood ta fito daga ‘bed-rest’. Har da ita aka yi mata rakiya ta tashi ranar Asabar.
Ta tarar da abokiyar zamanta a dakin (Dhuha) ta riga ta dawowa. Ta gyare masu dakin tsab. Balarabiyar Afghanistan ce.
Suka ci gaba da karatu, wanda duk rabi bincike ne cikin manyan littattafai wato (research).

Tana tsaye gaban book-shelf na main library din Ummul-Kura, tana kokarin zaro wani littafi. Dai-dai lokacin da agogon library din ya buga karfe goma sha daya na rana, ya yi dai-dai da bugawar zuciyarta da faduwar gabanta. Dai-dai lokacin ta hango wani ‘giant’ yana tahowa cikin fararen kaya, iska na kada shi, yana tafe yana waya, ba ta san lokacin da littafin ya suvuce, ya fadi daga hannun ta ba.
Ba ta yi wani motsi ba har ya karaso . Ya russuna ya dauko mata littafin ya mika mata, sannan ya kama hannunta suka fito daga library din. Ta zamo kamar mutum-mutumi, sai janta yake tana binshi ba uhm-ba-umh-uhm.
A al’adarta tunda ta zo Ummul-Kurah, kullum sai ta kai ziyara shabbaki, kamar ya san hakan, don kuwa da ya tare tasi shabbaki ya ce ya kai su.
Kasancewar masallacin maza daban da na mata, a nan harabar masallaci ya sata ta yi addu’o’inta, shi ma ya yi. Suka fito ashe tuni ya yi masu ‘booking’ din mota wadda za ta kai su har cikin Mecca.
A cikin mota Lailah ke bin shi da idanu, yadda ya damke hannunta kamar wata matarshi. Abbas dinta.....abokin kan hanya!
Ya kara kyau na misali, ya kara murjewa. Ta yadda har ba ta gajiya da kallon kyakkyawar fuskarsa.
Ta sunkuyar da kai cikin siririn sauti ta ce, “Amma ka san hannun nan da kake ta rikewa, haramun ne ko?”
Ba ta kai ga rufe bakinta ba sai ya sa dukkan hannuwa ya rungume ta.

Lailah ta samu numfashinta yana sassarfa a cikin kirjin Abbas da kafadun shi. Ta yi ta kici-kicin ta kwace amma ta kasa. Ta kuwa daga hannu ta kai mishi wani wawan mari ya goce, hucin marin ya wuce ta gefen kunnuwansa. Ta fashe da kuka ta ce,
“Saboda na baka labarina shine ka dauke ni ‘yar iska ko?
To bari ka ji, ko na fi iblis iskanci ba zan yi a cikin garin da manzon mu ke kwance ba. Kai malam tsaya da motar nan in sauka.....”

Ya yi dariya sosai, sannan ya sake ta. Ya nuna mata agogon RADO dake daure cikin kwantacciyar sumar hannun shi.
“Karfe sha daya na rana wanda ya yi dai-dai da karfe biyar na yamma agogon mu na gida Najeriya.
Baffanninki Malam Ado da Malam Ilyasu da waliyyinki Isma’il suka damka mani igiyar rayuwarki, suka shaida na zama mijinki har zuwa karshen numfashinmu”.
Sai jikinta ya yi sanyi, ta rasa abin cewa, kuka za ta yi ko dariya? Bakin ciki za ta yi ko ko farin ciki? Bata sani ba.
Ya sake runtse hannunshi cikin nata sosai ya soma ba ta labarin yadda al’amarin ya faru. Ta tabbatar karfe sha daya na rana ta ji faduwar gaba da bugawar zuciya, ashe igiyoyin Abbas ne suka hau kanta.
Ya ce,
“Na je Egypt watanni biyu da suka wuce in gai da Momi da Isma’il. Yake gaya mani cewa kina nan Madina. Na tambaye shi Umrah kika je? Ya ce, a’a, karo karatu ne, don aiki kike yi. Ya ce kun rabu da mijinki tun wancan karon. Ban yi kauron baki ba ko A BARI YA HUCE.... na ce da Isma’il ya yi mani alfarma, ya aura min ke.
Ban san ya suka yi da Momi ba, ta ce, in ba ta lokaci za ta yi nazari tana so ta ji daga bakin ki. Sanda na sake komawa ta ce ta gama nazarinta in turo wakilaina wajen Baffanin ki a Kano su za su sake daura miki aure.
Don haka Isma’il ya taho Najeriya muka hadu, muka je Kabara aka daura auren, sadakinki yana hannun Isma’il
Ba yadda bai yi dani ba in bari za ki zo karshen watannan ban saurare shi ba, dole ya bani adireshin inda zan same ki wato jami’ar Ummul-Kura.
Ban sha wuya ba aka binciko min lambar dakin ki. Na tura a kira ki sai abokiyar zaman ki ta ce kina nan. To kin ji.
Nima ba dan iska bane. Da kuma dan iskan ne da ba yau zan fara ba......” Ya karasa da dariyar da ta cunkushe masa ciki.
Ita dai Lailah binshi take da ido, mamaki ya hanata magana. Hakika tana cikin mutane masu sa’ar samun duk abin da suke so a rayuwa. Da da hali da itama ta rungume shi ta yi kukan godiya ga Allah a kan kirjinsa.
Sai yamma lis suka shigo cikin Mecca, ko abinci basu nema ba sai da suka fara yin (Dawafi) suka yi sallar magariba da isha da nafiloli. Sannan suka je wani ‘restaurant’ suka ci abinci, daga nan suka taho Ka’aba suka ci gaba da gabatar da ibadodinsu.
Sai asuba suka koma masauki, wanka kawai suka yi ya shige ciki ya kwanta yana biyan bashin barcin da bai samu ya yi ba saboda godiya ga Allah da ya mallaka mishi abin da yake so, bai kuma tava tsammanin samu ba, ya samu a bayan fidda rai.
Ita dai Lailah ko gezau, tana zaune dungurgur  a kan kujera tana kallon talabijin din da ke ta aiki ita kadai ba ta san me suke yi ba.
Kamar ka ce kyat.....! Ta arta a na kare. Don ita kwata-kwata yanzu kowanne namiji ma tsoron shi take ji balle ya kai hannu ya tava ta.
Bai tashi ba sai karfe goma na safe, shi ma din kiran Isma’il ne ya tashe shi, suna gaisawa ya mikawa Laila.
Bayan sun gaisa yake mata bayanin da Abbas ya yi mata, ta ce a sanyaye,

"Toh!"
Momi na karva sai ta valle da kukan kaunar da take mata. Tana so ma ta yi mata godiya amma ta kasa.
Momi ta ce,
"To kukan na mene ne?
Ke fa da bakin ki kika gaya mani kina son Abbas?"
Ta share hawaye tana murmushi ba ta ce komai ba. Ta ce, "A'a, in kin daina son nashi ne ki gaya mani sai in ba shi hakuri ya karvi sadakin shi, tun da dama bai zo hannun ki ba."
Ta yi saurin cewa, "A'a Momi".
Ta yi dariya ta ce, "To shi kenan, a sha amarci lafiya, ki kula da shan 'fresh milk' da cin dabino da shan zam-zam tare da inibi".
Kunya ta kama ta, don ta san sune abubuwan da take ba ta sanda za ta yi auren fari.
Abbas ya fito daga shi sai 'short – nicker' kanshi da tawul yana goge ruwan cikin sumar kanshi. Kallo daya ta yi mishi ba ta kara ba ta kara takurewa a cikin kujera. Ya juya mata baya yana dariya ya zuba farar jallabiya mai santsi, ya fesa turaren shi (one-man-show), ya fesa turaren baki (mouth fresh), sannan ya iso gare ta.
Ya zauna a gefenta yana so ya ja ta jikinshi amma ya lura da yadda ta ke a tsorace da shi. Sai ya yi murmushi ya mike zuwa hammam (bayan gida) ya hada mata ruwan dumi cikin kwami, ya ce ta yi wanka ta ji dadin jikinta su fita su nemi abin karyawa.
Ba don ta so ba ta mike ta shiga wankan, amma fa ta kukkulle kofar bandakin da (jam-lock) sannan ta fara wankan, shi kuma ya sauka kasa ya samo musu abin karin kumallo.

****

Kwanansu uku suna Umrah, amma ya kasa gane kan hutsuwar amaryar tashi. Ba ta umh ba ta umh-umh, duk ta takura kanta. Maganar duniyar nan idan zai yi sai dai ta bishi da 'eh' ko 'a'ah'. Har yana mamaki kamar ba Lailan shi ba.
Ya kuma soma tunanin ko dai ba ta son auren ne. Ta hana mashi amarcin har zuwa ranar da za su rabu, dama shi a kan hanya yake zai wuce London.
A daren ranar dai ya rantse yau sai ya gane abin da Lailah take nufi da shi, ba ta son shi ne ko iya shege ne? Ita ba yarinya ba balle a yi mata uzrin kuruciya.
Tana zaune cikin kujerar falon hotel din da suka sauka, hannunta remote ne tana canza channel ya kwankwasa kofar.
Ta tashi ta bude idanunshi cikin nata aka jefe shi da wani miskilin murmushi. Turata cikin dakin ya yi da kafadunshi ya aje ledojin dake hannun shi. Sannan ya juya ya karvo na hannun yaron hotel din da ke waje ya aje gefe ya rufe kofar.
Ba ta yi aune ba sai ji ta yi ya sunkuce ta ya yi sama da ita. Bai dire ta ko'ina ba sai cikin kwamin wanka, duk da kayan da ke jikinta.
Ta ce, "Haba Abbas, ya za ka jikani? Yanzu na yi wanka fa".
Bai saurare ta ba ya saukaka kayan jikinta ya manne bakinta da nashi da wasu irin matsiyatan 'kisses' da ba ta tava sanin akwai irinsu a duniyarta ba.
Ya saki 'shower' a kansu, cikin wani sabon al'amari da Lailah ba ta tava tsintar kanta a kwatankwacin sa ba.
Ashe dai wannan ita ce soyayyar, na baya duk shirme ne? Wane Sa'idu wane Yayansa!?

Wadanan MANYAN MAZA ke magana…., wadanda basa furta SO ko I luv u a fatar baki, sai dai ZUCIYA da GANGAR jikinsu ya nuna.
Fatan alkhairi gare ku ABBAS DA LAILAH! -Takori

Washegari ta kama Lahadi, Abbas kam yau sallar asuba a gida aka yi ta, Lailah ta samu kanta da kasa hada ido da angon nata. Shi kuma hakan bai hana shi gudanar da amarcin shi ba, soyayya ruwan zuma gangariya ake gunadarwa cikin kwanaki biyun da suka biyo baya.
Ya kasa amincewa wai ya tafi ya bar Lailah, har na tsayin watanni uku. Ga ayyuka ya bari masu dimbin yawa. Ita kanta Lailar ta baro nata ayyukan a makaranta don haka ta karfafe shi da su daure su tafi, lokaci kankani ya rage mata ta kammala gaba daya sai su tsara mai yiwuwa.
Sai da ya kaita har Madinah tamkar ba za su rabu ba, hakan dai aka daddaure aka ciccije aka rabun da alkawarirrika masu yawa da ma'ana.
Ya biyo Ajrah (tasi) ya dawo Jiddah, karfe goma na daren ranar ya bi British-Air zuwa London.

Tana canza kaya a dakin su Dhuha ta yi sallama ta shigo, kallon mamaki ta yi mata tare da tsoro, ta ce cikin harshen Larabci.
"Ke kuwa ina kika shiga Lailah har tsayin kwana biyar? Yanzu haka daga kai 'report' din vatanki nake ga 'security' din makaranta. Hankalina ya tashi sosai".
Lailah ta yi dariya ta ce, "Kai Dhuha? Ana yankan kai ne a Saudi-Arabia?"
Ta ce, "Ina na sani, tun da na ga wani ya zo neman ki kuma tun daga ranar ne ban kara ganin ki ba, ba dole in yi zaton ya sace ki ba?"
Lailah ta kara yin dariya ta ce, "Sai ki koma ki gaya musu gani na dawo". Ta juya tana cewa, "Yanzu kuwa".
Lailah ta kwanta a gadonta ta lumshe lumsassun idanunta tana tariyo rayuwarta filla-filla tun daga kuruciya har girma.
Ta tuno Mohammed da rayuwar ta dashi, ta tuno Sa'idu. Sai ta samu kanta da yi musu addu'a. Ta kuma gode Allah da ya musanya mata da miji na gari dai-dai yadda take buri a rayuwarta ta duniya.

****

Bayan shudewar watanni uku suka samu hutu ta koma gida Egypt, ta tarar da haihuwar Sujood, ta haifi kyakkyawar yarinya mai kama da Momi Najla. Wannan ne ya sa take yanayi da ita Lailan, don duk cikinsu ta fi su kama da Momi. Duk yadda ta so ayi shagalin suna da ita hakan ya faskara, sakamakon rashin isasshiyar lafiya, komai ta ci sai ya dawo ba ta ko son ganin abinci ko kamshin sa.
Daga rowan lipton din 'Tetley Tea' sai gugguru, su kadai ne in ta ci ko ta sha ba ta amansu. A matsayin Sujood na cikakkiyar likita, a take ta gane abin da ke damun Antin tata, ciki ne na watanni biyu ko Momi ba ta gane ba.
Sujood ta rubuta magungunan da za su taimaka mata aman ya tsaya ta ba wa Isma'il ya siyo mata ba tare da ya san na wace ce a cikin su ba, tun da ba ranar ta fara aiken shi siyan magani ba.
Baby ta ci sunan Momi wato NAJLA, suke kiran ta Nawal. Sujood ta dage da kula da Lailah don duk hidimar Nawal Momi da su Najat ke yi, tsakanin ta da ita sai shan nono wanda sai ta wuni

ba ta sha ba, saboda Momi tana ba ta madara.
Suna wajen motsa jiki Sujood ta dakata ta dubi Lailah ta ce,
"Antinmu ni fa kallon mai ciki nake miki, ki daina edcercise dinnan".
Lailah ta jinjina kai ta ce,
"Nima na dade da zargin kaina, don watanni uku kenan rabona da al'adata....."
Hawaye suka zubo mata na tunawa cewa; wannan dan HALAAL ne a jikinta, wanda kowa zai karva.
***
A yammacin ranar Abbas ya iso. Washegari suka wuce London. Ga mamakin Lailah Abbas ya tashi daga gidan hayarsu, gida guda Muslim College ta ba shi a cikin gidajen malamai. Aka koma rainon ciki, tattali da kulawa wurin Abbas wane na baya, wanda ake da shamaki a cikinsa. Watan ta guda ta koma Ummul-Kura. Ta karasa rubutunta na (project) ta mika, ta amshi kwalin Dr. of Philosophy (PhD). Suka tattara suka koma Ingila.
Haka rayuwarsu ke garawa cikin nasara da ci gaba kala-kala. A NHS Lailah ta haifi 'bouncing baby' dinta mai kama da ubansa har duhun kalar.
Abbas ya ba shi sunan Isma'il, a cewar shi shine ya shige masa gaba ya ba shi Lailah a lokacin da ya riga ya fidda rai.

ABBAS da LAILAH, sun zamo manyan-manyan malaman Falsafa a kasar England, a babbar Jami'ar Musulunci (Muslim College) da ke birnin London.
Akai-akai kuma suna zuwa gida Najeriya gai da Baffaninsu, da yi musu hidima iyakar karfin aljihunsu. Balle Egypt kuma da ba sa yin watanni uku kwarara ba su zo ba.

MURFI

A'study' ya same ta tana shirya litattafanta cikin kabinet, a gefe Isma'il ne (Sayyid) da Khalisa (Sayyidah) tare da autarsu Najwa suna wasansu cikin na'urar koyon karatu mai Alifun-Ba'aun.
Ya yin da babban yaya wato Sayyid ke gefe yana ta rubuce-rubucen sa, dukkansu basu ankara da shigowar Daddyn ba, kasancewar kowannen su ya mai da kai ga abin da yake yi ko sallamar shi basu ji ba.
Ya karasa ga Momin ta bayanta ya rungume ta, kamshin turaren shi kawai ta shaka ta lumshe idonta tana murmushi.
Ya dora habarshi a kafadunta ya ce, "Momy fatawah nake nema".
Ta ce, "A kan me Daddy?"
Ya ce, "A kan karin aure?"
Ta zumvura baki ta zame shi daga kafadunta ta ci gaba da shirya littattafanta tana cewa,
"Bani da sani a kan wannan sam!".
Ya juyo ta ya ga yadda ta yi kicin-kicin da fuska sai ta ba shi dariya, ya ce, "At thirty five Momi kin girma fa, ki barni in dauki sweet sidteen, ta zo daga Muzambikue yin Diploma, shine nake neman fatawa a kai.
Shin wanda Allah ya yi wa baiwa da mace mai ilimi, kyautatawa, biyayya, tausayi da jin kai ga mijinta, tare da kular masa da tarbiyyar 'ya'yansa da gamsuwar sa a shimfidar su, ta tsare masa mutunci da dukiya idan baya nan, ta zamo mai himma da kokari ga son faranta masa rai, ta cancanci ayi mata kishiya?"

Abin ma ita sai ya ba ta dariya, ba ta san sanda ta ce,
“Idan mijin butulallen Allah ne, ba sai ya yi mata ba?”
Ya jinjina cikin dariya ya ce,
“Kada fa ki manta, Ubangiji (S.W.T) cewa ya yi, “Ku auri abin da ya yi muku dadi daga daya-daya, biyu-biyu, uku-uku ko hur-hudu.....”
Ta zame cikin sanyin murya ta ce,
“Don Allah Abbas ka auri goma-goma.....” Sai hawaye suka zubo.
Ya kai hannu ya shafo hawayen yana murmushi ya ce,
“Ni din me Lailah? Da za ki zub da hawaye a dalilina? Idan kin ga na hada rayuwa da wata, to sai a Aljannah, idan Allah ya yi min kyautar Hurul-eeni, sai in hada da ke ta zama kwarkwara........wannan alkawari ne Lailah. You are more than enough to me......and I’m only yours!” Ya kara rungume ta.
Ta yi murmushi wanda ya fito tun daga karkashin zuciyarta, kaunar mijinta ta kara kwanciya cikin ranta kamar ta hadiye shi don so da kauna. Sai itama ta rungumeshi sosai. Sannan ta yi mishi nuni da Sayyid wanda ya aje rubutunshi ya zubo musu ido.
Ya sake ta ya koma gabansa ya zauna, ya kama hannun shi kafin ya yi magana yaron ya riga shi.
“Me ta yi maka ka sa ta kuka?”
Suka kyalkyale da dariya shi da Lailah. Ya dora hannun daman shi a kan yaron ya ce.
“Ban yi mata komai ba, tsokanarta na yi na ce zan kawo muku Aunty, shine take kuka”.
Ya ce,
“To Daddy ai mu muna son Auntyn”.
Ya ce,
“Ban isa ba Sayyid in yi abin da Momi ba ta so, ko ina so kuwa, balle ma wasa nake. Ba na son kowa sai Momi.....ni mijin ta-ce ne, ku kawai nake so..... I luv you all......” Ya hada su ya rungume gaba daya.

MASHA ALLAH LAKUWWATA ILLAH BILLAH!